(*b*) *Uwa tasa* or *uwa tai* is used for *uwarsa*; *uwarshi* is nearly always *uwanshi*, the "n" being incorrect, and the *shi* heard mostly only in Zaria, Nassarawa, and Muri. *Uwa tata* is often heard, *uwarta* drops the "r."

(*c*) *Ubanmu* is more generally *ubammu* (for euphony), and *uwarmu uwammu*, the "r" becoming first "n" then "m." See Note II (*A*). *Uwarsu* is also changed to *uwansu*.

(*d*) *Ubaninmu* or *ubanimmu* means "our ancestors" not "our fathers." *Uba* has many meanings besides father and guardian: *Uban-yaki*, commander of an army. *Uban-gida* or *uban-giji*, house-owner, master of slaves.

(*e*) *Uwayenmu* or *uwayemmu* is "our parents" (*iyayemmu* more common) not "our mothers." *Uwa*, too, has different applications. *Uwar-gida* or *uwori-gida* means "mother of the house," *i.e.*, first wife. *Uwar-rana* is "a mirage."

(ii) The separable forms are simply the *na* and *ta* joined to the *wa*, *ka*, *sa*, &c., without any contraction, the preposition and pronoun agreeing as before.

*Dokin nan nawa ne*, This horse is mine.
*Godiyar chan tawa che*, That mare is mine.
*Rakumin nan naka ne*, Is this camel yours (m.)?
*A, a, amma taguwar chan taki che*, No, but that she-camel is yours (f.).
*Karen nan nasa ne*, Is this dog his?
*I, kuma kariyar' chan tata che*, Yes, and that bitch is hers.

The "n" in *dokin*, &c., and the "r" in *godiyar*, &c., are definite articles. *Vide* Note XXIV.

*G.*—The demonstrative pronoun (*wannan*, &c.) is very simple, it is usually contracted to *da* for both genders and numbers. Numerous examples have been given already.

## XXIV.

### The Article.

There is a definite article in Hausa with the forms "-n" and "-r," and two explanations as to its formation occur to one.

(i) The first is that the "-n" is a contraction of the demonstrative pronoun *wannan*, this.

*Mutumen nan* (= *mutum wannan*) *ke nan, wanda* . . . . This man, it is who . . . . would become *Enna Mutumen*, Where is the man?
*Enna machen* (*nan*), Where is the woman?

A similar process is seen in *mutumenda* (*mutum wanda*), The man who.

The "-n" is used only when special emphasis is required:—
*Mutum ke nan*, It is *a* man (not a monkey).
*Enna mache wadda zata yi shi*, Where is *a* woman to do it?

There is an objection to this view, namely, that only the masculine form would appear, whereas there is feminine "-r" as well as the "-n," though it is not used before *nan*, probably for the sake of euphony.

(ii) I think the correct explanation is that the "-n" and "-r" are contractions of the masculine and feminine forms of the preposition "of" used with the word *nan*, and their employment gives meanings something like the following. The "-n" and "-r" are used only when the nouns to which they are attached have been previously mentioned:—

*Mutumen nan*, The man of (this place) here.
*Machen*, The woman of (our conversation).
*Igiar chan*, The rope of there.

Against this is the fact that "-n" is used with mache. The rule seems to be that only words ending in "a" have the "-r," all others whatever their gender take "-n." If the second supposition is correct, *wannan* has come from the original *wa* by a similar process.

*B.*—The indefinite article is the indefinite pronoun:—
*Na ga wanni mutum*, I saw a (certain) man.
*Wota mache ta zo*, A (certain) woman came.

# PART II.

# Hausa Text of Stories in Hausa Superstitions and Customs.

---

## 1

### There is no King but God.

En anzo fadanchi, anche " Ran sariki ya daddi." Sai wanni mutum ya che "Ba sariki sai Allah." Kullum kullum hakka, sai sariki ya ji fushi da shi, sai ya kawo zobe biyu azurifa, ya ba shi ajiya, en ji sariki. Ya che ya'a gamma da shi. Ba-Sariki-Sai-Allah* sai ya dauki zobe biyu, ya zuba a kafon rago, sai ya ba matanshi ajiya, shi, Ba-Sariki-Sai-Allah.

Sai da akakwana biyar, sai sariki ya che " Ba-Sariki-Sai-Allah, zan aike ka wanni kauye." Ya che " To." Da ya aike shi, ya che " Ache da talakawa su zo ginnin garu." Da ya taffi, sai sariki ya che "Aje wurin matan Ba-Sariki-Sai-Allah," ya che "Aba ta zambar dari, aba ta zanne dari, alfuta dari, ita kuma ta ba sariki abinda Ba-Sariki-Sai-Allah ya ba ta ajiya." Sai ta che "To," sai ta kawo kafo, ta ba su. Sariki ya taffi, ya bude, ya duba, ya ga zobenshi achikki. Sai sariki ya mayar achikkin kafo, ya dwade, ya che "Adauka, asakka a wanni taugi da ba shi konewa." Da zuwa, da akaje taugi, akajifa kafo, sai wanni katon kifi ya hadiye.

Sai ran nan, sai Ba-Sariki-Sai-Allah ya dawo dagga taffiya. Da ya dawo dagga taffiya, sai mutanen gari suka che za'ayi su a taugin nan. Da akaje, sai dan Ba-Sariki-Sai-Allah ya kama katon kifin nan sai ya zo ina fidi, ina fidi, sai wuka ya tabba kafo keras! Sai ya che "Opp, da wanni abu achikkin kifi." Sai Ba-Sariki-Sai-Allah ya che "Minene?" Sai dan ya che " Ai, da wanni kafo achikki." Sai ya che "Dauko mu ganni." Sai ya dauka, sai ya ba uban. Sai ya bude kafo, ya duba, sai

---

* Hyphened because now a name.

ya ga zoben sariki da ya ba shi ajiya. Sai ya che "Ba sariki sai Allah kuwa."

Sun gamma fiden kifi ke nan, sai manzon sariki ya zo, ya che "Ba-Sariki-Sai-Allah, en ka sha ruwa sariki yana kirranka." Sai ya che "To." Da manzon ya taffi, sai ya che da matansa "Enna ajiya da na ba ki?" Sai ta che "A, ni, ban sani ba, ko bera ta dauke shi." Sai ya che "Ba sariki sai Allah."

Da ya sha ruwa, sai ya kama hainyan fada. Da ya je, ya zona. Da ya zona, fadawa suka che, "Ran sariki ya daddi." Sai ya che "Ba sariki sai Allah." Sai sariki ya che duk fadawa su yi shiru, za'ayi magana da Ba-Sariki-Sai-Allah. Sai ya che "Ba-Sariki-Sai-Allah." Ya che "I." Ya che "Ina son ajiya na wurinka yanzu yanzu." Sai dogarawa suka tashi, suka tsaye akan shi, em ba ya bada ajiyan nan na sariki za'adauke shi a tsiri.

Sai Ba-Sariki-Sai-Allah, sai ya sa hanu a aljifu, sai ya dauke kafo, ya mika ma sariki. Sai sariki ya bude kafo, ya ga zobenshi. Sai ya che "Tabbas ba sariki sai Allah." Sai fadawa suka dauka Ba-Sariki-Sai-Allah, sai sariki ya dibi mashi rabbin gari ya ba shi.

---

## 2

### The Punishment of the Sabbath-breakers.

Mutane ke nan suka taffi su. Da suka chikaro da tsofo, sai tsofo ya che "Enna zaku?" Sai suka che "Zamu su." Ya che "A, yau ba ranan su ba ne." To, ran Assabat, kuma. Sai suka che su zasu taffi. Sai ya che "To, ku taffi." Suka taffi, suna su.

Sai bushiya ta yi masu sawa, sai ya che "Kuna kame da ni?" Sai suka che achikkin zuchiyansu ba wanda zaya hanna su yanzu. Sai yan-kamu suka zamma samba gaboroji, su kuwa mainyan, sai akazamma da su gauji, ba su koma gida ba.

Ka ji, ran Assabat ran sallan kifi ne.

---

## 3

### The Tender-hearted Maiden and the Fish.

Wanni mutum ya taffi kogi ya kama kifi, ya zo da shi gida, ya kawo ma matansa. Ta che da yar kishiyanta "Tashi, ki taffi

rafi, ki wanke kifi, izan kin sakke shi, da kin komo gida em ba ki duka."

Yariniya ta taffi kogi, tana wanka kifi, kifi ya che "Ke Yariniya, ba ki sakke ni ba en taffi em ba yayana mama?" Yariniya ta che "To, taffi." Ta zona har kifi ya komo, ya che "To, dauke ni mu taffi." Ta che "A, a, taffi abinki." Ya che "Na ji abinda anfada maki za'abuge ki." Ta che "Kifi, ka taffi abinka." Sa'anan ya che da yariniya "Sai gobe, da safi ki zo." Yariniya ta taffi gida, suka kama ta, suka buge ta. Ubanta ya che "Ku bar ta, Allah ya ba mu wanni gobe."

Sa'anan ta tashi da safi, ta taffi wurin kifi, kifi ya tara danginsa duk su zo su ga yariniya wada ta sakke shi. Dengi duk sun zo kuma, sun taru. Sa'anan ya kirra yariniya, ya che "Ki zo." Yariniya ta taffi. Ya che "To, ga wanda ta yi mani rai, ankama ni, anche adaffa ni, amba ta ta zo ta wanke ni, sa'anan ta sakke ni. Hakkanan na che 'Ku duk ku zo ku gan ta, ku yi mata murna kuma.'" Ya che "Taffi gida kuma, idan kin ji yunwa, ki rikka zuwa nan har watan salla ya zo."

Watan salla ta tsaya, zasu wasa irin na yara achikkin gari. Sa'anan ya che "Idan zasu wasa, ke kuma, ki zo nan wurina." Sun fitta zasu wasa, akakarbe tsofan zanne akabai wa yar kishiya, ita, yanta kuwa, amba ta sabon zanne, ta daura. Ita kuwa, ta taffi wurin kifi abinta da tsofan zanne, ita, yar kishiya. Kifi ya hadda mata kayan ado duk. Yariniya ta taffi wurin wasa, ta yi keyau.

Sai sariki ya aike, ya che yariniya nan yana son ta da aure. Ta che "To, ataffi gidan ubana, ba a wurin wasa anhaife ni ba." Sai sariki ya sa fadawansa su taffi gidan uban. Sa'anan uban ya che "A, a, ba ni da yan da sariki na so ba." Sa'anan ta che da yanta "Tashi ki gudu gida, ba kin ji sariki yana son ki ba?" Ta che "A, a, ba ni ne ba, wanchan a wurin wasa sariki ya gan ta." Akazo, akadaura aure, sariki ya ba kishiya dukiya, akache "Adauke ta akai ta wurin sariki." Sa'anan da da dare ta taffi ta gudu wurin kifi, ta gaya masa, ta che "Anyi mani aure da sariki." Kifayi sun che "Madallah," suka che "Ki taffi gidan sariki, gobe muna zuwa." Ta che "To." Da safi suka gammu duk, ya gaya ma danginsa abinda ya faru. Suka tara hatsi. Sai dayamma, dare ya yi kuma, sa'anan suka aike, suka che "Kadda mutanen gidan sariki su fita woje da da dare fa." Suka dauka garin hatsi su kai ma yariniya, suka tara zannuwa duk su kai mata.

Sa'anan matan gidan sariki da da dare suka kama hanun yariniya, suka yanka don kishi, suka che "Ga matan sariki ba ta da hanu." Ta tashi yariniyar dakinta, ta che "Ki taffi

wurin kifi, ki gaya mata ga abinda ankai mani, suka yanka mani hanu duka biyu." Da kifayi suka ji, suka che "To, tunda ba ta sa mamu kuka ba, ita kuwa ba ta yi ba." Da dare ya yi tsakka, kifayi suka kama hainya, suka taffi gidan. Suka mayar mata da hanu kuma.

Da gari ya waye, mata suka che aba su dawa su dakka, suka che "Akirra amariya ta zo ta yi dakka." Amariya ta fito, suna che ba ta da hanu biyu, sai ta dauke tabariya suka gan ta da hanu. Sai waddane mutane suka ji akache ba ta da hanu, sai suka yi ma kishiyoyi dariya, anayi masu dariya, sai sun ji kumya. Ta kiyale su kauwi, ta komo wurin sariki abinta.

---

## 4

## The Spider, the Old Woman, and the Wonderful Bull.

Jatuma che de, tana dafuwa gainye, tana kai a kasuwa, tana sayaruwa. To, sai ta samu kurdi, ta saye dan sa kankani. Shi ke nan, sai ta samu dan sa, sai ta sa a dakinta, tana kiwo. Tana kiwo har ya girima, har ya zamma sa kato.

Shi ke nan, sai ran nan sai gizzo ya ga sa, sai gizzo ya je ya gaya ma sariki, ya che "Sariki, kunnenka nawa?" Ya che "Kunnena daya." Ya che "Yanke daya ka ba ni en chi, ka sha labari." Shi ke nan, sai sariki ya che "Na yi, mi ka ga?" Sai gizzo ya che "Na ga sa a gidan jatuma, sa baba." Sai sariki ya sa mutane suka je suka kunche sa. Shi ke nan, sai akakunche sa, sai sa ya ki taffiya. Shi ke nan, sai akache "Abugi gizzo." Sai akache "Abuge ni, abugi kuwa jatuma," en ji gizzo. Sai ta che "Kuntu kuntu ga turiki, sai sarakai banna kwadaye gare su, abu kadan su kan kai ka fada." Shi ke nan sai sa ya taffi, ya shiga gidan sariki. Sai akayi da sa ya kwanche, ya ki kwanchiya, sai akache "Abugi gizzo." Sai ya che "Abuge ni kuma abugi jatuma." Shi ke nan, sai ta che "Sa yi kwanche ayanka ka." Sai sa ya kwanta, akayanka.

Shi ke nan da akayanka sa, akaba jatuma kayan chikki duka, da akaba ta, ta taffi. Sai jatuma ta bar auduga a daki, kan ta komo sai ta ga ankada auduga. Shi ke nan, sai ta boya achikkin daki sai ta tarada yam-mata suna kadi. Sai shi ke nan, sai yara zasu boya su zamma hanji, shi ke nan sai ta che "Ku yi zammanku." Sai sun che "To."

Sai ran nan gizzo ya zo yawo gidan jatuma. Sai shi ke nan, sai ya tarada yara keyaukeyauwa, sai ya je ya gaya wa sariki, ya

che ya ga yam-mata masu-keyau a gidan jatuma. Sai sariki ya che "Atafi, azo da tsofuwa da yara." Shi ke nan, sai yara suka zo, akache da tsofowa ta taffi gida da sauran yara, sariki ya zabe daya mai-keyau, ya aura.

Shi ke nan, sai sariki ya taffi yaki, sai akache yariniyan nan ta bar fitar woje, en ta yi aiki sai ta yi narike. Sai shi ke nan, sai sariki ya taffi yaki. Sai da ya taffi yaki, sai matan gidan sariki na da suka che ta fito ta yi aiki. Sai yariniya ta fito tana yin aiki, sai ta narike agabban wuta. Sai aka'aike kurichiya, akache "Ki je ki gaya wa sariki yariniya ta narike." Shi ke nan, sai sariki ya ji labari, sai ya komo gida, sai ya che "Enna abinda akasa yariniya ta fito, ta yi aiki?" Sai akache matan gidan suka sa.

Sai shi ke nan, sai akayi kirran jatuma, sai jatuma ta buga gunda yariniya ta narike, sai yariniya ta tashi. Sai sariki ya che "Mi ya sa ki kin fito kin yi aiki?" Sai shi ke nan, sai ta che "Sun sa ni ke nan na yi aiki." Sai sariki ya kashe matan gidansa duka. Da ya kashe, sai ya kirra jatuma, ya ba ta kaya, sai ya aura da yariniya ya zona da ita.

---

## 5

## The False Friend.

Wanni yaro ne da abokinsa. Sai ya che "Taffo ka raka ni gidan matana." Sai abokinsa ya tashi, ya raka shi. Sai suka kama hainya, suka yi ta taffiya. Sai suka zo gidan sarikuwansa, sai akache "A, marhabanku, marhabanku." Shi kuwa ya taffo da godiyansa, shi, mai-mata.

Shi ke nan, sai akakawo masa abinchi, sai ya che abokinsa ya chi, shi ba zaya chi ba, gidan matansa ne. Sai ya che "To." Sai akakawo masu abinchin ranan tsakka, sai ya che "Tashi mu chi," en ji aboki. Sai ya che "A, a, ka chi, ni ba zan chi ba, gidan matana ne." Sai ya chi abinshi. Sai akakawo kuma na mareche, sai ya ki kuma.

Sai tsakkan dare ya yi, sai yunwa ya kama shi, sai ya tada abokinsa, ya che "Ina jin yunwa, ga gero pal a gwona, ga igiya, bar en daura atsakkan dakin nan, em bi igiyan nan, en je en kariye tumu." Sai ya je, ya kariye tumunsa. Sai aboki da ya taffi, sai ya tsinchi igiya, ya daure a dakin sarikuwansa. Shi kuwa, da ya kariye tumu, yana biyo igiya har ya zo, ya shiga dakin sarikuwansa. Da ya zo, ya che Na je,

na kariye tumu, "ya che" mutanen nan banna sun yi gero, ina tumun geronsu kuma. Shi kuwa, sarikuwansa, yana kwanche, yana kallon sa, shi kuwa, yaro, ya che abokinsa ne. Sai ya tumi tumunsa du, ya kare, ya gassa, ya chi. Da ya chi, ya koshi, ya che "Abokina, enna ruwa?" Sai sarikuwansa ya nuna da hanu, ba ya bude baki ba, kadda ya shaida shi. Da ya sha ruwa kuma, sai ya che "Ba ni wuri en kwanche." Sai sarikuwan ya che "Samari, nan ba daki naku ne ba. Da ya yi leka, ya shaida sarikuwansa, sai ya fita woje, sai ya je ya dauke sirdinsa, ya hau godiyansa da dare, sai ya kama taffiya. Kafin gari ya waye ya yi kussa da garinsu. Lokachin nan da safi, sai godiyansa sai ta busheshi, sai ta koma chan gidan sarikuwanshi. Doki da ya komo gidan sarikuwansa, sai suka kama, suka daure.

Sai uban yariniya ya fito, sai ya zo ya bude jikkan nan na sirdin doki, sai ya sa hanu. Ashe, da dare, abokin yaro ya chikka rabbi da kashi. Sarikuwansa da ya sa hanu sai ya fida chiniyan kaza. Da ya koma ya sa hanu kuma, sai kashi ya kama hanu.

Shi yaro ba ya koma wurin matan ba, shi ko, ba ya zo ya kama godiyansa ba, duk sai ya tare, ya bari masu. Abokinsa, da safi, sai ya tashi abinshi.

Amana ba dadi ke nan wannan.

---

6

A Lie can give more Pain than a Spear.

Dila de ke nan, suka gamma da kura. En ya mika jikkinshi sai ya che "Daurewan magana ya fi na mashi chiwu." Sai kura ta che "Na mashi ya fi chiwu."

Sai ran nan dila ya taffi kasuwa, ya saye nakiya, sai ya taffi makunchen zaki da shi. Da zuwansa sai ya che "Gadanga, Wan Dowa, ga wanni abin marmari da na kawo maka." Sai ya ba shi nakiya. Sai zaki ya karbe, ya dandana, ya ji zaki, sai ya che "Mallamin Daji, enna ka samu wannan abu mai-zaki?" Sai ya che "A gidan kura na samu, kashenta ne, amma ba ta yarda ta ba ka, sai mu yara." Sai zaki ya che "Enna kura ta ke?" Sai ya che "Tana gida."

Sai zaki ya tashi zashi gidan kura. Da zuwansa, sai ya che mata "Yi mani kashi irin naki mai-dadi." Ta yi, ya dandana, ya ji ba dadi, ya che "A, a, ba wannan ba." Ta kuma yi

hakkanan, ya dandana, ya ji ba dadi, sai ya yi fushi, ya kama ta, ya matsa ta. Zaki yana matsan ta, kura tana yi ba dadi, har ya kussa kasshe ta. Sai ya bar ta, ya taffi.

Sai dila ya zo, ta che masa "Daurewan maganna ya fi na mashi chiwu." Ya che "Op kin gani ne?" Ta che "Na gani."

---

## 7

## The King who fulfilled his Promise to the Leper.

Makafo da kuturuwa suka yi aure. Da suka yi aure suka haife yaya dari, duk ba mai-taffiya achikkin su, dagga mai-jan-chikki sai mai-rafafe, sai wanda ba ya iya tashi.

Da suka haife yaya dari, sai yaki ya zo ya kama garin. Sai namijin ya che "ki dauke hamsin, ni kuma en dauke hamsin, mu je, mu boye." Sai mata ta dauke daya ta gwoya, ta dauke daya ta saka a gabbanta. Shi kuwa mijin, ya dauke daya ya aje a kafadansa daya, ya dauke daya kuma ya saka a wanchan kafada, ya dauke daya kuma ya sa a gabbansa. Sai suka fitto da yaya biyal, suka soma gudu. Sai dowakin yaki suka gan su, sai dowaki suka bi su aguje, su kuwa suka dauke gudu. Sai suka je bakin kogi, namijin sai ya fada, ya zamma dorina, yayan kuma suka zamma yayan dorina; mata kuwa ta fada, ta zamma kada da yayanta.

Lokachin nan mutanen yaki suka zo suka tsaya a bakin rafi. Sai dorina ya zo ya ture ruwa da kirijinsa, ruwa ya dauke doki ashirin, mutane suka tsere daket. Lokachin nan saura suka koma wurin uwar yaki, suka che "Ga wanni ya gagara achikkin ruwa." Sai sariki ya che "Mutum daya ya iya gagara?" Sai ya che "Mu je, en gan shi." Sai sariki ya kama hainya, ya zo bakin kogi. Da ya zo, ya tsaya, dorina sai ya debo ruwa ya zubar masu, da doki kaman hamsin duk suka mutu. Lokachin nan sai uwar yaki ya che "Ai, wannan ba mutum ba ne, iblisi ne." Sai suka tashi, suka je, suka koma akan garin.

Su ko, suka fitto, suka zamma mutane. Suka je, suka boye yayansu chan a wanchan ketare. Sai suka komo suka bi yaki abaya, suka shiga chikkin gari. Sai suka je, suka gaya ma sarikinsu, suka che "Ga yayamu dari ba biyal, talafi na Allah da Ma'aike, amma mu zamu gudu." Sai ya che "To." Sai su, suka tashi, suka gudu.

Sai yaki kuwa ya zo, ya chi garin. Da ya ga yaki ya chi

gari, sariki sai ya che "Amana na Allah da wiya gare shi." To, zaya tsere da nasa na chikkinsa ya bar na kuturu—ko zaya chikka alkawali da ya yi? Sai ya bar nasa ya sa nasu yayan dari ba biyal akan doki, ya gudu da su. Duk akazo akachi gidansa, akadebe sarai.

Lokachin nan, sai abayan yaki kuma, makafo da kuturu suka komo da yayansu biyal, sariki kuwa ya kawo dari ba biyal, ya che "Ga yayanku." Lokachin nan sariki dagga shi sai ransa, bu shi da komi. Lokachin nan su yaya sun yi girima, sai yariniya guda daya ta yi keyau achikkinsu, sai sariki ya che yana so aba shi ya aura. Suka che sun ba shi.

Da ya aure ta, yariniyan, da safi ta kan yi kashi zambar goma, da mareche ta kan yi na zambar ashirin. Sariki kuma ya saye bayi, duk ya chikka gidansa, har gida ya fi na da. Sai surukuta ya zamma atsakaninsu, da shi da kuturu.

---

## 8

### The Friendly Lion and the Youth and his Wife.

Wannan ne, mahalbe ne. En ya taffi dauji sai ya kasshe naman dauji. Ya dauko ya chi, da shi da matansa. Sai ran nan, sai ya komo, ba ya kasshi komi ba, sai yunwa. Sai da safi ya taffi, yana yawon halbe ba ya samu komi ba, sai ya kama babe, ya nadda achikkin kunnen itache, ya zo da shi gida, ya aje. Da matansa ta ga kunnen, sai ta che "Ko nama ne," sai ta fura wuta, ta sa tukuniya, sai ta bude kunnen nan, sai babe ya tashi "Bup," ya taffi. Sai ta che da mijinta "Abinda ka kawo ya taffi." Sai ya zage ta, ya che "Ki taffi, inda ya shiga duk ki bi shi, ki kawo." Matan kuwa da chikki. Sai ta taffi ta kama hainya, ta bi baben nan. Da zata kama, sai ya tashi, ya taffi, sai ta bi shi. Da zata kama sai ya tashi, ya taffi, sai ta bi shi.

Kullum hakka, sai ta gaji, dare ya yi kuma. Sai ta nema kogon itache, ta shiga, sai haifuwa ya kama ta, sai ta haife nan a kogon itache, da namiji. Sai ta gwoye shi, ta taffi neman abinchi. Suna nan, suna zone, sai dan ya yi wayo kadan, yana taffiya wurin zaki, zaki kuwa da danta. En de zaki ta kawo nama, sai yaro sai ya dauke nasa ya kai ma uwansa a kogon itache, sai dan zaki ya saba da su, suna wasa.

Sai ran nan, sai uwar zaki da ta taffi farauta, sai ta ga uwar yaro, sai ta damfaro kan ta, ta kasshe, sai ta dauke gawan, ta zo gida. Sai dan zaki ya san ta, ya ki chi, sai ya gaya wa yaro, sai

suka haka rami, suka sa. Sai ran nan sai dan zaki ya yi girima, sai ya kasshe uwansa, ya gaya wa yaro. Sai suka yi wanni rami kuwa, suka sa.

Sai ran nan sai yaro ya che da dan zaki "Ni zan taffi gari zan yi aure." Sai dan zaki ya che "To." Yaro ya che "Ina so riga, ina so wando, da rawani kuma, da kurdi, da dukiya." Sai dan zaki ya che "To." Sai ya taffi bakin dauji, ya kwanto a hainya. Da fatake suna wuchewa sai ya damfaro kan su, ya kasshe, suka wa'atse, suka bar kaya. Sai zaki ya dauke, ya kai ma yaro, yaro kuwa ya dauke ya taffi gari.

Da ya zo gari anyi mashi aure, yana zone, zaki kuwa yana zuwa da da dare, yana shiga gidan yaro. Sai ran nan sai matan yaro ta gan shi, sai ta ji tsoro, sai ta gudu, tana che "Da zaki a gidam mu." Sai zaki zuchiyansa ya bache, sai ya taffi dauji, ya zo ya kwanta akassan itache. Sai da zaya taffi, ya gaya ma yaro "En ka ji na yi kuka so-daya ka san na mutu ne, en de ka ji so-biyu, ka san ina da rai kuma." Sai yaro ya che "To." Sai ya taffi, shi zaki.

Sai ya ji kukan zaki so-daya, ya san zaki ya mutu sai ya tashi, ya bi sawun zaki, ya zo wurin, ya iske zaki ya mutu. Sai ya che "Tun zaki ba shi da rai, raina ba ya yi mani wanni anfani." Sai ya dauke wukansa, ya soke chikkinsa, sai ya mutu akan zaki. Alkawali ya chikka ke nan.

---

## 9

### HOWEVER POOR YOU ARE, THERE IS SOMEONE EVEN WORSE OFF.

Wanni mutum ne, tsiyata ta yi masa yawa, ba shi da abinchi, ba shi da riga, ba shi da komi sai walke. Sai ya tashi, ya je wurin sariki, ya che "Zaki," ya che "amma ni na gaji da rai, sai ka kasshe ni, ba ni da abinchi, ba ni da riga, ba ni da komi sai walke, tsiyata ta yi mani yawa." Sai sariki ya che "To," sai ya sa mutanensa su taffi da shi zasu kasshe.

Sai da zasu kasshe, sai wanni matsiyachi, yana zona tsirara, ya gani, ya che "Ni ma, abinda ni ke so, sai da kuka kasshe mutumen nan sai ku ba ni walkensa." Sai wanchan ya ji, ya che "Ku barri, kadda ku kasshe ni, ku koma da ni wurin sariki, ina so en yi magana da shi." Sai akakoma da shi wurin sariki, akache "To, mutumen nan shina da magana." Sai sariki ya che "To, shi zo, shi yi, en ji." Sai ya che "To, sai ka bar ni da rai en taffi, yau na ga wanni ya fi ni tsiyata,

shina son walkena. To, shi ne ya sa na che akoma da ni wurinka. Ba ni so en mutu ba." Sai sariki ya che "To, taffi abinka, ka gode, ka ga wanni ya fi ka tsiyata."

Ya kare ke nan wannan.

---

## 10

### The Boy, the Girl, and Dodo.

Wanni sauraye ya kan taffi wanni kauye ya dauko yariniya ya kwana da ita. To tsakanin su kuwa, akwai wanni kogi. Ran nan da suka zo bakin kogi da yariniya, ya ga ruwa ya karu. Sai ya che "Tsaya, en shiga, en duba ko da zurifi, ko ko babu zurifi." Ya zo ya shiga zaya fitta ke nan, sai ya je baban Dodo ya che "Kun kama shi?" Sai yayan Dodo sun zo sun chafe shi a kaffa, sai ya subche, ya fitta. Sai ya che "Ku kiyale shi kauwi, zaya komo."

Da ya ketare sai ya ji kukan kura, kaman ashirin suna zuwa kan yariniyan nan. To, ga kura suna wanchan ketare, ga Dodo achikkin ruwa. Zaya kama hainya ya tsere ya bar yariniya, ko zaya koma a wurinta? Sai ya che shi kaka zaya yi? Sai ya che "Amma mutum zaya mutu ya mutu akan yanshi." Lakachin nan sai ya fada ruwa, ya fitta, ya dauke yariniya.

Da suna komowa, sai Dodo ya rikke shi, da shi da yariniya duk suka rikke su, sai suka nitse. Ya yi kukuwa da su kwana kaman ashirin, iyayen yaro suka neme shi, ba sun gan shi ba, iyayen yariniya kuma suka neme ta, ba sun gan ta ba. Sai kwana ashirin da daya ya fi su karifi, sai ya fitto dagga ruwa duk da yariniya, sai ya kai ta har gidansu.

Suka murna.

---

## 11

### Falsehood is more Profitable than Truth.

Waddansu mutane ne, da Sarikin Kariya da Sarikin Gaskiya. Suka tashi, suna taffiya, Sarikin Kariya ya che da Sarikin Gaskiya shi ya nema masu abinchi yau. Suka taffi suka kwana a gari, ba suka samu komi su chi ba. Da safi suka tashi, suka kama turaba, Sarikin Gaskiya ya che da Sarikin

Kariya "Garinda zamu kwana, kai ka nema mamu abinchi." Sarikin Kariya ya che "To."

Sai suka tashi suka taffi, suka taffi baban gari. Sai uwar sarikin garin nan ta mutu, sai duk gari suna ta kuka, wai "Uwar Sariki ta mutu." Sai ya che "Mi ya sa ku ke yi kuka?" en ji Sarikin Kariya. Sai sun che "Uwar Sariki ta mutu." Ya che "Ku je, ku gaya wa sariki uwatasa ta'a fitto." Sai akache "Bakin nan enna su ke?" en ji sariki. Sai akache "Ga su nan." Sai akakawo baban gida akaba su.

Sai ya je da da dare, ya kama damafifito, irin kwaran nan da yana "kurururu," ya zo ya saka shi achikkin batta. Sai ya che aje, anuna masa kabari. Da ya je ya duba kabari, sai ya che "Du mutane su taffi." Sai ya bude bakin kabari kadan, sai ya kawo zirnako, ya saka achikki, sai ya birni bakin kaman na da. Sai ya kirro sariki, ya che ya zo ya sa kunnensa a jikkin kabari. Lokachin nan kwaron nan ina kurururu. Sai ya che "Ka ji, uwanka tana magana." Sai sariki ya tashi, ya dauko daki ya bai wa Sarikin Kariya, ya kawo mata ya ba shi. Gari duk suka fada murna, uwar sariki zata fitto.

Sai ya che da Sarakin gari ai, ubansa kuma ya mutu ko? Sai ya che "I, ya mutu." Sai ya che "To, ubanka ya rikka uwanka achikkin rami suna ta fada." Sai ya che "Ubanka en ya fitto zaya karbe maka sarautanka." Sai ya che uban kuma zaya kasshe shi. Sai ya gaya ma mutane duka, shi sarikin garin, sai suka hada dutsi akan kabari. Sai ya che "Kai, Sarikin Kariya, je ka, na ba ka dowakin nan." Sai ya che shi, uwansa kuma ba ya so ta fitto.

Ashe, kariya ta fi gaskiya achikkin duniyan nan.

---

## 12

### Virtue pays better than Greed.

Da Sarikin Keyau da Sarikin Makiyetata suka kama turaba, suna taffiya. Sai Sarikin Keta ya che "Sarikin Keyau, ka kawo abinchinka mu dinga chi har mu taffi." Suna taffiya, suna taffiya, sai abinchin Sarikin Keyauwawa ya kare. Sai ya che "Kai kuma, Sarakin Makiyetata kawo abinchinka." Sai Sarikin Keta sai ya hanna, sai Sarikin Keyau ya rame.

Suna taffiya, suna taffiya, sai ran nan suna kwana a gindin baban bishiya. Suna kwanche da dare. Ashe, da gidan tsuntsu asamman bishiya. Sai tsuntsun nan sai ya che "Gainyen bishiyan

nan"—Sarikin Makiyetata kuwa yana barchi, Sarikin Keyau yunwa ya kama shi, ba ya samu dama zaya yi barchi ba—sai tsuntsun nan ya che "Bishiyan nan, wanda ya debe gainyensa," sai ya che "en ya shafa idon makafo sai ya bude." Sai Sarikin Keyauwawa ya tashi da hankali, sai ya je, ya fige gainyen bishiyan nan, ina zuba achikkin jikkansa. Yana fisgen gainye, yana jefa achikkin jikkansa kuma har gari ya waye.

Suka tashi, suka kama turaba, suka taffi wanni gari. Ashe, dan sarikin garin nan makafo ne. Sai Sarikin Keyau ya je wurin sarikin gari, sai ya che aneme masa makafo ya bude masa ido. Sai ya che "Kai ka iya maganin budewar ido?" Sai ya che "Na iya." Sai ya che "To, ga dana makafo ne." Sai ya che "Nawa zam ba ka ka bude min idon dana?" Sai ya che "Sai zambar dubu." Sai ya che "To, sai da safi."

Da gari ya waye, sai ya che akawo su wanni daki, su biyu, dagga shi sai dan sariki. Sai akakawo su wanni daki. Sai ya che aba shi ruwa kadan achikkin kasko. Sai ya debe magani, ya zuba. Sai ya dauko, ya goge idon makafo, sai ido ya bude. Sai sarikin gari ya che "Tun da ka bude min idon dana," shi zaya yi mashi madaki. Sai akayi masa madakin gari, rabin gari duk ya komo wurin madaki. Shi ko, sai ya dauke Sarikin Makiyetata, ya zo ya yanke shi.

---

## 13

### The Victim does not always see the Joke.

Wannan de barawo ne, shina zamma da matansa. En de ya yi sata a gari, sai ya kawo mata. Suna nan, suna zone, sai ran nan sai farin wata na chi kaman rana. Sai mata ta che "To, ga wannan farin wata ya yi dadin taffiya, zaka zona a gida ne?" Sai miji ya che "To na taffi." Sai ya tashi, ya taffi gidan surukinsa, shi ko uban, shina da wanni baban rago, duk garin ba wanni rago kamansa. Sai barawo ya taffi ya dauko shi, ya kai ma matansa, ya che "To, ga abinda Allah ya ba mu yau." Sai matan ta che "To amma ayanka shi yanzu, kadda gari ya waye mai-rago shi gan shi, shi sani nashi ne." Sai ya che "To," ya yanka, ya fide, ya yanyanka nama.

Sai gari ya waye da safi, matan ta ga patan rago kaman patan ragon ubanta, sai ta che da mijin "Kai, Mai-Gida, enna ka samu ragon nan, ko ragon ubana ne?" Sai ya che "Kai, ragon ubanki ne kadai a garin nan? Ai ragon nan na kama

ne kauwi." Sai ta che "To, na ji." Sai da suna zone, sarakuwan barawo ta zo, ta che da matan "Ke, ba kin ji labari ba? Jiya da dare wanni barawo ya shiga gidammu, ya dauke ragon ubanki." Sai yar ta che "To." Sai da uwanta ta taffi, ta che "Kai de, ka sani sarai ragon surukinka ne, sai ka taffi ka sache, ka che ba nasa ne ba." Sai tana kuka, tana hawaye. Sai ya che "To, ba ke kin che mani en taffi en yi sato ba? Ke de, da akayi sata a gidan wanni, da ba kin yi kuka ba, sai da kin san ragon ubanki ne." Sai ya che "Ashe, wanzami ba ya so ayi masa aski." Sai ta che "To, zuchiyana ya bache." Sai ta fitta dagga gidansa, ta dawo gidan iyayenta.

---

## 14

### Dodo, the Robber, and the Magic Door.

Dodo ke nan, shina nan, shina yawo, shina neman mutane a dauji. Ya kama wata mache, ya zo ya aje, ya aura, tana nan a wurinshi.

Sai kanuwarta ta che zata taffi wurin yaruwanta. Sai ta dauke duma, ta shuka, ta che inda yarta ta ke dumankai ya kai ta wurinta. Sai duma ya taffi kofan dakinta, sai yan ta che "Mi ya kawo ki ye?" Sai ta che "Na zona shekara da shekaru ban gan ki ba, shi ne na sa dumankai ya kawo ni wurinki." Ta che "To, ga Dodo shina chin mutane." Sai ta che "To, yanzu zan yi yaya ne da ke?" Sai ta dauke ta, ta sa ta rumbun auduga. Sai Dodo da zuwan shi ya che "Ambashira, yau kin samu mutum a angane?" Sai ta che "Ni ne, ka gaji da ni zaka kasshe ni ka futa?" Sai Dodo ya yi shiru. Sai da safi ya yi ta daura ma kanuwa kaya, sai ta che ta taffi gida, ta kwana bakwai, ta komo.

Kwana bakwai ta yi, kanuwan ta komo, Dodo yana dauji, suka kwana. Sai gari ya waye sai suka daura kaya, suka taffi, suka haye kogi, da zasu fitta sai Ambashira ta yi kashi a daki. Dodo ya komo dauji, ya che "Ambashira." Sai kashi ya amsa. Sai Dodo ya shiga daki, ya taffi ba ya ga kowa ba sai kashi. Sai ya kama turaba, ya bi sawunsu. Dodo ya iske su sun haye kogi, sai Dodo ya tsaya wankai ketare, sai ya komo da baya.

Sai su matan suka gammu da wanni barawo, wai zashi zo shi yi sata a gidan Dodo. Sai sun che "En ka taffi ka che da kofa 'Zirka bude,' en ka yi sata ka fitta, ka che 'Zirka gum-

gum.'" Ya taffi ya che "Zirka bude," sai kofa ya bude, sai ya shiga, ya yi sata. Da zaya fitta sai ya manta da magana, ya che "Zirka gumgum," sai kofa ta mannu da bango. Ya yi, ya yi ya fitta, ya gagare shi.

Sai dagga chan suka zo, su ke waka wai "Ma-haukachin Barawo, mun ba ka sata, ba mun ba ka mantuwa ba." Sai mata suka taffi abinsu. Dodo ya taffi, ya samu barawo a daki, ya kasshe, ya kiyafe namanshi. Sai naman ya kiyafu, sai ya zo ya chi.

---

## 15

### The Deceitful Spider, The Half-Man, and the Rubber Girl.

Gizzo ke nan ya che a'auna masa gujiya. Ya che "Abare, adaffa." Sai akabare akadaffa akasa gishiri da mai, ya che zaya taffi ya yi shuka.

Sai ya dauke galma, ya samu wurin ennuwa maisainyi kussa da ruwa. Sai ya chi ya koshi, ya sha ruwa, ya kwanta, ya yi barchi. Da ya tashi, sai ya dibi tabbo, ya shafa a jikkinshi. Sai ya zo gun matansa, ya che abashi ruwan wanka, ya dawo dagga wurin aiki.

Ananan, ananan, sai kwanakin kakan gujiya ya yi, sai matan ta che ta ga gujiya a gidan kowa ta yi keyau, ita wanda mijinta ya shuka ta nuna yanzu. Sai ta che tana so ta je gwona ta yi gino. Sai ya che "A, a, ba ke kika shuka mani gujiya ba, ni zan taffi en yi tono." Ashe zaya taffi yin sata wurin barin mutum. Sai ya taffi, ya sato gujiyan, ya kawo gun mata.

Sai barin mutum ya zo ya ga anyi mashi sata, ya che zaya yi tarko da buduruwan danko, ya kama. Sai gizzo ya zo ya ga buduruwa da keyau, ga wiya, ga mama. Sai ya zo ya tabba mama, ya che "Buduruwa"! Sai danko ya kama shi. Sai ya che "A, Buduruwa, sakke ni manna, ko kina son na ne?" Sai ya sa dayan hanu kuma, sai hanu ya kame. Sai ya che "Ku yammata kuna son mutum, sai ku rikke shi? Sai en haure ki." Sai ya haura kaffa daya, danko kuwa ya kama shi. Sai ya yi fushi kuma, ya che "Dan-durin uwanki." Ya haura kuma da wanchan kaffa. Da ya haura, danko ya kama shi duka, sai doro. Sai ya che "To, na yi maki tunkwiye." Sai ya yi mata tunkwiye, sai kai ya kame.

Dagga chan, barin mutum ya gani, sai ya che "Madallah."

Ya samo tsumangiya na tsamiya, sai ya sa ta a wuta, sai ya kawo main shanu, ya shafa. Sai ya zo ya fiyada gizzo nan, sai baya ya kware, duk jikkinshi ya kware. Sa'anan ya kwanche gizzo a danko. Ya che "Kai Gizzo," en ji barin mutum, "en ka kara zuwa nan, ni, barin mutum, en kasshe ka."

---

## 16

### The Rich Mallam, the Thieving Spider, and the Hyæna.

Wannan de, mallami ne, shina da dukiya dayawa, da shanu, da dowaki, da awaki, duk yana da su. Sai ran nan, gizzo ya zo wurinshi, ya che "Salla'am alaikum," sai mallam ya che "Alaika salla'am." Sai ya che "Amma ina so en yi maka kiwon awaki, na shara maka wurin tumkiya kuma." Sai mallam ya che "To," ya yarda.

Suna nan, suna zone, kullum da safi gizzo ya kan dauke kashin dabobi ya kan zubar, yu kan share wurin. Gizzo de, da ya zo ya dauko baban kwando, ya che zaya sa shaara achikki. Ashe, kullum da safi sai ya yanke akwiya, ya sa achikki, ya rufe da shaara, sai ya kai dauji, ya chi.

Sai ran nan, mallami ya gani dabobi suna karewa, sai ya che "Ko gizzo yana yi mani wayo ne?" Sai ya che "To, bar en dube shi dakeyau." Da safi kuma, gizzo ya yanke baban bunsuru, ya sa a kwando, sai ya faskara daukawa. Sai mallami ya gani, sai ya zo ya che "Bar en dauke ka." Sai da ya ji nauyinsa, ya che "Sai aragi." Sai gizzo ya che "A, a, na iya de, kadda aragi." Sai mallami ya che "Ba ka iya ba hakka." Sai ya sa hanu, ya ragi shara, sai ya tabba gangan baban bunsuru, ya fitta da shi. Da ya fitta da shi, sai ya che "Ashe, hakka kana yi mani?" Sai ya kama shi, ya daure shi a kofar garike, ya buge shi, ya barri.

Sai da da dare, kura ta zo. Da ta zo ta gan shi, sai ta che "Mi ya sa akadaure ka?" Sai gizzo ya che, "Op, ina yi ma mallamin nan kiwo." Kullum ina kissan akwiya da ya ba ni, ina chi, amma na che na gaji, zani gudu "Shi ne ya sa mallami ya daure ni kadda en gudu." Sai kura makwadaye ta che "Ashe, mutum yana da koshi a gidan mallami har ya gaji da abinchi?" Sai ta che "To, ni ma, ina so koshi hakka." Sai gizzo ya che "Op, wannan mai-sauke ne, sai ki zo ki kunche ni, ni fa, en daure ki." Sai kura ta che "To." Sai ta zo ta kunche shi, shi kuwa gizzo, ya daure ta. Sai ya che "To, zani dauji." Sai ya taffi.

Da safi, mallami ya zo, sai ya ga kura. Sai ya buge ta, yana bugen ta har ta kusa mutuwa. Sai ta kubche, ta gudu, ta je dauji tana neman gizzo.

Shi ke nan, da gizzo da kura duka suka tsere.

---

## 17

### Little Fool, or the Biter Bit.

Waddansu suna da da sunanshi Dan Wawa. Sai da suka taffi gwona, suka komo, suka che "Ba ka daffa mamu wake ba?" Sai ya che "A, a, ba kun che adaffa muku ba." Sai suka che "To, gobe ka daffa mamu wake."

Da gari ya waye, sai ya dauke kwayan wake guda daya, ya sa achikkin randa, ya girika. Da suka dawo, suka ga randa baba, suka che "Dan Wawa, mi zamu yi da wanchan wake?" Sai suka zo, suka bude, suka gani kwayan wake guda daya achikki ya tosa, sai suka che "A, Dan Wawa, wake daya ka daffa mamu?" Sai ya che "Ai, ba ku che adaffa 'wakake' ba, 'wake' kuka che." Sai suka che "To, gobe adaffa mamu wakake."

Da gari ya waye, sai ya shiga rumbu, ya yi gaya, akadaffa wake duka. Sai suka zo, suka iske wake tun dagga kofar gida har chikkin gida. Shi ke nan, sai suka che "Dan Wawa, mi zamu yi da wake dayawa hakka?" Sai ya che "A, ku kadai ne masu-chi? A, asamu masu-taya ku." Sai suka che "To." Sai ya taffi daji, ya samu barewa goma, sai ya che "To, ga masu-taya ku chi." Shi ke nan, da gari ya waye kuwa, sai suka taffi gwona, suka bar shi da baraye. Shi ke nan sai ga gizzo ya zo fatauchi, ya che Salla'am alaikum." Sai Dan Wawa ya che mashi "marhaba." Sai ya che "Yanzu baraye naku, sai ayanke su," en ji gizzo, "ni kuma en dauke nama en yi maka fatauchi." Sai ya che "To." Sai akayanke baraye duka, akasa nama a taiki, akasa a jikkan gizzo.

Sai Dan Wawa ya che "A, taikin nan ba ya chikka ba," ya che "yanzu kai ka tsaya a gida, ka jira iyayena sun je gwona, ni ko en taffi da jakuna naka agabba, en je en sami nama en chikka taiki." Sai gizzo ya che "A, Dan Wawa, habba, ka san amana ba ta yi hakka ba." Sai Dan Wawa ya che "Ai, ni ba zan ki amana ba." Sai ya che "To."

Dan Wawa da ya taffi da jakai, ya sauke taiki sai ya kwashe toroso, ya chikka taiki, ya kawo hanta, ya chikka baki. Sai

ya koma da jakai, ya che "To, taiki yanzu sun chikka, fatauchi ya faye riba." Sai ya che "To, na taffi," en ji gizzo. Yana taffiya sai jakuna suna che "Toroso, toroso, toroso." Sai ya che "Kai Yan-durin Uwarku, ku fadi 'Da sauka, da sauka.'" Shi ke nan, sai ya taffi gida, ya che da matansa "Massa, massa ki sauke jakuna." Sai ta sauke su. Sai mage ta che "Um yau," sai gizzo ya che "Gafara, ko hanta ya iske ki koshi?" Sai ya sa hanu achikkin taiki ya chiri hanta, ya ba mage, sai ta chainye.

Da ya sake sa hanu, sai achikkin toroso. Sai gizzo ya che "Op, Dan Wawa ya zalumche ni garin wayonshi, har gari ya waye mashi." Sai gizzo ya che "Allah ya issa."

---

## 18

### How the Spider ate the Hyæna-Cubs' Food.

Gizzo ya tashi, ya taffi dakin kura, ya tarada kura ta taffi yawo, sai yayan kura achikki. Ya che "Sunanka wa?" Ya che "Sunana Mohammedu." Wannan kuwa ya che "Sunanka wa?" Ya che "Sunana Isa." Wannan kuwa ya che sunansa Nata'ala. Ya che "To, ga shi, kura ta che en zo en zona da ku, amma sunana 'Na-ku-duka.'" Sai kura en ta kawo abinchi, ta kan che "Ga shi, naku duka." Sai gizzo ya che "To, nawa ne kadai, kun ji abinda uwarmu ta che." Sai gizzo ya chainye duka.

Suka yi kaman wata guda suna yi hakkanan, gizzo yana chainye abinchi, sai yayan kura duk suka lalache. Sai kura ta che "Kai, ku fitto Yayana, en gan ku." Sai suka fitto, duk sun rami. Sai ta che "Mi ya same ku Yayana ku ke ramewa?" Sai sun che "A, ba kin ba mu abinchi." Ta che "Enna abinda ni ke ba ku ku duka?" Sai sun che "A, Naku-Duka ya chainye, ga shi chan." Sai ta che "Enna Naku-Duka ya ke? Shi fitto en gan shi." Shi kuwa ya mika kunnensa awoje, ya che "Soma rikke mani takalamina har en fitto, ki gan ni." Ita kuwa da ta kama kunnen, sai ta jefa abaya da fushi. Shi kuwa dagga chan, sai ya tashi ya gudu. Sai ta che "Enna Naku-Duka ne?" Sai yayanta suka che "Ai, shi ne kika yar achan abayan ki."

Shi kuwa, gizzo, ya tashi, ya taffi wurin kare yana saka, sai ya je ya zona wurinshi. Sai kura ta taffo, tana neman gizzo, sai ta zo ta tarada kare da gizzo azone. Sai ta che "Achik-

kin ku wa na koro?" Sai gizzo ya che "Duba bakin mai-lumfashi dayawa, ai shi ne ya gudu." Sai kura ta dirka kare aguje, shi kuma gizzo ya gudu, kare ya gudu, sai suka tsere na kura dukan su biyu.

---

## 19

### The Slave who was wiser than the King.

Wanni sariki ke nan, shina da bayinshi uku mazza. Suna da aurensu, suka haife yaya uku, kowanni ya haife danshi. Akasa ma daya suna Ma-Ki-Gani, akache ma daya Allah-Keyauta, sunan na-uku kuma Ka-Fi-Sariki-Wayo. Sai akakai ma sariki ya gani.

Suna nan suna nan, sai suka girima. Da suka taffi gun sariki, akakawo damin dawa akaba Ma-ki-gani, akaba dami ma Allah-Keyauta, sai akakawo damin kaikai akaba Ka-Fi-Sariki-Wayo. Sai ya che "To, badi, kowa ya kawo dami dari uku uku," en ji sariki. Sai suka che "To." Suka taffi.

Da suka yi shekara, kaka ta yi, Ma-Ki-Gani ya kawo dami dari uku, Allah-Keyauta ya kawo dami dari uku, Ka-Fi-Sariki-Wayo ya kawo kwandon dusa. Sai akazo wurin sariki. Ma-Ki-Gani ya che "Ga dami dari uku." Allah-Keyauta ya che "Ga dami dari uku." Ka-Fi-Sariki-Wayo ya che "Ni kuma, ga nawa." Sariki ya che "Domi ba ka kawo dami dari uku ba?" Sai ya che "A, daminda ka ba ni na kaikai na shuka, abinda ya tsiro ke nan." Sai sariki ya che "To, na ji." Sai ya kawo karsana ya ba Ma-Ki-Gani, ya kawo karsana ya ba Allah-Keyauta, ya kawo bijimi ya ba Ka-Fi-Sariki-Wayo.

Da badi ya yi, Ma-Ki-Gani ya kawo yayan shanu biyu. Allah-Keyauta ya kawo yayan shanu biyu. Ka-Fi-Sariki-Wayo ya dauke gatari, ya sa a wiya. Da wanni itache busashe a bayan gidan sariki, ya hau, yana saran itache. Sai sariki ya che "A, ga kowa ya kawo nasa shanu biyu, enna Ka-Fi-Sariki-Wayo?" Sai akache "A, ga wanni kaman shi yana saran itache." Sai akache "Ai, shi ne." Akache "Ka-Fi-Sariki-Wayo, mi ka ke yi anan?" Sai ya che "Ina sara ma ubana itache, ya haifu." Sai sariki ya che "Ashe, miji na haifuwa?" Sai Ka-Fi-Sarikin-Wayo ya che "Ashe, ka sani miji ba shi haifuwa, ka ba ni namiji sai ka che akawo maka yayan shanu biyu?"

Sai sariki ya che "A, mi zan yi da wannan yaro?" Sai suka che "Op, sai akasshe shi." Akache "Aba shi rigan saki, da

wandon saki, da rawani mai-bakin-cheriki," en ji fadawa. Suka che ku zabi doki mai-keyau, ku hada masa kaya." Suka che dan sariki ya sa tsofan riga, da tsofan wando, da tsofan rawani. Akache "Asa su su yi taffiya, asa yan-bindiga agabba, su je, su kwanto a hainya. Ache masu wanda sun gani da kayan addo su kasshe shi, shi ne Ka-Fi-Sariki-Wayo."

To, shi ko, da ya ji hakkanan, sai ya sa wanni mutum agabba da goran giya goma, da goram bakin ruwa goma. Da suka taffi suka iske wurin, Ka-Fi-Sariki-Wayo ya che da dan sariki "Barri mu sha ruwa." Sai ya karba goran giya ya ba dan sariki, shi ya sha ruwa. To, Dan sariki, ya fara tangadi. Da suka taffi gabba, sai ya che "Mu sake shan ruwa." Sai suka sake sha. Da ya sha, dan sariki ya bugu. Sai Ka-Fi-Sariki-Wayo ya che "To, Dan Sariki, ba za'arena ka ba," ya che "Karbe rigan sakin nan ka sa, karbe wandon sakin nan ka sa, karbe rawanin nan ka sa." Ya che "En sauka wannan doki ka hau." Sai ya che "To." Sai ya ba shi doki da kaya duka, sai ya sa riga mara-keyau, ya hau doki mara-keyau.

Suka zo, suka iske bayin sariki masu-bindiga. Da suka zo, suka halbe dan sariki, ya mutu. Ka-Fi-Sariki-Wayo da ya yi sukuwa ya kai ma sariki jinjina. Sai akache "Wanene kaman Ka-Fi-Sariki-Wayo?" Sai ya che "Ni ne." Sai sariki ya tashi zaya kama, sai ya zamma kwado. Sai sariki ya zamma machiji zaya hadiye shi. Sai Ka-Fi-Sariki-Wayo ya zamma bera. Sai sariki ya zamma mage. Ka-Fi-Sariki-Wayo ya zamma jira. Sai sariki ya zamma karamata. Da zuwan jira ya iske tsofuwa tana shara gida, sai ya fada a ido, sai ya zamma bakin ido, sariki kuma ya zamma gira. Sai suka zona hakkanan, ba ya iya fitto kadda sariki ya kama shi.

Iyaka ke nan.

---

## 20

### The Cock by his Wit saves his Skin.

Zakara de ke nan, ya tashi zashi gaisuwar masu-kukan mutuwa. Da yana taffiya, sai ya gammu da muzuru, ya che "Enna zaka?" Ya che "Zani gaisuwar mutuwa." Ya che "Enna?" Ya che "A gidan dangi." Sai muzuru ya che "Ashe, za'ayi biyu?" Ya che "A, a, ba biyu ne ko uku, ina zone da karc ne."

Suna taffiya, sai muzuru ya che "Ashe, Zakara, da ban dariya ka ke, amma ni, na taffi abina." Ya taffi, zakara kuma ya taffi.

## 21

### The Hen seeks a Charm from the Wild Cat.

Kaza ta taffi wurin muzuru, ta che tana neman maganin haifuwa. Sai muzuru ya che "Taffi ki fige kainki, ki sa gishiri da barkono, ki zo, em ba ki maganin haifuwa." Sai ya fura wuta, ya sa gumagumai, wuta ya kama. Sai ta taffi, ta fige, ta shafe gishiri da barkono, ta komo, ta che "To, na zo, ka ba ni maganin haifuwa." Sai ya che "To, mu je wurin wutan nan, kina gabba, ina biya da ke, muna kewoye wuta. Kina chewa 'Maganin haifuwa ni ke nema, maganin haifuwa ni ke nema.'"

Sai suka je wurin wuta, suna kewoye, muzuru na baya, sai ya dauke ta, ya saka wuta, sai ya chainye.

---

## 22

### The Battle between the Beasts and the Birds.

Da zakara da giwa suna gida daya. Giwa ta tashi, ta kama itachen kofar zakara ta kariye. Zakara ya tashi, ya zo ya kwashe shaara, ya zubar mata achikkin dakinta. Sa'anan giwa ta che "Zakara ina son yaki da kai." Zakara ya che "To, kowa shi gaya danginsu." Giwa ta taffi ta gaya naman daji duk. Zakara kuwa ya gaya tsuntsu duk. Sa'anan suka zo wurin yaki. Shafo ya che "Ni ne sarikin yakinka."

Akasa kura ta duba taronsu ya taru. Sa'anan akache "To Jimina, ki shigi, ki taffi ki gani nasu taru ya yi." Ashe kura tana zuwa, jimina kuwa tana zuwa, suka zo suka ga junansu. Kura ta che "Jimina, taronku ya yi?" Jimina ta che "Ku fa, naku ya yi?" Ta che "I." Sa'anan jimina ta che "Ki koma ki fada masu, ni zan komo en fada ma namu." Da jimina ta juya, kura ta gani nama a gusun jimina, ta ji kwadaye ta che "Jimina tsaya, mu yi namu yaki ni da ke." Jimina ta che "To, ki buge ni so-uku, ni kuma en rama so-uku." Kura ta zo ta buga jimina so-uku. Jimina ta tashi ta che "Bar en rama." Ta zo ta buge ta da fukafukenta, ta halbe ta da kaffa, ta sare ta da baki. Kura ta che "So-uku ke nan." Ita kuwa ta che "A, a, sai so-daya." Ta sake bugen ta da baki ta chiri mata ido, sa'anan ta che "Mu koma." Naman daji da suka ga kura ba ido, sun che "Kaka?"

Ta che "Kun ga anchiri mani idanu, ba mu iya yakinsu

kuma ba." Tsoro ya rigaya ya kama ta. Sa'anan akache "To, mu taffi."

Suka zo yaki baki daya. Sa'anan zakara ya che "Mu yi yaki." Sa'anan sarikin yakin tsuntsu ya zo, ya yi ma zakara jinjina. Suka zo garin yaki. Ya dauke tsaiwa, ya dauke kwain kaza, ya nemi giwa, ya passa mata kwai a kai. Shafo ya che "Kain giwa ya passu, kain giwa ya passu." Giwa ta tabba kai da hanun hanchi, ta che "Ashe, an passhe mani kai." Sa'anan ya jefa mata tsaiwa, ya che "Hanji ya fitta, Hanji ya fitta." Da naman daji suka ji, suka gani, suka gudu duk.

Sai kuma zakara ya koma gida abinsa. Sa'anan ya che "Kai shafo, zam ba ka goron yaki, koyaushi matata ta haifu ka rikka zuwa, ka dauka da daya, gorona da ku ke nan."

---

## 23

### The Goat frightens the Hyæna.

Wannan de, akwiya ne, tana zone da danta namiji. Sai ran nan, suka tashi suka taffi yawo, sai suka bata hainya. Rana kuwa ya kussa fadi. Sai suka ga wanni gida agabba. Sai suka zo, suka iske kura a gida, tana magana da yaranta. Sai ta che "Marhabanku."

Sai da suka zo, suna zanche, sai kura ta tashi ta debo hatsi ta yi ta nika, sai akwiya ta che mata "Kura, bar en karbe ki." Sai kura ta che "A,a, bako zaya nika ne?" Sai akwiya ta che "En yi de, mache ba ta bakunchi." Sai ta karbe nika, tana nika, tana nika, kura tana kallon ta. Sai dan akwiya ya ji tsoro. Ya che ko kura zata kama shi, sai ya zo ya tsaya kussa ga uwan, akwiya. Sai ta che "To, en na yi waka, kai zaka rikka karbawa." Sai dan ya che "To." Sai akwiya ta yi wakanta, ta che "Na kasshi giwa goma." Sai dan ya che "Gaskiya ne kuwa." Sai akwiya ta che "Na kasshi zaki goma." Sai dan ya che "Gaskiya ne kuwa." Sai akwiya ta che "Na kasshi damisa goma." Sai dan ya che "Gaskiya ne kuwa." Sai akwiya ta che "Na kasshi kura goma—" Sai dan ya che "Habba, Iya, kadda ki fadi hakka, en kura ta ji sai ta gudu ta bar mu ba abinchi."

Sai kura ta ji, ta che "Mi kika che Akwiya?" Sai akwiya ta che "Na kasshi giwa goma." Sai dan ya che "Gaskiya ne kuwa." Sai akwiya ta che "Na kasshi zaki goma." Sai dan ya che "Gaskiya ne kuwa." Sai akwiya ta che "Na

kasshi damisa goma." Sai dan ya che "Gaskiya ne kuwa." Sai akwiya ta che "Na kasshi kura goma—"

Sai kura ta che "To, bar en aike yayana su taffi su debo mamu ruwa." Sai ta shiga dakinta, ta che "Yayana, ku taffi, ku gudu, kadda ku komo, abin nan ya fi karifimmu." Sai suka gudu, suka wa'atse a dauji.

Da suka gudu, sai kura ta zo, ta zona, da ta zona, akwiya tana wakanta, sai kura ta che "To, Bakuwa, na aike yara su debo ruwa, ga shi ba sun komo ba, bar en taffi en nemo su." Sai kura ta taffi da gudu, ba ta komo ba. Sai akwiya, ta dauke dukiyan kura, ta taffi da su, da ita da danta.

---

## 24

### The Spider, the Guinea-Fowl, and the Francolin.

Makaruwa ta zo, ta che da zabuwa "Ki yi mani rakiya." Sa'anan gizzo ya zo, ya che "Raka ni en je en gaida sarakuwana." Zabuwa ta che "Taffiyanka ta fi, mu taffi tare, da ni da kai." Sa'anan suka taffi zasu garin iyayen matan gizzo.

Suka zo turaba, gizzo ya che da zabuwa "Ga chiyawa, izan mu taffi gari amba ni gadda, ki zo ki kwasshe chiyawa ki gassa." Ta che "To." Suka taffi, suna taffiya, ya che "Ga kwoshiya, izan mu taffi, amba ni tuwo, ki zo ki dauka."

Suka taffi gida, akayi tuwo akakawo masu. Sa'anan ya che ma zabuwa "Dauko chokali, ki zo da shi." Ta taffi daukan kwoshiya, gizzo ya chainye tuwo, ya ragi shi kankanni. Da ta komo, ya che "Ke, kin taffi kin daddi, mutane suka zo suka dauke tuwousu."

Sa'anan ya che "Ga shi ankawo gadda, sai ki kwasshe chiyawa, ki zo mu gassa." Ta taffi garin chiyawa, ta zo da shi, ta iske gizzo ya chainye gadda. Ya che "Kin zona har mutane sun kwashe gaddansu."

Gari ya waye kuma, suka che "To, zamu gida." Akadaura ma gizzo kayanshi, akadaura ma zabuwa nata. Suka tashi, suka kama hainya. Suka zo bakin kogi. Gizzo ya fura wuta, ya che "Zona nan." Ya che "Ni zani chan, izan kin ji na fada ruwa, ke kuma, ki fadi a wuta." Sa'anan ya taffi, ya dauke dutsi, ya jefa a ruwa, ya yi *pinjim* a ruwa. Zabuwa ta ji, ta che "Gizzo ya mutu," ta fadi a wuta, ta mutu, ita kuma. Sa'anan gizzo ya zo, ya chiri zabuwa dagga chikkin wuta, ya garta sarai, ya chi. Sa'anan ya dauka kayan zabuwa, ya gamma da nashi, ya kama hainya, ya taffi gida.

Sa'anan ya zo ya che "Makaruwa, ba ki raka ni, ke kuma ba?" Ta che "I." Suka kama hainya zasu. Suka taffi, suka zo chiyawa. Gizzo ya che "Ga chiyawa, izan mu taffi gari, amba mu gadda, ki zo ki kwashe chiawa mu gassa." Makaruwa ta kwashe chiawa asiri ta boye.

Sai gizzo ya che "Ga kwoshiya, izan mu taffi gari, amba mu tuwo, ki zo ki dauko ta." Ta che "To," ta daka ta boye. Sai suka taffi gari, akakawo tuwo, gizzo ya che "Taffi ki kawo chokalin nan." Makaruwa ta che "A, ka che adauko, ga shi." Gizzo ya yi fushi, ya che "To, dauke tuwo ki chi." Makaruwa ta daka, ta chi, ta ragi kankanni, ta ba gizzo ya chi.

Sa'anan akakawo masu gadda, ya che "Ki taffi, ki kawo chiyawa mu gassa." Ta che "A, ga ta, na kawo tun dazu." Gizzo ya yi fushi da gaski, ya che "Dauke gaddan, ki chi." Makaruwa ta daka, ta gassa ta chi. Da ta chi ta ragi kankanni gizzo ya kwache ya chi.

Da gari ya waye sun che "To, zamu gida." Akadaura ma gizzo kayanshi, akadaura ma makaruwa. Suka daka zasu. Suka zo bakin kogi, gizzo ya fura wuta, ya che "Zona nan," ya che "ni, zani chan, izan kin ji na fada ruwa, ke kuma ki fadi a wuta." Ta che "To." Sa'anan ya taffi ya dauke dutsi, ya jefa a ruwa, ya yi *pinjim.* Makaruwa ta ji, ta daka takalamin gizzo, ta sa achikkin wuta, ita ta shiga achikkin kayan gizzo, ta boye. Sa'anan gizzo ya zo, yana duba achikkin wuta, ya daka takalami ya chi. Ya che "Ashe, zabuwa ta fi makaruwa mai." Sa'anan ya dauka kayan makaruwa ya gamma da nashi, zashi gida.

Sa'anan makaruwa, tana chikki, tana che "Gizzo wawa, ya chi takalami." Gizzo ya ji tsoro ya gudu, ya taffi gida, ya che anakiddi a garinsu. Sa'anan ya zo da kaya a gida, ya kwanche, yana zubar achikkin kwariya. Sa'anan makaruwa ta fitta, ta sauka a kain matan gizzo. Gizzo ya che da matansa "Ki tsaya kauwi, kadda ki yi motsi." Ya dauke tabariya zashi buga makaruwa a kain koki. Makaruwa ta tashi, ya buga, ya kuskure, ya kasshe matanshi. Makaruwa ta sauka a kain danshi, gizzo ya buga, ya kasshe dansa. Makaruwa ta sauka a kain autan gizzo, gizzo ya dauke tabariya, ya kasshe autan dansa, shi kuma. Sa'anan makaruwa ta sauka a kain gizzo. Gizzo ya fitta woje, ya kama itache yana hau, yana hau, har ya taffi chan bissa itache. Sa'anan ya juya kainsa, zaya kassa makaruwa. Makaruwa ta tashi da fukafukanta, gizzo ya fadi, ya mutu. Makaruwa ta taffi, ta kwache kayan gizzo duk, ta taffi.

## 25

### How the Cunning Jerboa killed the Strong Lion.

Naman dauji ke nan, zaki yana kasshe su, yana chi. Sai ran nan suka che, " To, ga zaki yana kare duniya, ayi dabara abinda zamu yi mu samu rai." Sai suka taru, suka je wurin zaki, suka che " Gadanga, Wan-Dowa, amma muna roken ka ne." Suka che " Kullum kullum muwa kai maka daya achikkin mu da safi, ka chi, amma sai ka bar mu saura da rai." Sai zaki ya che " To," sai suka taffi abinsu. Sai da safi suka yi kuriya, sai kuriya ta fadi kan barewa. Sai suka kama barewa, suka kai ma zaki. Sai zaki ya kasshe, ya chi, ya koshi, ba ya nemi wanni ba. Da safi kuma suka yi kuriya, suka kama gwanki, suka kai ma zaki, sai zaki ya kasshe ya chi.

Kullum hakka, sai ran nan kuriya ta fadi kan kurege. Suka kama zasu taffi da shi, sai ya che " A, a, sai ku bar ni, ni ko zan taffi wurin zaki dakaina." Sai suka che " To," suka sake shi. Ashe, kurege, mai-wayo, zaya kasshe zaki ke nan.

Sai kurege ya taffi raminsa, ya yi barchi, har rana ya yi tsaka, ba ya fitta ba. Sai zaki dagga chan yana jin yunwa, ba akai masa komi ba, sai ya tashi, ya yi fushi, yana neman naman dauji, yana kuka. Sai kurege ya fitta dagga raminsa, ya hau a wanni itache kussa ga rijiyanshi, yana hange zaki ya wuche. Sai ya che " Mi ya sa kana kuka?" Sai zaki ya che " Tunda safi ina jiran ku, ba akawo mani komi ba." Sai kurege yana bissa itache, ya che " To, ga shi, muka yi kuriya, kuriya kuma ta fadi a kaina. Ina zuwa ke nan da wanni zuma da zaka chi ka ji dadinshi, sai wanni zaki a rijiyan nan ya tare ni, ya kwache mani zuma." Sai zaki ya che " Enna zakin?" Sai kurege ya che " Yana rijiya, amma ya fi ka karifi." Sai zaki ya yi fushi, sai ya gudu wurin rijiya, ya tsaya a bakin rijiya, ya duba, sai ya ga wanni zaki achikkin rijiya yana kallon sa. Ashe, kamansa ne, ba zaki ne. Sai zaki ya zage shi—shiru. Ya zage shi—shiru. Sai ya yi fushi, ya damfaro kan shi achikkin ruwa, sai ya nutse, ya mutu.

Sai kurege ya komo wurin naman dauji, ya che " To, ni ma, na kasshe zaki, ku yi kiwonku a dauji, amma ni, ina zone a rami." Sai naman dauji suka che " To." Suka che " Zamma dabara wanda ta fi karifi, kurege ya kasshe zaki."

## 26

### The Camel and the Rude Monkey.

Dila ya hau, yana chin yayan kainya. Rakumi ya zo ya che "Dila!" Ya che "Na'am. Ya che "Kana chin mine?" Ya che "Ina chin yayan kainya." Ya che "Debo mani." Ya debe mashi. Sa'anan kuma dila ya shirko daga itache ya taffi abinsa.

Akakwana, da safi biri ya zo, ya hau, shina chin kainya. Rakumi ya che "Ba ka sa mani ba en chi?" Ya ba shi, ya sake ba shi. Ya che "Karo mani." Biri ya gaji, ya che ba shi ba shi ba. Ya che da biri "Durin uwarka mai-kurmin ido." Biri ya ji fushi, yana kumiyan idanunsa da rami, ya che rakumi da kankannin gusu. Sai rakumi ya kama shi ya daure shi, ya tashi, ya taffi da shi.

Yana taffiya, suka gammu da gizzo, ya che "Rakumi mi ya yi ka kama biri?" Ya che "Ka tambaya shi manna." Ya che "Ina chan kainya, ya che en diba mashi, ya che en kara mashi, ya kuma che en kara mashi. Na gaji, na che da shi 'mai-tozom baya' ya che 'mai-kurmin ido.' Ni kuma na che masa 'mai-kan kannin gatto.'" Gizzo ya che "Daure shi."

Suka zo wurin zaki. Zaki ya che "Mi ya gamma ka da biri?" Ya che "Tambaya shi." Ya che "Ina chan kainya, ya che en diba mashi, na diba mashi, ya che en kara mashi, na che ba shi da kumiya ba. Sa'anan ya che 'mai-kurmin ido,' ni kuwa na che 'mai-tozom baya, da gatto kaman ansha kimba.'" Ya che "Daure shi."

Sa'anan suka zo suka samu dila yana zone awoje, a gusun itache. Ya che "Ku zo en yi maku shari'a." Dila abokin biri ne, rakumi ba ya sani ba, wayo kuma gare shi. Suko zo, suka zona. Ya che "Ka kwanche mashi igiya."

Biri ya zona wojen dama, rakumi yana zona ahagu. Ya che "To, kai biri ka hau itache, ni kuma na shiga rami." Biri ya tselle, ya kama itache ya hau, dila ya shiga raminsa aguje, sun bar rakumi azone.

Shi ke nan shari'a ta kare, rakumi ya taffi abinsa.

---

## 27

## The Boy who was Lucky in Trading.

Wanni yaro da ubanshi. Yaron ya che zashi fatauchi. Sai uban ya che "Ga dan kunama, ka yi guzuri da shi." Sai ya dauke dan kunama, ya kama hainya, sai ya iske da masu-noma. Sai masu-noma suka che "Kawo dan kunama," sai suka kasshe. Sai ya che "Ku, Masu-Noma, ba ni kunamana." Sai suka che "Wanni kunama?" Sai ya che "kunama da ubana ya ba ni guzuri." Sai suka dauke magiribi suka ba shi.

To, ina chikkin taffiya, sai ya zo ya iske masu-saran dawa. Sai suka che "Kawo magiribinka mu yi sara da shi." Sai suka karbe magiribi. Da suka karbe, suka sare, sai ya che "Ku Masu-sara, ba ni magiribina." Sai suka che "Wanni magiribi?" Sai ya che "Magiribinda masu-noma suka ba ni." Sai suka che "Waddane masu-noma?" Sai ya che "Masu-noma da suka kasshe kunamana." Sai suka che "Wanni kunama?" Sai ya che "Kunama da ubana ya ba ni guzuri." Sai suka kawo garin gero suka ba shi.

Sai yana taffiya, sai ya gammu da Ba-Hilata da tana sayar da nono. Sai ta che "Kai, Yaro, kawo garin geronka, agamma da nono." Ya ba ta, sai ta gamma da nono, ta shainye. Sai ya che "Yowa, Ba-Hilata, ba ni garin gerona." Sai ta che "Wanni garin gero?" Sai ya che "Garin geronda masu-sara suka ba ni." Sai ta che "Waddane masu-sara?" Sai ya che "Masu-sara da suka karbe magiribina." Sai ta che "Wanni magiribi?" Sai ya che "Magiribinda masu-noma suka ba ni." Sai ta che "Waddane masu-noma?" Sai ya che "Masu-noma da suka kasshe kunamana." Sai ta che "Wanni kunama?" Sai ya che "Kunama da ubana ya ba ni guzuri." Sai ta ba shi mai.

Sai yana taffiya, yana taffiya, sai ya gammu da mai-taba. Sai mai-taba ya che "Ai, kana da mai, akawo, agamma da taba, en dakka." Sai ya ba shi mai. Sai ya toye, ya dakka taba da shi. Sai yaro ya che "Wayo, wayo, Mai-Taba, ba ni maina." Sai ya che "Wanni mai?" Sai ya che "Mainda Ba-Hilata ta ba ni." Sai ya che "Wache Ba-Hilata?" Sai ya che "Ba-Hilata wadda ta shainye garin gero." Sai ya che "Wanni garin gero?" Sai ya che "Garin geronda masu-sara suka ba ni." Sai ya che "Waddane masu-sara?" Sai ya che "Masu-sara da suka karbe magiribina." Sai ya che "Wanni magiribi?" Sai ya che "Magiribinda masu-noma suka ba ni." Sai ya che "Waddane masu-noma?" Sai ya che "Masu-noma

da suka kasshe kunamana." Sai ya che "Wanni kunama?" Sai ya che "Kunama da ubana ya ba ni guzuri." Sai ya ba shi kanwa.

Yana taffiya da kanwa, sai ya gammu da Ba-Filache, yana kiwon shanu. Sai Ba-Filache ya che "Kai, Yaro, kawo kanwan nan en sa ruwa, en ba shanu su sha." Sai ya ba shi kanwa, ya ba shanu, suka sha. Da suka sha sai ya che "Wayo, wayo, Ba-Filache, ba ni kanwa." Sai ya che "Wanni kanwa?" Sai ya che "Kanwa da mai-taba ya ba ni." Sai ya che "Wanni mai-taba?" Sai ya che "Mai-taba wanda ya sha maina da Ba-Hilata ta ba ni." Sai ya che "Wache Ba-Hilata?" Sai ya che "Ba-Hilata wadda ta shainye garin gero." Sai ya che "Wanni garin gero?" Sai ya che "Garin geronda masu-sara suka ba ni." Sai ya che "Waddane masu-sara?" Sai ya che "Masu-sara da suka karbe magiribina." Sai ya che "Wanni magiribi?" Sai ya che "Magiribinda masu-noma suka ba ni." Sai ya che "Waddane masu-noma?" Sai ya che "Masu-noma da suka kasshe kunamana." Sai ya che "Wanni kunama?" Sai ya che "Kunama da ubana ya ba ni guzuri." Ba-Filache sai ya kawo sa ya ba shi.

Sai yana taffiya da sa, yana taffiya da sa, sai ya zo wanni gari ya sauka gidan sarikin pawa. Sai sarikin pawa ya che "Kai Yaro, kawo san nan naka, ayanka." Da akayanka, da akasayarda nama, sai yaro ya che "Wayo, Sarikin Pawa, ba ni sana." Sai ya che "Wanni sa?" Sai ya che "Sa da Ba-Filache ya ba ni." Sai ya che "Wanni Ba-Filache?" Sai ya che "Ba-Filache wanda ya karbe kanwana." Sai ya che "Wanni kanwa?" Sai ya che "Kanwa da mai-taba ya ba ni." Sai ya che "Wanni mai-taba?" Sai ya che "Mai-taba wanda ya sha maina da Ba-Hilata ta ba ni." Sai ya che "Wache Ba-Hilata?" Sai ya che "Ba-Hilata wadda ta shainye garin gero." Sai ya che "Wanni garin gero?" Sai ya che "Garin geronda masu-sara suka ba ni." Sai ya che "Waddane masu-sara?" Sai ya che "Masu-sara da suka karbe magiribina." Sai ya che "Wanni magiribi?" Sai ya che "Magiribinda masu-noma ya ba ni." Sai ya che "Waddane masu-noma?" Sai ya che "Masu-noma da suka kasshe kunamana." Sai ya che "Wanni kunama?" Sai ya che "Kunama da ubana ya ba ni guzuri." Sai sarikin pawa ya kawo bawa biyu ya ba shi, da mache da namiji.

Da ya ba shi, sai yaro ya komo gidan ubanshi, ya che ma uban "Fatauchi ya yi keyau, na komo." Kunama ya yi masa sanadi ya samu bayi biyu.

Iyakanshi ke nan.

## 28

### One cannot help an Unlucky Man.

Wanni ke nan matsiyachi, ba shi da komi, sai dusa su ke chi da matanshi. Wannan kuwa shina da matanshi, da bayi da yaranshi. Sai suka yi gwona kussa da juna.

Sai wanni, wanda ya fi su duka arziki, ya zo zaya wuche, a hainya. Ya sa tsuman riga, da tsuman wando, da tsuman fula, su ba su san shi mai-arziki ba, suka che mai-bara ne. Sai da ya zo sai ya che da mai-arzikin nan "Sanu da aiki." Da ya che "Sanu," sai mai-arzikin nan ya che "Kai, ko dagara mu ba mu sani ba." Sai ya wuche, ya je, ya zo gwonan matsiyachin nan. Sai ya che "Sanu da aiki." Sai ya che "Um, um," sai ya che ma matanshi, "Massa, ka yi farafaron dusa, ki je ki ba shi ya sha." Sai ta kai mashi, ta durukussa, ta che "Ga shi, abinda mu ke sha ke nan." Sai ya che "To, madallah," ya kaffo bakinshi kaman zaya sha, ba ya sha ba, ya ba ta, ya che "Na gode."

Sai ya koma gida, sai ya che "To, mutumen nan da ya yi mani alheri, sai na rama mashi." Sai ya taffi. Akawanke kwariya pal da farin kassa, akachikka kwariya duk da liyari har baki, akakawo sabon fefe, akarufe. Sai mutumen nan ya sa yarshi agabba ta dauke kwariyan nan. Da suka zo bakin daji, sai ya che "Kin ga mutane chan suna aiki dayawa?" Ta che "I, na gan su." Ya che "To, kin gan mutum daya yana aike da matanshi?" Ta che "I." Ya che "To, shi zaki kai mashi kwariyan nan." Sai ta che "To." Sai ta zo ta wuche, ta je wurin matsiyachin nan, sai ta che "Sanu," sai ta che "Anaike ni wurinka," ta che "Ga kwariya, anche akawo maka."

Shi matsiyachi ba ya bude ya gani abinda ya ke chikki ba, tsiyata ta hanna shi ya bude. Sai ya che "Akai ta wurin Mallam Abba, ya dibi garin nan ya ba mu saura." Da akakai ma Mallam Abba da ya ga liyari achikki, sai ya sake achikkin alkilanshi. Sai ya kawo garin gero ya damfara achikkin kwariya, ya che "Ki kai masa, na diba." Sai matsiyachi ya che "To, madallah, sai ki zuba saura a kwariyam mu, ki taffi, na gode."

Shi kuma, mai-arziki, yana kallo dagga nesa, haushi ya kama shi, sai ya che "Ai matsiyachi en ka saka shi a tandun mai sai ya fitto farifat. Ni ina so shi da arziki, hakka Allah ya yi shi."

29

## The Wonderful Ring.

Wota de, nan de ta haife yayanta biyu mazza, ita mache. Sai suka tashi zasu fatauchi, yayan. Baban ya taffi da zanne uku, karami da zanne uku. Baban ya sayo akwiya, karami ya sayo busashen kare. Sai suka dawo, uwan ta che "Sanunku da, zuwa." Sai baban ya che "Ga abinda na samu, akwiya." Sai karami ya che "Ga abinda na samu, kare." Sai ta che "Kai de, Allah wadan ka, mi ya sa ka sayo busashen kare?" Sai baban ya che "Op, zaya yi arziki ne, ni ina nan?"

Sai zasu koma fatauchi, baban ya same zanne fudu, karami ya same zanne uku, sai suka taffi. Sai baban ya sayo sa, sai karami ya sayo mage busheshiya. Da suka dawo, sai uwan ta che "Sanunku." Sai baban ya che "Ga abinda na samu, sa." Sai karami ya che "Ga abinda na samu, mage. Sai uwan ta che "Kai de, Allah wadan ka, mi ya sa ka sayo mage busheshiya?" Sai baban ya che "Op, zaya yi arziki ne, ni ina nan?"

Zasu koma fatauchi kuma, sai baban ya same zanne goma, karami ya same zanne uku. Da suka taffi sai baban ya samu bayi biyu, yam-mata masu-mama kaman churan hanu. Sai karami ya samu kuyanga tsofuwar mache karamasashiya, mamanta ya zamma takalami. Sai suka dawo, sai uwan ta che "Sanunku." Sai baban ya che "Ni ga abinda na samu yam-mata bayi biyu." Sai karami ya che "Ga abinda na samu tsofuwar mache." Sai uwan ta che "Kai de, Allah wadan ka, mi ya sa ka sayo tsofuwar mache karamasashiya." Sai baban ya che "Op, zaya yi arziki ne, ni ina nan?" Sai karami ya che "A, Allah nana."

Ashe, tsofuwa karamasashiya yar sarikin gari da su ke yi fatauchi. Shi kuwa sariki ba shi da wanni da, ba shi da wanni ya sai ita tsofuwa. Yaki ne ya kama ta, ta bata, shi ko karami ya saye. Sai mutumen garinsu ya zo garin yara. Ita, kuwa, amba ta fura, tana sayaruwa. Sai tana talli, tana talli, tana che "Ga fura, ga fura." Sai mutumen garinsu ya che "Kawo," Da ta kawo, ya gan ta, sai ya rikka chikki, ya che "A, Gimbiya, ananeman ki gari da gari, ba agan ki ba." Sai ta che "Ina nan, wanni yaro ya saye ni, ina bauta." Sai ya che "To," sai ya che "Mu taffi, ki nuna mani uban-gidanki en gane shi." Sai suka taffi. Sai ta kirra yaro woje daya kadda uwan ta ji, ta che da mutumen garinsu "Ga uban-gijina." Sai shi mutumen gari ya che "Da ka yarda ka bi ta, ka taffi garinta, ka taffi wurin ubanta, sarikin gari, ya panshe ta." Sai yaro ya che

"To." Da ya zo sai ya gaya ma uwanshi, yaro. Sai uwan ta che "To, taffi, Mara-Arziki, taffi su kwache maka tsofuwar karamasashiya." Sai ya che "To, ni ne zan taffi."

Sai ya sa kuyanganshi agabba, sai suka je garinsu, sai kofan gidan ubanta. Sai gari ya taru duk, akache "Gimbiya ta zo." Sai sariki yana murna, ya kai shi wanni gida, ya che zaya yanke mashi sa. Sai ya che rago ya issa.

Ita kuwa, kuyanga, ta che "To, idan ubana ya ba ka zambar dubu, ka che ba ka so. En ya ba ka saniya dubu, ka che ba ka so. En ya ba ka doki dubu, ka che ba ka so. En ya ba ka bawa dari, ka che ba ka so." Sai ta che "Abinda zaya ba ka ya panshe ni sai dan zobe na dankwurin yasa." Ya che "To." Ta che "Shi kadai zaya ba ka ya panshe ni ke nan, izan ka karbe zoben nan, mafarin gari ke nan, ka chi gari duka." Sai ya che "To." Sai sariki ya che "To, ga pansa zambar dubu." Ya che "Ba na so." Ya che "Ga saniya dubu." Ya che "Ba na so." Ya che "Ga doki dubu." Ya che "Ba na so." Ya che "Ga bawa dari." Ya che "Ba na so." Sai ya che "Abinda zaka ba ni ya panshe ta sai dan zobe na dankwurin yasanka." Sai sariki ya che "Yanzu izan na ba ka zoben nan duk gari zasu taru su bi ka a hainya, su kasshe ka." Ya che "To, zan ba ka zobe, amma zan ba ka wanni dokin zagi, ina tsere dokin garin nan duka da gudu." Ya che "To, ga zoben, ka saka chikkin bakinka." Ya che "To, da fittanka kofar, ka yi ta sukuwa."

To, dagga garin nan zuwa garin yaro, taffiya kwana talatin, to, shi kuwa, zaya sukuwa rana daya, ya tsere. De de da ya fitta kofan gari, sai gari duk suka je, suka yi kuwa, suka daure surdi. Da zuwansu, sai suka bi yaro da sukuwa. Suna ta sukuwa, suna ta sukuwa, suna ta sukuwa, har zasu kama shi, shi ya shiga garinsa, sukuwa su ke woje. Sai suka che "To, izan kuna bin mutum ya tsere har ya shiga garinshi, sai ku bar shi."

Da zuwan yaro gidanshi, da ya raba kaffa, sai doki ya padi, ya mutu. Sai uwan ta che "Ai, na gaya maka ba ka da arziki, ga shi, ankwache maka karamasashiyan baiwa naka, amba ka doki, ga shi ya mutu." Sai baban ya che "Op, shi zashi yi arziki ne ni ina nan?" Sai ya che "Arziki na Allah ne." Sai ya fitta dagga gari, ya yi wanni buka a bakin daji.

To, zobe kuwa na hanunshi. Da ya kwanta, sai ya ji "dit, dit, dit," kassa na motsi, gari ina zuwa. Gari ya waye kuma, ga baban gari, ga katanga da gidan soro, ga mata ba iyaka. Sai ya je ya kirra uwanshi, ya yi mata daki dabam, bushashen kare da kekashashen mage ya yi nasu gidansu dabam, da wansa ya yi masa gida.

Sai wota karuwa ta ji labari, ta che ba ta son wanni sai shi. Ya che shi kuma yana son ta. Suna zona da karuwa, komi ta ke so ya ba ta, komi ta ke so sai ya ba ta.

Sai ran nan gari ya waye, ta yi ta kuka, ta yi kuka, ta yi kuka, har rana ya fadi tana kuka. Ta che "Ashe, ba ka so na?" Ya che "Domi kina che ba na son ki?" Sai ta che "Tsakanina da kai, da ka so na, sai ka ba ni zoben nan ya kwana a hanuna." Da ya ba ta zobe sai ta dauka ta kai ma farakanta. Da dare ya yi sai gari ya tashi ya koma wurin farakanta. Akabar shi da bushashen kare, da karamasashiyan mage, da uwanshi, da wanshi.

Sai ya tashi da safi ina kuka. Sai kare ya che "Mi ka ke yi mashi kuka?" Ya che "Ka ji yanda karuwa ta yi mani." Sai mage ta che "Mi ka ke yi mashi kuka?" Sai ya che "Kin ji yanda karuwa ta yi mani." Sai suka che "Op, wannan mai-sauke ne, ba kai ka aje mu zamu yi maka rana?"

Sai kare da mage suka tashi, zasu taffi garinda karuwa ta kai zobe, zasu sato. Sai suka taffi, sai kogi ya tsare su. Sai kare ya che "Op, ni na iya ruwa, Ke, Mage, zo en gwoye ki." Sai ya gwoya mage, suka haye, rana kuwa ya fadi. Sai mage ta che "To, Karre, shiga gari ka yi sata, ka chikka koshi, ka zo ka iske ni." Sai kare ya shiga gari, ya yi ta sata, ya yi ta sata, sai ya chikka koshi ya komo, ya iske mage a bakin rafi. Sai ta che "To, zona nan, ni kuma zan shiga gari." Da ta shiga gari, gidanda ta fara shiga ta kasshe kusu dubu. Ta fitta, ta shigi wanni kuma, ta kasshe kusu dubu. Ta fitta, ta shigi wanni kuma, ta kasshe kusu dubu. Sai sariki ya ji labari, wanda zobe yana wurinshi, sai ya che "Akawo mani magen nan, ta zo ta kasshe mani kusu a gida." Sai akakawo ta, ta kasshe dubu. Sai sarakunan bera suka zo, suka che "Wanni laifi muka yi bana kina kissa mu hakka?" Sai ta che "Zoben uban-gijina yana nan wurin sarikin garin, em ba ku sato ku kawo mani ba zan kasshe ku duka." Sai suka che "To, muna duba." Sai suka yi ta dubawa, suna yi ta dubawa, ba suka samu ba. Sai ta che "Tun ba kun samu ba kun shiga uku." Sai ta kasshe dari biyal anan wurin.

Sai wanni sarikin bera ya che "To, mu irinmu, ba muwa samu, sai kirinkori." Sai akaje gidan sarikin kirinkori, aka-kirra shi. Sai sarikin bera ya che "Kai, Sarikin Kirinkori, ka ji abinda ya same mu, amma sai ka yi dalili da iyalenka su sato mamu zoben nan don mu futa da kissa hakka." Sai sarikin kirinkori ya che "Op, ai wannan mai-sauke ne."

Ashe zoben nan sariki ya kan kwana da shi a baki da dare.

Sai kirinkori suka nema a daki, suka nema a daki, ba suka samu ba, sai suka hau gado. Sariki yana barchi, ya bude baki, ashe zobe ya fitta dagga baki, ya fadi kussa da shi. Sai kirinkori daya ya dauke zobe, sai daya kuwa ya chije shi a halshi don ya falaka. Da ya falaka, sai yana lalabe, sai karuwa ta che "Minene?" Sai ya che "Bera ne ta chije ne a baki." Sai karuwa ta che "En je, ba sun dauke zobe ba?" Sai ya lalaba ya che "A, a, da safi agani."

Sai sarikin kirinkori ya dauke, ya kai ma mage, sai mage ta saka chikkin bakinta, sai ta je ta iske kare, sai kare ya gwoye ta, suka haye. Sai suka zo, mage ta che "Kai, Uban-gijina, barri kuka, abin nan mai-sauke ne, ga zobe."

Da ya tashi da safi, sai ya gani gari ya dawo. Da gari ya waye, karuwa ta gani ba gari kuma, dagga ita sai farakanta. Sai ta che "Allah wadan ka, matsiyachi, ko ansaka shi chikkin tandun mai sai ya fitto farifat, mai-arziki kuma, ko a Kuwara sai ya sayerda ruwa."

---

## 30

### The Greedy Girl and Her Cure.

Wannan de, yariniya ke nan, tana kwadaye, komi ta ga sai ta dauka, ta chi. Sai ta ga kasshi ko ya yi shekara dari sai ta daka, ta chi. Sai iyayenta sun che "Tashi, ki taffi, ba muna son ki kuma, kin chikka kwadaye." Sai ta taffi wurin kawa tata, ta che "Ga shi, iyayena sun che en taffi yawon duniya, ba suna so na kuma, na chikka kwadaye." Sai suka taffi, da ita da kawa tata. Sai suka taffi, suka samu karnuka guda tara a hainya, sai ta chainye. Da ta chainye karnuka, kawa tata kuwa tana kan hainya, ta che da ita zata bayan gida. Da ta komo kawa tata ta che "Kin yi bayan gida?" Sai ta yi kukan kare "Um, Um," ita yariniya, ba ta iya magana ba, sai na karnuka.

Sai suka taffi wanni gari chan, suka sauko gidan sariki, sai sariki ya che shi yana son ta da aure, ita kuma ba ta magana, sai yaruwa. Akadaura mata aure da sariki, kekeyawa che ita kuma, ita kawa galadima ya aure ta. Suna kwana da sariki, ba ta magana sai haushin kare, sariki ya yi, ya yi ta yi magana, ta ki, ba ta iya magana ba. Shi ke nan sai akache atara matan gari duka su yi gayan dakka a gidan sariki sabada ajuya bakin yariniya.

Shi ke nan sai kawar yariniya da tsakkar dare ta zo ta tashi

yariniya suka koma gunda ta chi kare. Dagga nan suka taffi gun maiya. Sai yaruwa ta che da maiyar "Iya, ba ki yi mani maganin yariniya da ta chi kare ba?" Sai maiya ta buge bayan yariniya, sai kare su tara sun fitto. Sai su yam-mata suka koma gida kuma, a gidan sariki.

Sai gari ya waye, sai matan gari duk sun taru a gidan sariki zasu yi dakka. Shi ke nan sai ana ta dakka, ana ta dakka, sai shi ke nan sai tabariya tana che "Kare fitto massa, kare fitto massa."

Sai da suka kare sai yariniya ta fitto da tabariya na karifi a hanu. Shi ke nan sai rana shina chewa "Kurururu tana dakeyau." Sai kassa tana che "Em passa nan em ba ki gu ki wuche?" Sai ta che "En kin passhe enna zan taka?" Sai ta taffi gun dakka, sai ta yi dakka, ta yi dakka. Sai ta che da sariki "Chiro ma takobi," ta che "izan zamma da mugun baba, yaro sake dubara." Sariki ya ji magana, ya zona da ita kadai, suna chin duniya, sauran matansa duk ya kasshe su.

---

31

THE GLUTTONS.

Da Bankammi da Barrankamma sun yi gidansu, suna zone. En ya taffi daji ya kan kasshe giwa ya chi, izan ya dauko giwa ya zo ya kirra matanshi, ya che "Ungo Barrankamma," ya mika mata, kafin ya kewoya, ya zo gida, ya gamma da ita da kasshi zata zubas, ta chainye. Izan gari ya waye, ta kan nika masa rafogon dawa guda, ta ba shi, ya sha, zashi daji.

To, sarikin gari ya ji labari, ackache "Masu-chi ne da gaske, da shi da matanshi." Sariki ya che "Akirrasu, su zo." Sariki ya che "To, gari duk ayi dakka." Akayi dakka, gare duk, akache "Ayi tuwo, ayi gari, akawo gidan sariki."

Sa'anan sariki ya che "Ga mu da baki a gari." Sa'anan akakwashe tuwo da gari, akakai wa Bankammi da Barrankamma. Suka chainye duk, suka che wa sariki suna jin yunwa. Sariki ya che "Akawo masu ruwa a tulu." Akakawo masu suka sha, suka che ba sun koshi ba. Sai ya che "To, sai ku hakura hakkanan." Sariki ya che "To, ku kwana, da safi en sallame ku, ba mu iya da ku ba."

Safi ya yi, sariki ya kawo bawa fudu ya ba su, ya che su yi masu noma.

## 32

### How Dodo frightened the Greedy Man.

Wanni ke nan da danshi, mar-uwache. Sai uban yana da sa, sai ya che " Ni ba ni yanka a wurin, kuda ya zo ya tabba nama ba." Sai suka taffi chan tsakkan daji, sai ya che dan ya yi tusa su gani ko ba kuda. Sai ya yi, ba su ga kuda ko daya ba. Sai suka yanka sa anan.

Ashe, sun manche, ba sun zo da wuta ba. Sai uban ya hau bissa itache, sai ya hange dodo ya bude tsuliyanshi ja wur kaman wuta. Sai ya che ma dan " Ga wuta chan, ka taffi ka debo." Dan ya tabba tsuliyan Dodo ket, ket, ket, kaman zaya debo wuta. Sai Dodo ya che " Wanene nan?" Sai yaro ya che "Baba ya che ka zo." Sai ya dauko jakkansa wanda ya ke zuba nama achikki, tsawun jakkan nan ya kai dutsi. Sai ya zo wurin uban, ya che " Wa ke kirra na?" Sai uban ya che " Ni ne." Sai uban ya dauke karapatan sa ya ba shi. Sai ya saka a jakka, ya che " Don kankanin abin nan mutum ya kan kirra abokinshi?" Sai ya dauka daya kuwa ya ba shi. Sai ya saka a jakka, ya che " Don kankanin abin nan mutum ya kan kirra abokinshi?" Sai ya raba sa ya ba shi. Sai ya saka a jakka, ya che " Don kankanin abin nan mutum ya kan kirra abokinshi?" Sai ya dauke saura ya ba shi. Sai ya saka a jakka, ya che " Don kankanin abin nan mutum ya kan kirra abokinshi?"

Saura pata da kaffa, da kai, ya tara ya ba shi. Sai ya saka a jakka, ya che " Don kankanin abin nan mutum ya kan kirra abokinshi?" Ba saura sai kashi, ya tara kashi da toroso ya ba shi. Sai ya saka a jakka, ya che " Don kankanin abin nan mutum ya kan kirra abokinshi?" Sai ya che " Ai ba saura." Sai ya che " Ai ku nama ne." Sai ya dauke dan ya ba shi. Sai ya saka a jakka, ya che " Don kankanin abin nan mutum ya kan kirra abokinshi? Sai ya che " Ai ba saura." Sai ya che " Kai fa?" Sai ya sa uban achikkin jakka.

Ya fitta da dan, ya che dan ya duba kayan, ya che zaya je ya samu itache zaya gassa sa. Da ya taffi, sai dan ya dauke wuka, ya barke jakka, uban ya fitto. Sai suka gudu, suka bar nama a nan. Sai Dodo ya dawo, ya iske suka gudu, sun bar nama, sai ya gassa, ya chainye.

Sai uban da dan suka koma gida, sun che sun tuba, ba su kara rowa. En sun gan mutum yana wuchewa a hainya, ko ba kussa ba, sai su kirro shi su ba shi abinchi. Suka che rowa ba keyau, ba suwa kara yi ba.

## 33

### Bortorimi and the Spider.

Wannan ne de sunanshi Bortorimi, katon mutum ne, ba kamanshi. Sai en ya je daji sai ya kasso giwa kaman ashirin ya kawo. Sai ran nan sai gizzo ya aike matanshi, koki, ta taffi, wai ta dauko wuta a gidan Bortorimi. Sai koki ta zo tana dauka wuta, sai suka ba ta nama maiyawa. Sai ta je ta taffi da shi gida. Sai gizzo ya che "Wa ya ba ki nama?" Ta che "A gidan Bortorimi na samu." Shi ke nan, sai gizzo ya che "To, akasshe wutan." Sai ta kasshe, sai ta koma chan gidan Bortorimi, sai ta che "Wuta ta mutu." Sai akadada ba ta nama.

Sai gizzo shi ma ya taffi gidan Bortorimi. Da Bortorimi ya ba gizzo nama, sai ya chainye, ba ya kawo gida ba. Da ya chainye, sai ya tambaya Bortorimi "Enna ka ke samun naman nan ne?" Sai ya che "Chan daji ne da nisa kuwa." Sai ya che "To, ko en je en raka ka?" Sai Bortorimi ya che "To." Sai shi ke nan, sai Bortorimi ya che sai azuba ya zo.

Sai gizzo ba ya barri azuba ya zo, sai ya dauke kan dakinshi ya sa wuta a daki, ya yi haske duka gun kaman gari ya waye, azuba kuwa ba ta yi ba, tsakkan dare ne kuwa. Shi ke nan, sai gizzo ya taffi ya tsaya awoje, ya kirra, ya che "Kai Bortorimi, Kai Bortorimi, tashi, tashi, azuba ya yi." Sai Bortorimi ya che "Habba, Gizzo, ai ina ganin ka, ka dauke kan dakinka ka sa wuta." Sai gizzo ya koma gidanshi.

Shi ke nan, sai gizzo ya hau kan dutsi, ya yi kirran salla, ya che azuba ya yi. Shi ke nan, sai gizzo ya taffi ya tashi Bortorimi ya che "Gari ya waye, anakirran salla, ka tashi." Shi ke nan, ya che "Habba, Gizzo ba ka hakura ba?" Ya ki taffiya.

Hanchin Bortorimi kuma da girima kaman zaure, kasuwa na chikki. Sai gari ya waye, sai suka taffi da gizzo. Da suka je, suka samu wanni katon kogi. Shi ke nan, sai Bortorimi ya che da gizzo "Sha shanka." Gizzo ya sha, ya koshi, sai Bortorimi da ya kaffo baki, sai ya tashi da ruwa duka, sai tabo. Suna taffiya, sai suka taffi chan da nisa enda giwa su ke kiwo. Shi ke nan, sai Bortorimi ya che da gizzo "Ka je, ka duba masu-kiwon chan, ka zage su." Ya che "En ka zage su, su koro ka, ka gudu ka shiga hanchina." Sai ya che "To." Sai ya taffi. Da ya taffi sai ya zage giwa, ya che "Masu-kiwon nan, uwar ku." Sai suka farfaro gizzo aguje. Sai da ya wo gudu, sai ya shiga hanchi, sai Bortorimi ya kama giwa duk, ya kasshe.

Sai gizzo iya zalenchi achikkin hanchin Bortorimi, ya che shi yaron sariki ne, aba shi gadda ya chi. Sai jatuma ta ba shi.

Dagga nan Bortorimi ya kasshe giwa, iya kirran gizzo "Gizzo fitto manna." Sai gizzo ya fitto. Sai Bortorimi ya che da gizzo "To, zabe naka giwa da zaka dauka." Sai gizzo ya che ai shi ba ya iya dauka ba. Sai Bortorimi ya gamma duk ya dauka. Sai suka zo gidda. Sai Bortorimi ya che "To, Gizzo, ga naka." Sai gizzo ya gara giwa, ya gassa, duk ya chainye, ya ki sa mata koki.

Shi ke nan, da gizzo ya chainye sai ya komo gidan Bortorimi. Da de ya komo ya che "Bortorimi ba zaka koma gun ba?" Bortorimi ya che "Um, um, ba zan koma ba, ya issa."

---

34

## The Hyæna and the Spider visit a Chief.

Da kura da gizzo. Gizzo ya che "Kura ki saye zuma mu taffi mu yi gaisuwa awurin sariki." Sai kura ta che "To." Sai suka saye zuma. Sai suna taffiya, suna taffiya, sai kura ta che ma gizzo "Zani bayan gida." Sai gizzo ya che "To, aje tukuniyan zumanki tukuna, ki taffi, ki yi bayan gida." Sai kura ta che "A, a, ai nawa ne." Sai ta je ta shainye zuma. Da ta shainye, ta yi kashi achikkin tukuniya.

Sai suka je suka sallama a gidan sariki. Akayi masu marhaba, akayi masu wurin sauka. Sai suka dauko tukane, gizzo ya dauko nasa tukuniya, kura kuwa ta dauko nata, suka che "Ga gaisuwa muna yi ma sariki." Sai akadauke tukuniya na kura akaaje achikkin gida, akadauke na gizzo, akaaje a zaure. Da akabude na kura sai akaga kashin kuma achikki, da akabude na gizzo akatarada zuma achikki. Sai akagaya wa sariki, akache "To, tukuniyan kura sai kashinta achikki." Sariki ya che "To, sun zo su samu alheri wurina, na san alheri da zan yi mata."

Dayamma akazo da tabarima, akache "Ga shimfidan kura." Akakawo kirigi, akache "Na gizzo." Kura ba ta yarda ba. Sai gizzo ya che "To, kura, anche ni en kwanta a kirigi, ke a tabarima, kin che ba ki yarda ba, zaki chainye masu kirigi ke nan." Sai ta che "A, a, alkawali ba ya yi hakkanan ba." Sai gizzo ya che "To, kiya gani, en kin chi kirigin nan kin ba ni kuniya." Shi ke nan sai ya ba ta kirigi, ita kuwa ta ba shi tabarima, sai ta je ta kwanta.

Da barchin fari sai ta tashi ta soma chi, sai gizzo ya che "Kai, kin fara chi?" Sai ta che "A, a, bera ne." Kafin gari ya waye ta chi kirigi kap, ya kare. Sai gizzo ya che "To, kura, enna tsimi, enna dabara?" Sai kura ta che "Op, ba muwa che barawo ya dauke kirigi?" Sai gizzo ya che "Ke, Kura, ko anfadi hakka sariki ba ya amsa ba, ya sani ke nan." Sai ta che "Ni na same kofar shiga, na fitta oho." Sai akagaya ma sariki, akache "Ansache kirigi." Sai ya che "A, a, na sani kura ta chainye."

Sai shi ke nan, sai sariki ya che "Ni ma, yau na sallame ku." Sai ya kamo sa ya che ma gizzo "Gaisuwanda ka zo ka yi mani, ni ma na ba ka sa." Sai akakawo meyatachen bunsuru, akaba kura. Sai gizzo ya che ya gode, sai kura ta che ta gode. Sai suna taffiya, suna taffiya, tana ja meyatachen bunsurunta, sai ta che "Barri en chi kaffa daya ka zamma gurugu, kai gurugu ne." Sai ta chiri chinya daya ta chainye. Sai tana che "Taffi da uku uku, taffi da uku uku." Sai ta chiri daya kuwa ta chainye, tana che "Taffi da biyu biyu, taffi da biyu biyu." Sai ta chiri daya kuma, tana che "Taffi da daya daya, taffi da daya daya." Sai ta chiri dayan kuma, tana che "Taffi da babu babu, taffi da babu babu." Sai ta dauke saura ta chainye, sai ta bar dan hanta kadan, ta ba gizzo, gizzo ya chainye.

Sai suna taffiya, suna taffiya, sai ta che "Ba ni hantana." Sai gizzo ya nuna mata rana ya yi ja wur, ya kussa fadi, ya che "Ga wuta nan, sai ki debo wutar mu zo mu chi san." Sai kura ta yi ta gudu, ta yi ta gudu, kullum rana da nisa. Da ta gudu, sai gizzo ya yanka, ya fede, ya hau bissa da shi, ko pata ko kasshi ba ya barri ba, ya rufe jini a kassa.

Da ta gaji, ta komo, tana che "Enna gizzo, enna gizzo?" ta tsugune. Ashe, itachenda ta tsuguna kassa da shi, gizzo yana bissa. Sai ya jefe ta da kasshi a ka. Sai ta che "A, ashe, Allah ya ba ni abinchi a gaton itache?" Da ta chainye kasshi, ta duba bissa ta ga gizzo, sai ta che "Ashe, kai ne? Na che ko Allah ne." Sai ta che "Gizzo du Allah ka ba ni chiniya daya manna." Sai ya che ba zaya ba ta ba. Sai ta che "To, ba kana takama kaya hau itache ba? Na samu wanda zaya fi ka tsawo ya zo ya kama ka a itache."

Sai ta je ta kirra jimina. Shi gizzo da jimina ta zo sai ya yi zazagaga da igiya, ya kama jimina. Da ya zazaga ta sai kwai ya fado. Sai kura ta dauke kwain ta chainye. Sai tana che "Gizzo zazage ta kwai ya fitto." Sai jimina ta che "Op, Kura, sai hakka zaki yi mani? Kai Gizzo ka sake ni." Sai gizzo ya sake jimina, sai kura ta che "To, mu zo mu je aguje." Sai kura ta zubar da gudu, jimina ta bi kura, ta tsere daket.

Gizzo ya sauko, ya taffi gida abinshi.

## 35

### The Hyæna confesses her Guilt.

Naman daji ke nan, suka taru, suka yi shawara, suka che "Dawa ya bache, ran Aljimuwa azo da safi, agammu duk, adaure mugu."

Da ran Aljimuwa ya zo, da safi, hanchi ya yi, duk suka taru wuri daya, kura ta ki zuwa. Suka yi jiranta, suka yi jiranta har la'asar, ba ta zo ba. Suka gaji, ba ta zo ba, sai suka wa'atse.

Sai da da dare suka gan ta tana zuwa suwa suwa, sai suka che "Kura, akazo akadube ki, ba agan ki ba, sai yanzu kika zo?" Sai ta che "Tun ni ban zo ba wanene akadaure?" Suka che "Ba adaure kowa ba." Sai ta che "Ashe, ni che muguniya."

Dagga ran nan kura ta san muguntata har yau, kowache sata anyi ka sani ita che ta yi.

---

## 36

### The Greedy Spider and the Birds.

Waddanan tsuntsaye ne, su hankaki. Shi ke nan, sai suna taffiya tsakkan kogi, sai suna zuwa sai suna samu abinchi achikkin tabo, dan kadainiya. Shi ke nan, kullum kullum suna zuwa. Sai ran nan sai guda daya ya fadi a kofar gidan gizzo. Sai gizzo da gari ya waye sai ya dauko, ya chi. Sai ya che "To." Sai ya je gidan tsuntsaye, sai ya tambaya su, ya che "Enna ku ke samu abin nan?" Sai suka che "Chan ne da nisa." Sai ya che "To, da zaku taffi ba kuwa yi kirra na en taffi ba?" Sai suka che "To."

Sai gari ya waye sai gizzo ya taffi gidansu, sai suka chiri fukafuken dayansu suka sa ma gizzo, suka chiri daya kuma suka sa mashi a wannan gun. Shi ke nan, sai suka tashi, suka taffi. Da suka issa gindin itche, sai gizzo kowanni ya ga ya nuna sai ya che "Wannan nawa ne." Sai suka che "To." Ko daya ba wanda ya samu abinchinsu, sai gizzo duk ya debe.

Sai gizzo da ya debe, sai suka bar gizzo ya yi barchi akan samma. Shi ke nan da zasu tashi, sai suka chiri fukafiki, sai suka taffi gida. Da suka je, sai gizzo ya faraka dagga barchi. Sai gizzo da zaya tashi sai ya che "A." Sai ya dauke dan tsinke, sai ya sa a ruwa, sai ya che "En de da ruwa nan da zurifi karan ya nutse." Gizzo sai ya jefa, sai kara sai ya taso

samma. Sai gizzo ya che "Op, ashe, ruwan ba zurifi." Sai ko gizzo ya fada achikkin ruwa. Sai da ya fada, ruwa kuwa da zurifi, ya nutse, ya mutu.

---

## 37

### The Hare outwits the Hyæna.

Zomo da kura suka taffi farauta. En de zomo ya kasshi nama, sai kura ta karbe ta jefa achikkin jekkanta. Lokachin nan sai zomo ya je, sai ya kasshi ganja. Sai kura ya zo, ya che shi ne ya kasshe. Sai zomo sai ya bar shi, sai ya gudu, ya koma abaya.

Sai ya samu koya, ya shafa a jikkinsa, ya dauke alli kuma ya shafa, duk jikkinshi ya yi furtutu. Shi ke nan, sai ya hau kan dogon shuri, sai ya zona. Sai kura kuma sai ta dawo. Da ta dawo sai ta ga abu akan shuri. Sai ta che "Abin kan shuri, mun je farauta da zomo," sai ta che "em ba ki iyakachin nama da mun kasshe ne?" Sai ta dauke nama daya ta ba shi. Sai ta che "En wuche ne?" Sai ya che "Um, um." Sai kuma ta dauke wanni ta jefa masa, sai ta che "En wuche ne?" Sai ya che "Um, um." Sai ta dauke wanni kuma ta jefa masa, har nama ya kare, saura ganja. Sai kura ta che "En wuche ne?" Sai ya che "Da sauran batsi-batsi." Sai ta fidda ganja, ta jefa masa. Sai ya kiyale ta, ta wuche.

Zomo ya je ya yi wankan jikkinshi duka, ya karba namansa.

---

## 38

### Everything comes to Him who Waits.

Wanni ke nan da matanshi. Ba suna da abinda zasu chi, sai suna ginan ramin tururuwa, suna samun dan dawa achikki, suna chi. Sai suka zo suna kwanche a daki, sai miji ya ga kadangari ya bude baki kuda ya fada achikki. Sai ya che "Ni ba na kara fitta daki ba, na taffi ginan tururuwan nan, ga kadangari yana kwanche yana samun abinchi." Sai matan ta che "To."

Sai ta taffi. Da ta taffi wanni ramin tururuwa, ta haka, sai ta ga tukuniya rufefiya, sai ta bude, ta ga liyari achikki. Sai

ta mayar, ta rufe, sai ta je ta gaya ma miji, ta che "Amma sai mu taffi tare." Sai ya che "Ai, ni ba ni zuwa, sai ki je ki kirra yan-uwanki." Sai ta je wurin yeyanta, ta gaya masu. Sai suka che "Kariya ne, da abin kiriki ne sai kin gaya ma mijinki." Sai ta che "To, mu je de ku gani."

Da suka zo, da zuwa, da suka bude tukuniya, sai suka gani kumurchi achikki. Sai suka che "To, kin gani abinda muka che ke nan. Da abin kiriki da kin gaya ma mijinki, amma muwa rama." Sai suka taffi.

Sai dare ya yi, sai suka dauka tukuniya zeye, sai suka zo, suka aje, suka tura kofan daki, suka koma. Sai da gari ya kussa wayewa, sai miji ya duba, ya ga haske a kofan daki, sai ya che "Abinchi ya zo." Sai ya bude, sai ya ga liyari ya chikka tukuniya pal. Abin nan ya ishe su, har yariniya tana diba, tana ba yeyanta.

---

## 39

### The Lazy Frog and his Punishment.

Da kwado da kaza dakinsu daya. Izan dare ya yi sai kaza ta kan che "Kwado gobe ka taffi, ka yi itache." Izan gari ya waye, kwado ya ki fitta, ya kan zona awoje a rana, ya kan che "Ba na yi itache ba, ga rana ya fitta."

Wota rana shiruwa ta zo, ta kama kwado. Kaza ta che "Ki taffi da shi mai-tataurem baya." Shiruwa ta taffi da shi. Kaza ta zona ita dakanta.

---

## 40

### The Snake and the Scorpion.

Kunama ta je wurin machiji, ta che tana so dafi idan ta halbe mutum ya mutu nan da nan. Sai ya che "Kai, Kunama, ba na ba ki ba, fushi gare ki, zaki kare mutane." Sai ta che A, a, a hankali zata yi. Sai ya che "To, je ki, gobe ki zo, na ba ki."

Shi ke nan, machiji ya fitta yawo, kunama ta zo ba shi nan. Sai ta shiga dakinshi, ta kwanta woje daya. Sai shi machiji ya shigo, ashe garin shiga ya dani kunama, sai ta ji zafi, sai ta halbe shi.

Sai ya ji chiwu, ba shi daki, ba shi woje, ba shi daki, ba shi woje, zafi ya dame shi. Sai ta che mashi "Machiji, mi ya same ka?" Sai ya che mata "Marhaba, yaushe kika zo?" Ta che "Ai, na zo tuni ne, ba ka nan." Sai ya che "Du Allah, kiyale ni, wanni abu ya same ni achikkin daki." Sai ta che "Keya, Machiji." Ta che, "Ni ne. Da ka zo, garin shiga ka dani ni ko garin en yi motsi sai na soke ka, keyan nan, ko shi ne ya yi maka zafi?"

Sai machiji ya che "Fitta, fitta, ki ba ni dakina, ba zan ba ki dafina ba, kiya kare mutum."

---

## 41

### The Spider which bought a Dog as a Slave.

Gizzo ya tashi ya je kasuwa, ya ga karnuka. A'anan ya buga dawa, sa'anan ya che zaya saye bawanshi ke nan da dawa. Sa'anan ya zo da kare gidanshi.

Sa'anan ya taffi, ya saye galma, ya ba shi, wai shi taffi gwona. Sa'anan kuma kare yana kwanche shiru. Sa'anan shi ya tashi ya kwashe galma zashi dauji, sa'anan suka taffi dauji, ya che kare shi tashi shi yi noma, shi ko shina kwanche. Sa'anan ya nuna wurin noma, ya che idan sun yi baki hakka su tashi, sa'anan kare yana kwanche shiru. Sa'anan shi gizzo ya soma yin noma da kansa, kare ya kwanta abinshi. Sa'anan gizzo ya che kare yana lumfashi ya gaji, shi kwanta abinshi.

Sa'anan shi kare yana kwanche, naman daji gadda ta zo, kare ya tashi, ya gudu, ya kama gadda. Sa'anan ya che ashe, bawansa mahalbe ne, en ji gizzo. Ya che "Wanda ya halbe da hakori, balle ya samu kibiya." Ya dauke galman kare, ya ba biri, wai akira mashi kibiyoyi, sa'anan aba kare. Sa'anan shi kare ya koma gida, gizzo ya koma gida.

Sa'anan gizzo, kullum ya kan taffi wurin biri, biri ba ya kera mashi yau ba. Sa'anan biri ya tambaya gizzo, ya che "Ka samu bawa ne?" Ya che "I, shi ne ina yi mashi kibiyoyi ya ji dadin halbe." Sa'anan gizzo da ya che zaya zo da kare, biri ya che kadda ya zo da shi. Sa'anan gizzo kullum ya kan zo wurin biri, ba ya yi mashi kibiyoyi da saure ba. Sa'anan gizzo ya yi fushi ya zo da kare. Kare yana hange biri, yana kwanto, sa'anan sun zo kussa, biri ya gudu, kare ya gudu, ya bi biri ya kama shi. Da yana zuwa da biri, gizzo ya che "Barri, makeranka ne, kadda akama shi." Sa'anan gizzo kuma ya yi gudun

kare, ya wuche gida aguje, ba ya shiga gida ba, ya che ma matanshi "Ki tashi ki gudu, ga kare yana kama mutane yana chainye mutane."

Sa'anan da suka gudu, sun bar ma kare gida. Sai kare ya yi gadon gida kuma. Sai gizzo suka taffi dauji, da shi da matansa.

---

42

THE WOOING OF THE BASHFUL MAIDEN.

Wannan de, dan sariki ne, da shi da yaran gari. Shi kuwa yaron, sunanshi Musa. Sai shi ke nan wata yariniya mai-keyau tana son sa da aure, shi kuma, ba ya son ta. Ita kuma tana jin kuniyan shi.

Shi ke nan, sai ran nan yam-mata suka tashi, suka taffi kogi wanka, suka taffi, suka kwanche zannuwa, suna wanka. Sai ya zo, yaro, ya kwashi fatari, ya hau kan rimi. Sai shi ke nan, kowache ta yi wanka, sai ta duba, ba ta ga fatari ba. Shi ke nan, en ta duba ta gan shi, sai ta che "Musa, ba ni fatarina." Sai ya sauko mata. Da ya ba ta, sai ta taffi. Shi ke nan, da ta taffi sai daya ta fitto, ta duba, ba ta ga fatari ba, sai ta che "Musa, ba ni fatarina." Sai ya sauko mata, sai ta taffi.

Sai saura daya, wache yariniya da ta ke son shi. Shi ke nan sai ta che "Wane, wane, ba ni fatarina manna." Sai ya hanna. Shi ke nan, sai ruwa ya kama ta gwiya. Sa ta che "Wane, ba zaka ba ni fatarina ba?" Sai ya che "Ba zam ba ki ba sai kin fadi sunana, Musa." Ruwa kuwa ya kama ta wiya, ruwa yana karawa. Ita kuwa, ba ta so ta fitta sarara, tana jin kuniya. Shi ke nan sai ta che "Wane, ba ni fatarina." Ya ki. Ruwa kuwa ya sha kainta kaman zata mutu. Sa'anan ta che "Musa, ba ni fatarina manna." Sa'anan sai ya sako mata fatari. Sai ya figo bulala, ya yi ta dukan ta.

Shi ke nan, sai ya kama ta, ya taffi da ita gida. Ran nan kuma ya son ta. Sai akadaure masu aure.

---

43

THE GIRLS AND THE UNKNOWN YOUTH.

Wanni yaro duk ba mai-keyaunshi, duk gari. To, sunanshi kuwa, Denkin Deridi. Sai yam-mata duka suna son shi. Sai ya che sai wadda ta san sunanshi, ita che matanshi. To, duka

garin kuwa, ba wanda ya san sunanshi sai wota tsofuwa. To, yam-matan nan duka suka yi ta daffa. Ta-fari ta daffa shinkafa, wannan ta soye nama, wannan ta yi tuwon farafara, wannan ta yi fura na maiwa, wannan ta daffa gwaza, wannan ta daffa risga, wannan ta daffa dadawam basso, mai-wari.

Shi ke nan, sai yaro ya gina daki, ya rufe, duk ba kofa. Da yam-mata duk da zasu zo wurinsa, sai tsofuwan nan ta zo atsakan hainya, tana wanka da ruwa, kowache buduruwa da zata wuche, sai tsofuwa ta che "Zo ki chuda ni." Sai ta che "Kai, rabu da ni, zani wurin sauraye ban san sunanshi ba." Sai tsofuwa ta che "To." Duka yam-mata suka wuche ta, sai mai-kayan dadawam basso ta zo. Sai tsofuwa ta che "Ke, Yam-mata, zo ki chuda ni." Sai ta che "To." Sai ta sauke, ta chude ta. Da ta gamma wanka, sai tsofuwa ta che "To, sunan sauraye 'Denkin Deridi?'" Ta che "To."

Sai suka taffi duka Mai-daffan shinkafa tana gabba, sai ta zo, ta che "Samari, zo ka bude mani kofa, en shigo." Sai shi ya che "Wanene nan en bude mata kofa ta shigo?" Sai ta che "Ni ne Shinkafa, mai-dadin tuwo." Sai sauraye ya che "To na ji naki sunan, ke ki fadi nawa." Sai ta che "Ban san sunanka ba, Dan Yaro." Sai ya che "To, koma da baya." Sai ta koma, tana kuka.

Sai Mai-sauyen nama ta zo, ta che "Samari, zo ka bude mani kofa, en shigo." Sai ya che "Wanene nan en bude mata kofa, ta shigo?" Sai ta che "Ni ne Sauyen nama duk da gisheri." Sai sauraye ya che "To na ji naki sunan, ke ki fadi nawa." Sai ta che "Ban san sunanka ba, Dan Yaro." Sai ya che "To, koma da baya." Sai ta koma, tana kuka.

Sai Mai-farafara ta zo, ta che "Samari, zo ka bude mani kofa, en shigo." Sai ya che "Wanene nan en bude mata kofa, ta shigo?" Sai ta che "Ni ne Farafara, tuwon mai-dadin hadiye." Sai sauraye ya che "To na ji naki sunan, ke ki fadi nawa." Sai ta che "Ban san sunanka ba, Dan Yaro." Sai ya che "To, koma da baya." Sai ta koma, tana kuka.

Sai Mai-maiwa ta zo, ta che "Samari, zo ka bude mani kofa, en shigo." Sai ya che "Wanene nan en bude mata kofa, ta shigo?" Sai ta che "Ni ne Maiwa, mai-dadin fura." Sai sauraye ya che "To na ji naki sunan, ke ki fadi nawa." Sai ta che "Ban san sunanka ba, Dan Yaro." Sai ya che "To, koma da baya." Sai ta koma, tana kuka.

Sai Mai-daffan gwaza ta zo, ta che "Samari, zo ka bude mani kofa, en shigo." Sai ya che "Wanene nan en bude mata kofa, ta shigo?" Sai ta che "Ni ne Gwaza, maganin yunwa." Sai

sauraye ya che "To na ji naki sunan, ke ki fadi nawa." Sai ta che "Ban san sunanka ba, Dan Yaro." Sai ya che "To, koma da baya." Sai ta koma, tana kuka.

Sai Mai-daffan risga ta zo, ta che "Samari, zo ka bude mani kofa, en shigo." Sai ya che "Wanene nan en bude mata kofa, ta shigo?" Sai ta che "Ni ne Risga, mai-dadin sabi." Sai sauraye ya che "To na ji naki sunan, ke ki fadi nawa." Sai ta che "Ban san sunanka ba, Dan Yaro." Sai ya che "To, koma da baya." Sai ta koma, tana kuka.

Duka suka kare sai Mai-dadawam basso. Da ta zo, sai yam-mata suka che "Ke, dan-durinuwa, masu-keyau ba sun samu ba, barri ke, mai-wari." Sai suka che "Abar ta de, muwa gani abinda zata yi." Sai ta zo, ta che "Samari, zo ka bude mani kofa, en shigo." Sai ya che "Wanene nan en bude mata kofa, ta shigo?" Sai ta che "Ni ne, Dadawam Basso, mai-kamshi." Sai sauraye ya che "To, na ji naki sunan, ke ki fadi nawa." Sai ta che "Sunanka, Dan Yaro, Denkin Deridi." Sai ya che "Shigo daki, Yam-mata." Sai ya bude kofa, ya che ita che matanshi

Sai Mai-shinkafa ta che asara kanta ayi murufu da shi don takaichi. Sai Mai-nama ta che asara kanta ayi murufu da shi don takaichi. Sai Mai-farafara ta che asara kanta ayi murufu da shi don takaichi. Sauran suka che "Ni na dibo maki ruwa," "Na yiwo maki itache," "Mu, muwa zona, muwa yi maki nika."

---

## 44

### The Son of the King of Agaddaz.

Wannan de, matanshi su biyu, kowache ta haife mache, uwar daya ba ason ta. Shi ke nan, akaje, akayi mata daki abakin juji gunda akezubar da shaara. Shi ke nan, sai ta zo, ta zona. Da ta zona, shi ke nan, sai tuwon dusa ta ke chi.

Sai shi ke nan, sai mijin zashi chiwo kasuwa shi ke nan, sai yar wache ba aso ta che "Baba, ga kurdi nan, asayo min Dan Sarikin Agaddaz." Sai ya zage ta. Sai ta che "En ka je, ka sayo min Dan Sarikin Agaddaz." Sai ya karbe kurdi biyal.

Da ya je kasuwa, sai ya che "Enna Dan Sarikin Agaddaz?" Sai akafada shi da duka, akache "Dan Durin uwanka, don minene ka che enna Dan Sarikin Agaddaz?" Akarufe shi da

duka, ya yi lilis. Shi ke nan, sai suka che "To, ku kiyale shi hakka, Taffi gida kuma."

Da zaya tashi ya taffi, sai dan Sarikin Agaddaz ya che "En ka taffi, ka gaya ma yariniyan nan ran Jimuwa ina zuwa." Shi ke nan, sai ya che "To." Sai ya taffi.

Da ya je, sai ya yi kirran yariniya. Da ya kirra ta sai ya kama ta, sai ya daure. Da ya daure sai ya dauka bulala, sai ya yi ta dukan ta. Shi ke nan, sai da ya duke ta, ya gaji, sai ta tashi. Sai ya che "Ki gara, ran Jimuwa iya zuwa." Sai ta taffi tana kuka. Sai ta che "To."

Shi ke nan, kaman gobe Jimuwa, sai ta shashara daki, ta gagara, ta shimfida tabarimi, shi ke nan, sai ran Jimuwa ya zo ya sauko kan daki, duk gari ya yi barchi, sai ita kadai, yariniya, ba ta yi barchi ba. Shi ke nan, sai ya zo, ya sauko kan gado. Ta sayo goro da turare, ta aje, da ya zo, ya sauko sai ta dauka ta ba shi, iya chi. Shi ke nan, da ta ba shi, sai en ya taffi sai azurufa. Sai yariniya ta kwashe. Ta kwashe, ta zuba a tukuniya, ta rufe. Sai ya ga azuba ya yi, sai ya tashi, ya taffi gida.

Shi ke nan, sai kullum iya zuwa kullum. Sai ran nan sai sun barri yariniya ta fitta, sai sun ga ta ta chikka tukane da azurufa. Shi ke nan, sai mutanen gida suka zo, suka sa alura akan gado, suka sa alura kaman dari. Shi ke nan, sai ran nan da ya zo, ita kuma, yariniya, ba ta nan ba, da ya sauko akan godo sai alura duk suka soke shi. Sai ya mutu. Shi ke nan, sai yariniya ta zo, ta taras ya mutu. Shi ke nan, sai ta dinga kuka, ta che yaya zata yi, dan Sariki ya mutu a dakinta.

Shi ke nan, sai shi, uban yaro ya ji labari, sai yariniya ta che "Ka ji, ka ji, ni ban sani ba." Sai akazo, akakama iyayen, ita yariniya akabar ta. Su ma, iyayen, akaba su wahala, shi ke nan, akaba su wahala har suka mutu. Da suka mutu, sai akakirra yariniya, akache "Is, kadda ki kara yin wannan, ba shi dakeyau." Ya che "Kin gani, kin kare min dana," ya che "Yanzu en kasshe ki, ko en bar ki?" Shi ke nan, sai ta che "A, abinda ka yi da ni duk shi ke nan, en ma ka kasshe ni ne, ni na ja wa kaina." Sai sariki ya bar ta, sai ya ba ta daki achikkin gidansa, sai ya ba ta dukiya. Ta zona. Shi ya ji tausayenta.

## 45

### The Boy who became his Rival's Ruler.

Wanni mutum mai-iyali dayawa, da mata da kwarakwarai pal gidanshi, ba ya samu da ba. Ya kan taffi wurin wanni, ya kan che " Ba ni magani ko na haife da." Shi kan che " Ba ni da shi ba." Har ya taffi wurin wanni Mallami, ya che " Sai ka taffi ka zona adauji, ka rikka tuka igiyan doki kana sayasuwa, kana tara kurdi, sa'anan ka saye baiwa, mache, sa'anan ka sa daki ka samu da."

Ya taffi dauji, ya zona, shina taran kurdinshi. Ya tara kurdi dayawa, ya saye baiwansa, sai baiwa kuma ta samu chikki ta haife danta namiji. Sa'anan ya tashi, ya taffi gari neman wanni kurdi kuma, ya aje. Sa'anan ya koma dauji. Yaro ya yi wayo, ya issa samari, shina zuwa chikkin gari, yana yawo, yana barri ubanshi awoje. Ya zo ya samu wanni dan sariki a turaba. Ya che " Kai yaro." Ya che " Um." Ya che " Ba ka raka ni ba?" Yaro ya che " To." Suka taffi gidan karuwaye, yaro yana rikka masa doki. Dan sariki ya fitta kuma, zashi gida. Suka zo hainya, dan sariki ya che " Kai, ka taffi gidanka, ni zani gida." Yaro ya kama hainya, ya taffi. Ubansa ya che " Ka taffi enna tunda safi?" Ya che " Na taffi chikkin gari garin yawo."

Da safi kuwa yaro ya sake zuwa gari garin yawo. Dan sariki kuwa ya sake zuwa. Ya che " Kai Yaro, tashi, mu koma wurin jiya." Yaro ya tashi, suka taffi. Ya sauka bissa doki, ya ba yaro rikkan doki. Mata suka fitta, suka che " A, ga yaro kekeyauwa anaba shi rikkan doki?" Dan sariki ya ji fushi, ya fitta, ya karbe dokinshi, suka mika, suka taffi. Yaro ya taffi gida, ya che da ubanshi " Ka bar ni ba bante ba komi? Ba ni da riga, ba ni da wando, ba ko rawani, ba fula." Uban ya tashi, ya taffi chikkin gari da da dare, ya bude dakin dukiyanshi, ya debo tufafi, ya kawo ma yaro.

Da safi yaro ya kama turaba, ya koma wurinda ya kan zamne. Dan sariki ya zo, ya che " Kai aron riga ko samu?" Yaro ya che " Um." Ya che " Tashi mu taffi." Yaro ya che " To." Suka zo dakin matan nan dan sariki ya sauka, ya che da yaro shi kama doki, yaro ya che " A,a," ya ki. Suka shiga daki tare da dan sariki wurin matan. Suka gamma abinda su ke yi adaki, suka fitta. Dan sariki ya che " Kai yaro." Yaro ya che " Um." Ya che " Abinda kowa ya chi a gidansa, gobe akawo shaida." Dan sariki ya koma gida, shi yaro kuma, ya koma gida.

Dan sariki ya che "Ayi tuwon dawa, ayi na gero, ayi na tamba, ayi na atcha, ayi na shinkafa, da na aburu kuma." Akayi masa, dan sariki ya chi. Shi yaro ya taffi gida, ya che "Akawo mani nono, akawo mani nono a kwariya." Ya che akawo mashi azurfa pal, akakawo dayawa. Yaro yana shan nono, yana zubar da azurfa abaki, yana hadiye.

Safi ya yi, yaro ya kama hainya, ya zo wurin. Dan sariki ya zo kuma, ya che "Yaro, ka zo?" Ya che "Um." Ya che "To, mu taffi." Suka kama hainya, suka taffi gidan mata. Ya che "To, kowa ya nuna shaida abinda ya chi jiya." Dan sariki ya rikka yin amai, yana amai, yana amai, da tamba, da atcha, da shinkafa, abinda ya chi duka, don mata su gani suna da koshi a gidansu. Yaro ya che "To, ka kare?" Ya che "Ba ni wuri, ni kuma," Yaro kuma ya yi nashi, ya yi amai, ya yi amai, har mata suna wasoson abinda yaro yana amai nan, suna yi murna da yaro. Dan sariki ya gudu, yana jin kumya.

Sa'anan yaro ya taffi gida, ya che da uban "Mu tashi dagga kauyen nan, mu shiga gari." Suka tashi, suka shiga.

Ya tambaya, ya che "Dan sariki yana da uwa?" Akache "Shina da uwa," akache "tana nan." Yaro ya tashi ya taffi ya sa ankawo mashi azurfa dumke biyu, ya kai makeri ya che ayi mashi mazari guda goma. Ya sa uban ya kawo siliya, ya che atuka mashi tsaiwa da shi. Ya tashi ya kama turaba yana rikken mazarin da goro guda goma a hanu. Ya taffi hainyar rafi ya je ya zona, wanni ya nuna masa yar uwan dan sarikin nan. Sa'anan ya kawo mazarin da goron nan guda goma mainya mainya, ya ba yariniya, ya che ta kai ma uwanta. Ta shiga gida ta che "Sauke ni." Uwan ta ta che "Kullum ki kan zo ban sauke ki ba sai yau?" Da ta fitta, ta dauke kwariya, ba ta ji ruwa da nauyi ba, zata yi magana, yariniya ta che "Yi shiru." Suka shiga daki, ta bude kwariya, sai ta gani mazari achikki, da goro guda goma, kaman kain barawo. Sa'anan ta che "Wanene ya aike ki?" Ta che "Wanni ya che agaya maki yana zuwa dayamma." Ta che "Enna zaya biyo shi zo?"

Sa'anan yarta ta koma wurin yaro ta che "Enna zaka biyo ka zo?" Yaro ya che "To, minene a turaba?" Ta che "Gidammu da zaure uku ne, wannan zaure karre goma masu-kumu achikki, wannan zaure bawa goma, wannan zaure kuma dabam doki goma. Dowaki suna chin kasshin sa, karnuka suna chin chiyawa, bayi ba su shan komi ba sai konwa." Ya che "To."

Dare ya yi, yaro ya sa ubanshi ya yanka sa goma, akachiri

mashi kain sa goma. Ya sa yara goma su yanka chiyawa, ya samu riga da gamman taba kuma guda goma. Ya tashi ya kama hainya zashi gidan sariki. Ya zo ya shiga wannan zaure, ya zubar ga dowaki chiyawa. Dowaki suka che "Ga abinda mu ke so, yau amba mu." Ya wuche, ya taffi wurin karnuka, suka yi "Wu, wu, wu." Akazubar masu kain shanu, suka che "Mu ba masu-chin chiyawa ba, ga shi yau Allah ya ba mu nama." Yaro ya wuche wurin bayin nan, kowani bawa ya tashi da adda a hanu. Sai ya ba dukansu keyauta, kowa ya ba shi riga da taba. Sa'anan ya wuche ya nemi kofar inda tsaiwa ta ke ya shiga chikkin gidan uwan dan sariki. Shina rikke da tulun wardi a hanu, ya passa shi achikkin dakin uwar gida. Sa'anan ya daure tsaiwa, ya kwanta.

Safi ya yi, sariki ya fitta woje, ya zona, ya zo zaure ya ga bayinshi da riga duk, ya wuche ya iske karnuka da kain shanu, ya zo wurin dowaki kuma, ya ga suna da chiyawa. Sa'anan ya che da mutane awoje, ya che "Ashiga, agaya ma yaronda chikki shi ne sariki, yau ni na fitta, wanda ba ta son shi sariki ta fitta ta bi ni, wadda ba ta son na ta zona abinta."

To, ga sarikin gari ke nan wannan yaro, ya yi sarauta. Da safi kuma dan fittachen sariki ya zo, ya gaishe shi, ya che "Baba barka da kwana." Yaro ya che "To, ga shi, dana ya zo." Mutane sun che "Ga shi, suna haminiya akan mata, ga shi kuma shi ne ya zamma ubanshi."

---

## 46

### The Wild-Cat and the Hen.

Wannan de kaza che. Sai ta yi aure da muzuru. Muzuru kuwa, sai ya che ta kirra danginta duk su zo su yi biki. Shi ke nan, sai biki ya taru. Sai muzuru ya boya chikkin daki. Sai kowache kaza ta zo ta duba daki, sai ta ga idon muzuru.

Sai shi ke nan, sai biki duk ya taru, sai muzuru ya hara, ya farfaro wurin kaji, ya kasshe. Da dare ya yi, sai muzuru ya gaya wa matansa ta hau gado, ta kwanta. Da ta kwanta, sai ya murda mata wiya, ya chainye.

---

## 47

### The Dishonest Father.

Kurichiya da abuyanta zasu kwarto. Da suka taffi, sai kurichiya ta samu kwarto, ta chi, ta hanna ma abuya. Sai ta yi fushi, suka koma gida.

Sai uban kurichiya ya faye rikichi, sai ya che "Zamu gudu," wai rikichinsu ya yi yawa. Sai ya che ta yi dakka. Tana dakka, tana waka "Dakkan guzuri mu ke yi, Baba ya chainye kurdin mutane, ko da safi ko da mareche zamu gudu, mu bar garin."

Sai uban ya che kaka zasu yi kuma, rikichinsu ya faye yawa.

Sai suka taffi, ya baida danshi aure, ya daya miji fudu. Sai akakirra makadda, anakiddi, anache mashi shi bar rikichi. Sai ya che abar rikichi ya chi mi? Sai akache "To, namiji daya ya biya kurdi duka." Sai ya biya, sai ya zona da matanshi.

---

## 48

### The Contest for Dodo's Wife.

Wata mache che, matar Dodo che, Dodo ne ya fitto dagga daji ya zamma mai-mache. Sai ta zo ta kawo wanni dan kwotashi, sai ta zo ta aje kwotashi a bakin korofi enda mutane suna rimi. Shi ke nan, sai ta aje, ta che "Wanda ya ture kwotashi, shi ne mijina."

Sai mutane suka yi ta jefa—su ba su sani ba ita ta rigaya ta yi aure da Dodo—suka gan ta mache mai-keyau. Shi ke nan, sai mainya mainya suka yi ta jefa, suka kasa budewa. Shi ke nan, sai wanni yaro kankani shi ya rage, ba ya jefa ba. Akache "Dauke de ka jefa." Sai ya che "Mainya suka yi suka yi ya ki budewa, barri ni." Shi ke nan, sai ya dauke zakuwa kankani, sai ya jefa, sai kwotashi ya budu. Shi ke nan, sai akache shi ne mijinta. Sai akadaura masu aure.

Shi ke nan, sai ankwana ashirin, sai mata ta che zata garinsu ta gano gidansu. Shi ke nan, sai yaro ya che "To." Shi ko yaro, ubanshi mahalbe ne, duk wurin ubanshi ya sani. Shi kan rikidda giwa, shi kan aikidda zaki, duk ya ke rikiddawa. Sai ya sani mache matan Dodo che, shi yaron kuwa ya sani.

Shi ke nan, sai suka taffi daji, yaro ya taffi ya rako ta gida.

Shi ke nan, sai suka taffi chan daukan daji, sai ta che " Bar en yi fisari yanzu." Sai ta je ta rikidda Dodo, sai ta zo zata chainye yaro. Sai yaro, shi ma, ya rikidda zaki, sai ta damfaro kan shi, sai ya zamma machiji. Shi ke nan sai ta bar shi, sai yaro sai ya zamma tsuntsu sai ya gudu.

Sai ya zo ya fada a gida. Shi ke nan sai iyayen suka che " A, mun gaya ma, kadda ka aure ta." Shi ke nan, sai iyayen suka che " En ka aure mache, bar gaya mata asirin gidanku." Shi ke nan, sai ya che " To."

---

## 49

### The Man and his Lazy Wives.

Wanni de manomi ne da matansa uku suna noma a gwonansu. Sai ran nan, sai su mata suka che ba zasu kara yin noma ba, sun gaji. Sai mijinsu ya che " To." Sai ya yi dabara. Ya yi bante guda uku, ya boye. Sai da safi ya kirra uwar-gida ya che " Sa banten nan, na ba ki, ki daure, amma kadda ki fadi ma kishiyoyinki fa. Da wanni maganin haifuwa achikki, ki daure kiya samu da, namiji." Sai ta che "To, da keyau."

Da ta taffi, sai ya kirra mai-binta kuma, ya che " Ga banten nan, na ba ki, ki daure, amma kadda ki fadi ma kishiyoyinki fa. Da wanni maganin haifuwa achikki, ki daure kiya samu da, namiji." Sai ta che " To, da keyau."

Sai kuma ya kirra amariya. Da ta zo, sai ya che " Ga banten na ba ki, ki daure, amma kadda ki fadi ma kishiyoyinki fa. Da wanni maganin haifuwa achikki, ki daure kiya samu da, namiji." Sai ta che " To, da keyau."

Sai suka taffi gwona, da miji da mata su uku. Da suka zo suka yi ta noma, sai mijin ya yi masu waka, ya che " Massa, massa, Mai- dan - Bante, massa, massa, Mai-dan-Bante." Sai suka kara saure, suka yi aniya, suka aiki da gaski. Suna buga kassa baki daya, suna tsere da juna.

Sai uwar gida bantenta ya dame ta, sai ta chiri, ta che " Ba na iya aiki da wannan ba." Sai da ta chiri sai ta gaji sosai. Ta che " Ashe, amba ni bante don na yi aiki dayawa, to, ba ni so kuma." Sai da waddansu suka ji, suka che " Op, hakka nan ne anyi mamu wayo ? " Sai suka kwanche bantensu kuma, suka chiri. Sai mijin ya che " To, da ba na yi maku hakka ba, da ba ku yi aiki da keyau ba." Sai ya che " To, mu koma gida." Sai suka koma.

## 50

### The Two Wives, the Hyæna, and the Dove.

Wannan de miji da matansa biyu, suna nan. Dayan mache tana da dukiya, daya kuma ba ta da shi. Sai ran nan uwargida, maras-dukiya, ta che "To, zani dauji." Sai mijinta ya che "To." Sai shi ke nan, sai ta taffi, tana taffiya, tana taffiya, sai rana ya fadi, dare ya yi kuma. Sai ta che "Allah shi ba ni daki karami," sai ta ga gida baba agabban ta. Sai ta zo, ta shiga, ta ga ba komi achikki, sai ta che "Allah shi ba ni tuwo." Sai ya ba ta. Sai ta koshi, ta che "Allah shi ba ni gado." Shi ke nan, sai ya ba ta, sai ta kwanta.

Shi ke nan, da zata kwanta, ta ji kurichiya tana kuka tana chewa "Yi kununki ki sha." Sai mata ta che "To wanni irin tsuntsu yana fadi hakka?" Sai ta tashi, ta yi kununta, ta sha.

Sai da da dare kura ta zo, tana kuka, tana chewa "En zo dandalin sariki? En zo dandalin sariki?" Sai mache ta rufe kofa, sai kura ta taffi abinta.

Shi ke nan, sai da tsakan dare ya yi, sai Dodo ya zo, yana kuka, yana chewa "En zo dandalin sariki?" Sai mache ta tashi ta bude kofan zaure, sai Dodo ya shiga. Shi ke nan da ya shiga, sai ta gudu, ta shiga daki ta boye. Sai Dodo ya zo, yana chewa "En shiga dakin sariki?" Sai mache ta bude kofan daki, ta gudu, ta shiga tsariya. Sai shi ke nan, sai Dodo ya zo, ya shiga daki, ya hau gado. Sai ya chiri rigansa da wandonsa, ya kwanta. Sai da safi ya zubar da kurdi azurifa, da riguna, da wanduna, da dukiya, duk ya barri mata sai ya taffi. Shi ke nan, da ya taffi, sai machen nan ta tara dukiya, ta zo gida da su, ta nuna ma mijinta.

Shi ke nan, sai ran nan kishiya ta che "To, ni kuwa zani dauji." Sai mijinta ya che "A, a dukiya ya issa mu duka." Sai ta che "En taffi de." Sai ya che "To." Sai shi ke nan, sai ta taffi, tana taffiya, tana taffiya, sai rana ya fadi, dare ya yi kuma. Sai ta che "Allah shi ba ni daki karami," sai ta ga gida baba agabban ta. Sai ta zo, ta shiga, ta ga ba komi achikki, sai ta che "Allah shi ba ni tuwo." Sai ya ba ta. Sai ta koshi, ta che "Allah shi ba ni gado." Shi ke nan, sai ya ba ta, sai ta kwanta.

Shi ke nan, da zata kwanta, ta ji kurichiya tana kuka, tana chewa "Yi kununki ki sha." Sai mata ta che "To, wanni irin tsuntsu yana fadi hakka?" Sai ta ki tashi. Sai ta dauke sanda

ta buge kurichiya, ta kasshe. Sai shi ke nan, sai ta daffa, ta chainye.

Sai da da dare kura ta zo, tana kuka, tana chewa "En zo dandalin sariki? En zo dandalin sariki?" Sai mache ba ta ji ba, tana barchi. Sai kura ta zo, ta kama ta, ta chainye.

Shi ke nan, sai da safi wota kurichiya ta ji labari, ta zo ta gaya ma mijin. Sai ya che "To, ai na gaya mata kadda ta taffi, ga shi, ta samu kanta." Sai kurichiya ta che "To," ta taffi. Sai suka zona da uwar-gida, ita daya.

---

## 51

### The Man and his Wives, and Dodo.

Wanni miji ne, yana da matanshi biyu. En ya taffi dauji, sai ya bar karnukansa a daki, ya daure. Sai ya che wanda ya kunche su, da ya dawo sai ya ba ta kashi.

Sai ran nan sai ya dauke sarewansa, ya taffi dauji. Sai yana taffiya, yana taffiya achikkin dauji, sai Dodo ya hange shi, sai ya zo. Sai ya gudu, ya hau bishiya, ya dauke sarewa, yana busa. Dagga chan sai kare suna ji, suna yi ta kuka. Sai uwar-gida ta che "Op, mi ya sa kare suna kuka hakka? Sai en kunche su." Sai kishiya ta che "A, a, kadda ki kunche su, uban-giji ya che wanda ya kunche su da ya dawo sai ya ba ta kashi." Sai uwar-gida ta che "Zan kunche." Sai ta che "To, ki yi." Sai ta kunche. Da ta kunche sai karnuka sun yi ta gudu, sun yi ta gudu sai sun zo bishiya. Sai da zuwansu, sai Dodo ya gudu, kare suna bin sa. Sai suka kama shi, suka kasshe Dodo anan.

Sai da suka kasshe, sai mutumen nan ya koma gida, ya che "Wa ya kunche kare?" Sai kishiya ta che "Ita che, ta kunche, ni ma na che kadda ta yi." Sai mijin ya che "Da ba ta kunche, da Dodo ya kama ni." Sai ya ba ta kashi, ita kishiya, ya kawo dukiya ya ba uwar-gida.

---

## 52

### The Wife who would not Work Alone.

Wanni mutum de, da shi da matansa daya. Ana nan suna zone, ana nan, suna zone, har shakara tara. Sai ran nan, ita matan ta che "Mai-gida." Sai ya che "I." Ta che "Kai wanni irin mutum ne?" Sai ya che "Domi kina che ni wanni

irin mutum ne? Mi kika gani?" Sai ta che "Abinda na gani, ni ina zone nan shekara tara ni kadai, ba za'ayi mani wanni kishiya ba?" Sai ya che "A, a, ba ni so en yi maki kishiya ba kadda hankalinki ya tashi." Sai ta che "A, a, hankalina ba zaya tashi ba, ni ma en nemo maka mata." Sai ya che "To, nemo mani manna, mutum zaya ki, aure?"

Sai ta taffi, ta kirra abuyanta, bazawara, ta kawo ta gida. Suka shiriya. Da safi kuma akadaure masu aure. Sai suka zone da amariya. Sai mijin nan, komi da ya samu sai ya kai dakin amariya, ba ya kai komi dakin uwar-gida ba. Ya tashi dakin uwar-gida, yana kwanche da amariya.

Kullum kullum hakka, sai ran nan sai uwar-gida ta zo, ta che "To," ta che "Mai-gida." Sai ya che "I." Ta che "Wa ya kawo maka amariyan nan, ba ni ne ba?" Sai ya che "Ke ne." Sai ta che "To, ba ni son ta kuma, sai ta fitta dagga gida, sai ka kore ta." Sai ya che "A, a, muna tare da ke, ke ne kin che kina so en yi maki kishiya, ba ni na nemo ta ba. To, ni yanzu ba na kore ta ba." Sai uwar-gidi ta che "Ni fa, ba na yarda da ita, sai ka kore ta." Sai ya che "A, a, ke ne zaki taffi." Sai ya kore ta.

Da ya kore ta, ta che "Wayo, da na sani da ban yi hakka ba." Ta che "Kowa ya hau dokin 'da na sani' sai ya sha wahala."

---

## 53

### The Thoughtful and the Thoughtless Husbands.

Wanni ne, da shi da abokinsa suka tashi suka taffi yawo. Da suka taffi yawo, suna yawo, sai suka samu diniya. Sai suka hau—kaman zuma ya ke dadinsa. Sai abokinsa ya che "Mu chainye kadan mu kai gida." Shi ke nan, sai ya che "To." Abokinsa en de ya fuse, sai ya sa achikkin jekkansa. Lokachin nan abokinsa ya che "To, mu taffi gida kuma." Ya che "To, mu taffi." Suka taffo gida.

Suka zo. Da dare su ke kwanche da matansa, sai abokinsa sai ya debe diniya, sai ya bai matansa. Da ta chi, sai ta ragi kankani. Lokachin nan da safi da ta tashi, ta taffi wurin matan abokin mijinta, sai ta kawo dan diniyan nan, ta bai wa wanchan. Sai ta che "Ke, mijinki ba ya kawo maki ba?" Sai ta che "A, a, ba ya kawo mani ba."

Shi ke nan, sai suka tada fada da mijinta a gidansu. Sai

ta che kaka ita, mijinta ba ya kawo mata diniya ba. Sai ya che "Bar en taffi en kawo maki." Da ya je, ya hau bishiyan diniya, sai kura ya zo, ya tsaya a karkashin bishiyan diniya. Sai zaki kuma ya zo. Sai shi, mutumen nan na sama, sai ya soma waka, ya che "Ya kura, kure bangaya." Sai kura ya tashi ya yi rawa, ya taffi. Zaki kuwa ya bi ta. Da suka taffi, sai shi mutum, ya sauko, ya gudu har gida. Sai kullum kullum yana kai wa matansa diniya.

---

## 54

### Solomon and the Birds.

Wota mache, matar Annabi Sulimanu, ta shiga wanni gida, ta ga mata ta yi dabbi, ta garta gidanta dakeyau. Ta che "Kin sa mine a dabbinki ye ya yi keyau hakka?" Ta che "Mijina ya halbe naman daji dayawa, na tara jininsu na sa."

Sa'anan ita kuwa ta koma gida, Sulimanu ya yi magana da ita, ta yi shiru. Ya che "Mine ya same ki kina fushi ye?" Ta che "Na taffi, na gaida abuyana, na ga dabbinta dakeyau, mijinta ya halbe naman daji, ya ba ta jini, ta sa dabbinta, ga tsuntsaye duka suna yi maka lema, sai ka debo tsuntsu ka yanke, ka ba ni en sa dabbi." Ya che "To, gobe adebe, aba ki." Ta che "To, Allah ya kai mu gobe."

Tsuntsu da safi ba sun zo ba, sai da hanchi ya yi, sarikin tsuntsu ya fadda fadda, ya zo wurin zakarra. Ya che mashi "Ka ji ka ji abinda Sulimanu ya fadi jiya ye?" en ji zakara. Ya che "Mine?" Ya che "Annabi Sulimanu ya che zaya yanka mu." Sarikin tsuntsu ya che "To, bar en koma gida."

Wallaha ta yi, sarikin tsuntsu ya komo, Sulimanu ya che "Ka tsaya achikkin gari tunda safi ba ka zo ba?" Ya che "Ana magana guda uku a gidana." Ya che "Minene gardama da tsuntsaye suna yi?" Ya che "Suna tambaya 'da dare da rana, wa ya fi yawa ye?' Ni kuwa na amsa 'da safe tun anakirran salla har yamma har kussan barchi, duk rana ne, ai rana ya fi yawa.' Sa'anan sun che kuwa fa, 'da mazza da mata, wanene sun fi yawa ye?' Na che 'mata,' na che 'miji ina amsa maganan mata, shi kuwa mache ne.'" Sa'anan Sulimanu ya che "Ka tashi abinka."

Sa'anan mata ta fitto, ta taffi gidan mai-dabbin nan. Ta che "Ashe, na yi maki maganar wasa, ke, kin karba da gaski, sa'anan kin taffi kin fada ma annabi? Itache ne na sara, na dakka, na sa ruwa na zubar a dabbi, sa'anan na yi maki wasa."

## 55

### The King who coveted his Son's Wife.

Wannan che de, yariniya, sunanta Kwallabbe, mumuna che da ita. Shi ke nan, sai uwar sai ta turo ta gari, ta che "Je ki, ki nemi gida, ki zona." Sai ta taffi, ta je gidan sariki, akakarbe ta, ta zona.

Shi ke nan, dan sariki en ya zo chin abinchi, sai ya che "Agusa da ita," wai ta chikka muni, shi ba ya son ta ba. Shi ke nan, sai yariniya ta koma gun nata, sai ta che "Iya, ba su son na, suna nema su kore ni a garin." Shi ke nan, sai uwar ta hadiye ta, ta fitta da ita mai-keyau. Sai ta che "To, taffi gari, ki zona." Ta je, ta koma gidan sariki, tana zone. Shi ke nan, da tana zone, sai dan sariki iya neman ta da aure. Sai ta koma, ta gaya ma uwar, akaje, akadaura masu aure.

Suna nan, suna nan, sai sariki yana neman yariniya da aure. Shi ke nan, sai ya hada yaki, sai ya gaya wa yaro zashi yaki. Da zaya taffi, sai yariniya ta kissa masa yayan dabino a ka. Shi ke nan, sai suka taffi. Da suka taffi, rana ta yi tsaka, sai uban ya che "Chiroma," wai shi shiga rijiya shi debo ruwa aba dowaki. Sai ya che "To," sai ya shiga. Da ya shiga, ya debo ruwa, duk dokuna suka sha, suka koshi, shi ke nan, sai sariki ya che "To, ku rufe rijiya da kassa." Akarufe, shi ke nan, sai sariki ya taffi gida. Da ya taffi gida, sai ya yi kirran matar, ya che "To, ga shi, mijinki ya mutu." Sai ta che "To." Shi ke nan, sai ta ki chin abinchi, kaman kwana goma ba ta chi ba.

Sai yaro iya chikkin kozozobi, dabino a kainshi sai ya soma tsarowa, har ya fitto bakin rijiya, ya yi girima. Shi ke nan, sai yaro, sai ya dinga biyowa, iya hawa, dabino iya fittowa. Shi ke nan, sai ya fitto sama, iya chikkin dabino.

Sai baiwar matanshi yaro, sai tana fuchewa, tana karba madara chan wanni rugan Filani. Shi ke nan, sai ta ga mutum kaman Dodo. Sai ya che "Yariniya, zo manna." Sai yariniya ta ki zuwa, ta ki zuwa. Ya che "Zo manna." Sai ta che "To." Da ta zo, zobe na hanunshi, sai ya chiri, ya sa mata achikkin nono, sai ya che "To, en kin je, kadda kowa ya sauke ki sai matata." Sai yariniya ta che "To." Shi ke nan, da ta je, sai ta che "Zo ki sauke ni Yaya." Ta ki. Ta che "Ke, de, zo." Sai ta zo, ta sauke ta. Da ta sauke ta, sai ta che "Sa hanunki achikkin nono." Ta sa; sai ta samu zobe. Shi ke nan, sai ta che "Wa ya ba ki?" Ta che "Kin gani de." Sai ta gaya mata gunda ya ke.

Sai yariniya ta ja doki, ta yi kirran masu-kidda, ta yi kirran wanzami, suka taffi. Da ta je, akasa akayi mashi wanka. Da akayi mashi wanka, akasa akayi mashi aski. Shi ke nan, da akayi mashi aski, akasa mashi riga. Da akasa mashi riga, sai ta che "To mu taffi." Ya hau doki. Da ya hau doki, sai ya je ya tarada uban, anayi mashi fadanchi. Sai dan ya che "To Jema'a, mi kan yi da ma-kiye?" Sai suka yi shiru. Sai dan ya kara chewa "To Jema'a, mi kan yi da ma-kiye?" Sai suka yi shiru. Sai ya zare takobi, sai ya sare uban. Da ya sare uban, sai ya che "Alhamdulalahi, gari ya zamma nawa." Shi ke nan, sai yan-uwa suka yi mashi "Barka da arziki." Sai ya che "Um, hum." Sai ya zona gidansa kuma, ya chi sarautan gari.

---

## 56

### The Girl who married Dodo's Son.

Wanni mutum ke nan yana taffiya, ya zo wurin sarikin gari, ya che "Ga Arna na yaki, amma da ruwa a turaba, ba shi bar ku yi yaki ba." Ya che "To, bar ni en taffi." Ya tashi ya taffi har wurin kogi, ya che "Kogi, abinda ke chikkin ruwan nan na zo en roke su su ba ni turaba en taffi en yi yaki." Dagga chikkin ruwa suka che "Mi zaka ba mu kadan ka taffi yaki?" Ya che "Izan na taffi na yi yaki na komo, Allah ya ba ni nasara, na ba dan sarikin ruwa yana na chikkina aure." Suka che "To." Ruwa ya komo wannan woje ya ba shi turaba. Ya taffi, ya yi yaki, ya kama bayi dayawa a garin. Ya zo, ya ketare kuwa zashi gida, ruwa ya koma abinshi.

Sa'anan kuma, ya zona abinshi agida, yana da sayasuwa da bayi da ya kama, ba ya kara che da ruwa komi ba. Sa'anan kogi ya tashi, ruwa ya zo har kussa ga gari, anche "To, ga ruwa zaya chi gari." Sariki ya tashi, ya yi rusuna, ya che da kogi "Yi hankuri, yariniya ba ta yi girima, awota tukuna." Sa'anan ruwa ya koma.

Ya tashi ya shigga gida ya che "Uwar-gida." Ta che "Na'am." "Ba ki ba ni yanki em ba mutanen ruwa ba?" Ta che "A, a." Ya tashi ya taffi wurin daya kuma—ita madakin uwar gida che—ya che "Ki ba ni naki yan em ba mutanen ruwa." Ta che "Ni ba zam ba ka ba." Ya taffi wurin Kishiyansu, ya tambaya ta ita kuma ta ki ba shi. Sai ya tashi ya je wurin amariya, ya che "Ni ma, na zo wurinki,

du Allah ki ba ni naki." Ta che "To, da ni da yariniya duk nawanene? Ba naka ne ba? Kama ka ba su." Sariki ya sa anzo da yariniya, akazo da goro, akazo da kurdi, akadaura aure. Ya sa mutum goma ya che su taffi da yariniya kogi. Suka taffi da yariniya kogi, suka sa ta ta yi rusuna, suka che "To mutanen ruwa ga amariya mai-keyau mun kawo wurinku kuma." Suka tashi, suka komo abinsu suka barri yariniya nan, suka taffi. Akafitto dagga ruwa, akakama hanun yariniya, akashiga da ita chikkin ruwa. Akashiga da ita gida kuma, gidan Dodo sarikin ruwa, har yara suka saba, suna wasa da yariniya kuma.

To, matan sariki tana da goyo abayanta, goyo ta yi wayo, har ta yi girima. Suna fadda da ita su yayan sariki, suka che da yariniya "Muna fadda da ke don anjefa yanki a ruwa." Yariniya ta che da uwanta "Ashe, ina da yaruwa anjefe ta a ruwa?" Ta che "Kina da yaruwa manna." Ta che "To, Allah ya gamma mu da ita."

Yariniya ta taffi kasuwa, ta saye wanni abu da zasu zo su chi. Ta samu diyan duma, ta zo da shi wurinda anawanke idanu, ta tona kassa ta sa duma, ta che "To, Duma, ina so ki kai ni wurinda yaruwata ta ke." Sai duma ta chira, ta kama hainya, tana taffiya, ta fitta a garu, tana tofa, tana tofa, har ta taffi ruwa, ta shiga, ta taffi dakin yaruwan, ta hau daki, har ta yi da, danta kuma gora ne. Da safi yariniya ta che da uwanta "To, zan bi yana. Ta che "Kin san enda ta ke?" Ta che "Ni zam bi duman nan, ta kai ni." Da safi ta fitta, uwan ta che "To, ki taffi, na rasa baba na dangana, barri ke kankanuwa."

Yariniya tana bin duma, tana bin duma, tana bin duma, har ta zo bakin ruwa, ta che "Ashe, nan ne yana ta ke." Sai ta rufe idanu, sai ta fada a ruwa. Yariniya tana daki ta ji faduwa, sai ta fitta ta ga mutum, sai ta dauke ta, ta shiga daki da ita. Yariniya, hankali ya zo mata kuma, sa'anan ta che "Kin fitta enna?" Ta che "Na fitta gidan sariki." Ta che "Wane ubanki?" Ta che "Wanche ta haife ni." Ta che "To, ya, suna mini gori, suna che kin bata a ruwa, shi ne ya sa na zo en gan ki." To, suka rikka kuka su yaruwa.

Sa'anan miji ya fitta, yana zuwa, shi dan Dodo. Ta che da kanuwanta "Ki gudu, ki boya, kadda mijina ya gan ki." Yariniya ta tashi, ta shiga champe, ta boya, yaruwata ta rufe ta da zanne. Sai ya zo ya shiga daki. Ya che "Kai! Ina jin warin mutum a dakina." Ta che "Ba kowa. Ni ne." Ya che "A, a, da bako a daki." Sai ya tashi, ya bude zanne, ya dauke yariniya, ya che "Muna yin bakuwa ba ki nuna mani ba?

Kina boye mani ita?" Ta che "Um, kanuwana ne ta zo." Suna nan, suna zone kuma abinsu har suka kwana biyal. Suka saba da shi dan sarikin, suna wasansu kuma.

Ran nan da safi, ta che "Na tehhi, na je gida." Ta che "To, barri sai mai-gida ya komo en fada mashi, sa'anan kiya taffi gida." Ya komo, dan Dodo, ya che "Yariniya, gobe zaki gida?" Ta che "I, gobe zani kuma, kadda uwana ta yi kuka." Ya che "To, izan safi ya yi, ki dauke ta ki sa ta chikkin rafoniya ta dauke kwotashi biyu, ta fitto da su." To, ta dauke yariniya ta fitta da lefe guda biyu. Ta che "To, en kin taffi ki gaida gida kuma." Yaruwan sai ta fitta da ita ruwa tana raka ta hainyan gida. Ta che "En kin taffi, kin fitta dagga dauji chan, ga wanni biriji chan agabba, ki jefa lefe na hanun dama. Ki taffi chana kuwa adauji, ga wanni biriji kuma chan en kin taffi, ki passa na hanun hagun." To, ta taffi ita kuma, ta koma ruwa abinta.

Yariniya ta taffi, ta taffi birijin nan da ta nuna mata, ta passa kwotashi daya. Da shanu, da bayi, da doki, suka fitto dagga kwotashin nan, sai suka dauke ta suka dibiya ta bissa doki. Ta taffi chan kuma gabba wanchan birji kuma, ta passa wannan kwotashi na hagu. Rakuma, jakai, alfadaru da masu-kidda, da masu-kakaki, da masu-busa, duk sun fitta nan ba abinda ba ya fitta ba. Sai ta kama hainya kuma, zata gida. Ta aike mutum uku ta che "Kadda sariki ya gudu en ya ji motsi dayawa, ni ne ina zuwa da na taffi wurin yaruwana." Sako ya zo wurin sariki kuma. Sa'anan ta zo gida akatare ta. Ta sauko kuwa, ta taffi abinta gida.

To, sa'anan wota yariniya tana gida ta che "Ni ma, en taffi en ga yaruwana." Ita kuwa, ta yi shuka nata duman kuma wurin allola. Duma kuma ta yi tofa ta taffi kogi, ta shiga achikkin ruwa kuma, ta kama dakin yariniya ta hau. Yariniya ta fitta gida, ta che "Na samu gora kuma." Shi, dan Dodo, ya che "To rikke abinki." Ya che "To, zan gaya maki magana daya, randa wanni ya tambaya ki sunana, ki fadi, ba kiya kara ganin na ba."

To, yariniya ta zo wurin uwanta, ta che "Na kama hainya da safi gobe, na taffi gaida yaruwana." Akache "To." Ta kama hainya kuma da safi, ta taffi. Ta zo bakin ruwa, sai ta fada. Yariniya kuma ta fitta, ta dauke ta, ta che "Ke kuwa dagga ungwan ne kin fitto?" Ta che "Dagga gidan sariki." Ta dauke ta, ta shiga da ita gida, ta aje ta. Sa'anan dan sarikin ruwa ya tashi, yana zuwa daki. Ta che "Tashi ki boya." Ta che "A, a, kina boye ni donka dda en ga mijinki

ne." Sa'anan miji ya zo daki ya ga bakuwa azone, ya fitta woje ba yai magana da su ba.

Sa'anan yariniya ta che da safi zata gida. Yariniya ta che "To, barri sai mai-gidan ya zo, sa'anan ya sallame ki." Safi ya yi, ta zo ta che mashi "Yariniya zata gida." Ya che "To, ke ki dauke ta ki sa ta a rafoniyan nan, ta dauke kwotashi biyu kankani." Ta dauke yariniya ta sa ta rafoniya. Ta gaya mata. Ta che "Ga kwotashi mainya mainya kin che adauko kankani?" Sai ta dauka baba guda daya. Akafitta da ita dagga chikkin rafoniya, yariniya ta chikka gardama. Ya che "To, ki taffi da ita, ki sa ta a turaban gida." Ta taffi, ta sa ta hainya. Ta che "To, ga wanni biirji chan, en kin taffi ki jefa kwotashin nan." Ta kama hainya, ta taffi, ita kuma ta komo ruwa abinta. Yariniya ta passa kwotashi nan da nan, sai doki maras-kaffa, da jaki daya, da bawa guda daya duk makafi, da akwiya gurguwa. Ta kama hainya ta taffi gida ta ji fushi.

---

## 57

### The Man who married a Monkey.

Wanni mutum ya aure biri tamache. Ya che shina noma. Ya che ta taffi gwona. Sai ta che hakorinta suna yi mata chiwu. Sai ya che to, ta zona a gida. Sai da mijin ya taffi gwona, ta hau rumbu, ta diba dawa, ta zo, ta yi nika. Tana waka, ta che tana chiwun kirsa, ta che mijinta shina gwona, ita ba komi ba. Sai ta yi tuwo, ta chi, ta koshi, ta kwashe saura ta taffi ta boye. Miji da ya komo sai ta hau gado, sai tana kuka, wai hakori ya dame ta.

Sai wota mache ta zo, ta gaya wa mijin, ta che matanshi ba nakiriki ne ba. Sai ya che to, kaka zaya yi? Ya che sai ya kore ta. Sai ya kore ta. Da ya kore ta, sai ya zona goro.

---

## 58

### The Monkey-Woman.

Wanni mutum ke nan, ya auro wota bazawara. Ashe, tana rikidda biri. Shi kuma yana noman yalu. Da ya auro ta, sai ya che "Zan taffi daji yawon halbe, ga gwonan yalu ki duba, kadda birowi su zo su chi." Sai ta che "To."

Shi ke nan, da ya taffi, ita kuwa, ta taffi gwonan yalu, ta

tsaya tsakan gwona. Sai ta kwanche zannenta a gidan tururuwa, sai ta kwanta, tana birgima. Da ta birgima, sai wuchiyan biri ta fitto a gindinta, ta zamma biri sosai. Sai ta sa hanu a baki, ta kirra "Kai Biri, Kai Biri, Kai Biri." Sai biri kaman dari biyal suka fitto daji. Sai ta che ma birowi "To, ban da furefure, ban da kankana." Duk mainyan nan sun chainye, sun taffi. Ita kuwa, ta zamma mutum, ta koma gida.

Shi ke nan, da mahalbe ya komo, sai abokinshi ya che "Matanka tana rikidda biri." Sai ya che "To, ka fara ke nan, zaka kasshe min aure ne?" Sai ya che "Ban so ka da alheri na so ka da mugunta?" Sai ya che "Amma tunda ka yi gardama, gobe ka che ta nika maka gari, zaka tsari." Sai ya che "To," ya amsa.

Ta nika mashi gari. Da ta nika mashi gari, sai ya taffi, ya gara itache a bakin gwonan yalu, enda zaya zona. Ya sa tsani, ya hau, ya zona. Sai da yana zone, ya hange ta tana zuwa. Shi ke nan, tana zuwa mutum fa. Da ta zo tsakan gwona wurin gidan tururuwa—shi ko ina kallon ta de—sai ta kwanche zannenta, ta yas, sai ta fadi a gidan tururuwa, tana birgima. Shi ke nan, sai ya ga ta zamma biri, ta tashi. Sai ta sa hanu a baki, ta che "Kai Biri, Kai Biri, Kai Biri," sai ya ga birowi suna fittowa a bakin daji rat tat tat, rat tat tat. Suka chi yalu kop. Da suka taffi, sai ta komo mache, ta dauke zannenta, ta daura, ta taffi gida.

Sai ya sauko dagga tsari, ya bi ta. Sai ta che "A, Mai-Gida, sanu da zuwa." Sai ya che "Ba wanni 'sanu da zuwa,' sai ki kwashe kayanki ki fitta, ba na iya zamma da biri."

---

## 59

## The Despised Wife's Triumph.

Sarikin wanni gari ke nan, shina da mata fudu, yana son guda uku, daya ba ya son ta. Ya taffi, ya karba ma sauran maganin haifuwa. Suka zo zasu nika magani a duchi. Da sun nika magani, sun tashi, wadda ba ya son ta, ita ta zo da dawa a duchin, ta nika. Allah ya ba su chikki, su fudu, duk da ita. Sai sariki ya che kowa ta taffi gidanta ta haifu.

Waddanan sun fitta sun taffi gidajensu, ita kuwa zata. Sai ta che "Allah shi ba ni garinda zan haifu." Tana taffiya achikkin daji, tana taffiya achikkin daji, sai ta hange wanni

buka. Haderin ruwa kuwa ya taso, tana gudu buka na gudu, tana gudu buka na gudu, sai ta che "Allah, ba ka tsaye mani da bukan nan ba, na samu, em pakye ruwa ba?" Buka ya tsaya.

Ta zo garin shiga buka, sai ta iske gwoiwa baba kaman kwando, yana kwanche, kare yana kwanche kuma. Sa'anan gwoiwa ya che "Um," kare ya che "Wai ki shiga." Yariniya ta shiga, ruwa kuma ya sauko wurinda su ke zamne.

Sa'anan ruwa ya kare. Gwoiya ya che "Um," kare ya tambaya ta, ya che "Wai 'enna zaki?'" Ita ta che "Yanuwana sun taffi gidajen iyayensu zasu haifu, ni kuma, ba ni da dangi, zan neme garinda zan haifu." Gwoiwa ya che "Um," kare ya che "Wai, 'ke ba ki da iyaye ba?'" Ta chi "Ni, ba ni da su, ankai ni garin, ni kankani ne, ban san garina ba." Ya che "Um," kare ya che "Wai 'zaki zona inna tare da ni?'" Ta che "Mutum ya ki zamma enda mutane?" Ya che "Um," kare ya che "Wai, 'ki yi hakuri ki zona nan.'"

Har ta kwana goma, sa'anan chiwon chikki na haifuwa ya kama ta. Ya che "Um," kare ya che "Wai 'minene yana bata idanu?'" Ta che chikkinta ne yana mursawa. Ya che "Um," kare ya che "Wai, 'ki dauke, wannan rubutu a kwariya ki sha.'" Ta dauke, ta sha. Sa'anan ya che "Um," kare ya che "Wai 'ki fitta inna.'" Ta fitta, sai ta ga tana chikkin wanni daki kuma, sai ta ga kamacha, suka zo wurinta. Ta haife da namiji.

Sariki ya che da, wadda ta haife da namiji sai ya yanke mata sa a kofar gidan sariki ran komowa. Yariniya kuwa ta haifu da. Suka wanke dan. Sai de ta ga tuwo, ta chi, ba ta san enda yana fitto ba. Sai ta ga ruwa kuma achikkin tukuniya abayan daki, ta yi wanka.

Har kwana arabain. Ta tashi ta che da kare "Ka fada ma ubana gobe kishiyoyi zasu gida." Ya che "Um," kare ya che "Wai 'gobe kiya taffi.'" Safi ya yi, ya che "Um," kare ya che "Wai 'ki shiga nan.'" Sai ta shiga, ta ga gida da mutane pal, har uwanta da ta haife ta. Wannan ya kawo abu, wannan ya kawo abu, suka tara mata dukiya. Uwanta ta kawo rataya da lawaye na azurifa, da siliya achikki, ta sa shi chikkin kwotashi. Sa'anan suka kawo ta wurin gwoiwan nan. Tana rusuna, tana rusuna, ta che "Baba, zani gida kuma." Ya che "Um," kare ya che "Wai 'Albarka.'" Ya che "Um," kare ya che "Wai 'Lafiya.'" Tana kuka, tana kuka. Mutane suka yi mata rakiya kuma, har suka taffi da ita wurinda ta sani. Suka tsaya kuma, suka che "To, ki isa layfiya."

Sai ta je ta chi ma kishiyoyi a rafi, suna wanka, suka haifu mata duk uku. Ta shiga chikkin ruwa zata haye, uwar-gida ta che "Ba ki tsaya mu gani irin naki goiyon ba?" Ta che "A, a." Sai uwar-gida ta bi ta aguje, ta kwache goiyo. Da ta ga namiji ne sai ta goiya, ta sheka aguje, ta taffi, ta barri nata a rafi. Ita yariniya ta koma, ta dauke na uwar-gida. Ta taffi gida. Uwar-gida da ta issa gida sai ta che "Agaya wa sariki shi fitto shi yanke mani sa." Suka koma su waddanchan, suka shiga gida abinsu. Ita yariniya ta shiga gidanta shiru, ba ta che komi ba.

Har yaro ya yi wayo, ya fara fitta yana yawon daji. Har ran nan chiwo ya kama shi a daji, ya mutu. Sai yara suka komo, suka che "Mohammedu ya mutu a daji." Mutanen gari suka hau doki, duk suka je suka dauko shi. Sunka zo da shi gida. Za'ataffi arufe shi a kassa. Mallamai suka che "Gawan nan na magana ne, kadda arufe shi ba." Sa'anan akakirra matan gidan su fudu. Suka zo, mallamai suka che "Ku taffi gida, ku yi abinchi, ku zo da shi."

Suka taffi suka yi tuwo. Ita, uwar, ba ta da abin tuwo sai dusa, shi ne ta kwaba. Sunka dauko, sunka zo da shi wurin mallamai. Mallamai sunka che "Enna uwar-gida?" Suka cha mata "Zo ki dauke tuwonki." Ta che "To, izan ni na haife shi ya tashi." Ta zo ta che "Tashi ka chi tuwon nan." Ba ya tashi ba. Sa'anan ita daya kuma ta zo, ta che "Izan ni ne na haife ka ka tashi." Ba ya tashi ba. Daya kuma ta zo, ta che "Izan ni ne na haife ka ka tashi." Ba ya tashi ba. Sa'anan uwansa mai-haifiyansa ta zo da dusa—ba tuwo ne ba—ta che "Tashi ka chi dusan nan, don karifi akakwache mani kai a kogi." Sai ya tashi.

Sariki ya che adauke ta, ashiga da ita gidanshi don murna. Ta che "A, a, sai achiri mani kai na uwar-gida da su waddanchan duka biyu, a'yi mani murufu." Ya che "To."

Akachiri. Ta zona.

---

## 60

### The Good Kishiya and the Lucky Boy.

Wannan ne de da uwanshi, su biyu da kishiya, har yaro ya yi girima. Da ya yi girima, sai Yaruwanshi en sun hawo sai sun bi wota kofan gidan, suka che "Dan-uwa, en uwanka ba ta haushi, ta saya ma doki manna." Kullum su kan yi mashi,

sai kishiya ta che ma uwar "Ba kiya saya yaron nan doki ba?" Sai ita kuwa, uwan, sai ta che "Ke ba kiya saya mashi ba? Ai ni, ba ni da wuri." Sai ta che "Ai na saya mashi." Sai kishiyar uwar sai ta saya mashi doki da riguna.

Shi ke nan, kullum yan-uwan da zasu hau, shi kuwa ya hau, su kan taffi tare yawo. Shi ke nan, har yaro ya issa aure. Sai ta yi mashi aure, ita kishiya. Da ta yi mashi aure, sai ta che masa "Je ka inda zaka, koenna ka ga dama ka je." Shi ke nan, sai ya che "To."

Sai shi ke nan, sai sarikin gari ya kirra shi, sai ya che "Koenna zaka ne, da ka je garin nan da mu ke yin gaba da su, ka dauko min mashin sarikin garin." Sai ya che "To." Sai ya fitta.

Da ya tashi taffiya, da shi da matansa, sai gari da akeyi gaba da shi. Shi ke nan, sai suka gammu da yar sarikin garin. Ya che "Mu koma manna." Da suka je, ta kai su wurin sauka, daki mai-keyau. Shi ke nan, sai ya che "Ni ne, abu daya ni ke so agun ki. Ni de, ki kai ni en samu mashi." Sai ta che "Op, abin nan abin mai-sauke ne." Sai ta kai shi daki guda uku. Ga na takobi, ga na mashi, ga na kayan yaki. Sai ta che "To, ga dakin mashi, zabo wanda ka ke so." Shi ke nan, sai ya che "To," sai ya zabe na sarikin garin da su ke yaki da shi. Sai ya che "To, zamu taffi tare da ke?" Sai ta che "Um."

Shi ke nan, sai suka taffi, sai suka tarada kogi ya chikka. Sai shi ke nan, sai mata daya ta iya ruwa, yar sarikin kogi ta ke. Sai ta yi kuka, jirigi ya fitta. Sai suka dauke kaya, sai garinsu. Shi ke nan, sai yaro ya je ya kai wa sariki mashi. Sariki ya keta rabin gari, sai ya ba yaro, ya ba shi bayi, ya ba shi dokuna. Ya yi aure da yariniya na wanchan gari. Suka chi duniya, da shi da matanshi.

---

## 61

### The Determined Girl and the Wicked Parents.

Wannan de, yariniya che, sunanta Faddam. Shi ke nan, wanni miji yana son ta da aure, ita kuwa, tana son sa. Sai iyayen yariniya' ba suna son yaron, yanuwan iyayen kuma ba suna son yaron, sai suka ki. Shi ke nan, sai ta tara ruwan gari duk achikkin dan koko, ta hau sama. Gari kuwa, duk mutane babu ruwa da zasu sha. Sai shi ke nan, sai akazo, akatambaya

yariniya, akache aba su ruwa. Sai yariniya ta che "Wane na tambaya?" Sai akache "Uwanki." Sai ta che "A, a, ba ni ba ki ba."

Shi ke nan, sai ansoma mutuwa. Sai akadada zuwa wurin yariniya, akache "Aba mu ruwa mu sha, kadda gari duk ya mutu." Shi ke nan, sai ta che "En na ba ku ruwa ku sha, zaku ba ni Musa da aure?" Sai akache "I." Sai shi ke nan, sai ta sauko, sai ta bude dan koko, sai ruwa ya rufe gari.

Sai shi ke nan, sai akadaura aure. Shi ke nan, sai ta haifu da, namiji. Da ta haifu, sai yariniya ta bar dan a daki, sai iyaye suka zo, suka rufe dan, suka kashe. Da yariniya ta komo, sai ta gaya wa miji, sai ya che "To, muwa rama." Sai shi ke nan, sai ya sa akakirra iyayen su zo su kuka mutuwa. Mijin kuwa, sai ya haka rijiya, sai ya rufe bakinta da tabarima. Shi ke nan, sai da iyayen suka zo, sai ya sa su su zona akan tabarima, sai suka fada chikkin rijiya, suka mutu.

---

## 62

### The Wicked Girl and her Punishment.

Wota buduruwa ke nan, tana son saure, iyayenta suka che ba zasu ba ta ba. Kullum ya kan tashi ya taffi ya yi magana da su, su kan che "Ba zamu ba ka ba."

Sa'anan yariniya ta zo, ta che mashi "Na zo wurinka, ka ba ni wuka en taffi en yanka uwana, mu gudu mu taffi wanni gari mu yi aure." Ya che "A, a." Ta sake zuwa kuma, ta che "Ka ba ni wuka en taffi en yanka uwana." Ya che "A, a, domin na kadda ki yanke uwanki ba." Ya che "Taffi gidanki, ki zona." Ya che "Su wanda zasu ba iyayenki dukiya, su kuma, suwa ba ki." Sa'anan yariniya ta taffi gidansu; yaro ya taffi gida.

Akakwana biyal, yariniya ta sake tambaya, ta che "Ba ni wuka en yanka kubewa." Yaro ya manta, ya chiri wuka, ya ba ta. To, da karban wuka, sai ta taffi ta yanka uwanta. Ta che "To, ka gani, em ba mu gudu ba sai ayanka ni tare da kai, ga jini a wukanka na yanka uwana." Sai suka fitta, yaro ya rataye kwari, ya sa yariniya agabba, suna gudu.

Suna nan suna gudu zasu daji; suka kwana, suka gudu, suka issa tsakan daji, sai chiwun chikki ya kama yariniya, ya fiyada ita, ta mutu. Sa'anan ya zare kibiya daya, ya sa a bakka, yana tsaye, yana duben ta. Naman daji duk sun taru zasu chainye

ta, shi ba ya yarda ba, ya che ba mai-tabba namanta sai fa achi su tare.

Sa'anan mikiya ya zo, ya sauke gabban shi, yaro, ya che "Ba mu wuri mu chi nama." Ya che "A, a, ba mun yi alkawali da ita, em barri ku chi namanta ba?" Mikiya ya che "Mache, ba ayarda da ita ba, ba su da gaskiya." Yaro ya che "A, ni na yarda da wannan." Sai mikiya ya che "Kana da koko?" Ya che "Ina da shi." Ya che "Ba ni." Mikiya ya karba, ya tashi, ya taffi, ya komo da ruwa a koko, ya che mashi "Kana da wuka?" Ya che "I." Ya che "To, abude hakorinta." Mikiya ya chiri gashinsa na fikafiki, guda biyu, ya kada achikkin ruwa. Akabude bakinta, akazuba mata, yariniya sai ta tashi. Mikiya ya che "To, ka ga gashin nan, ka rikka, en ka taffi wanni gari ka samu abinda zaka chi, wata rana kuma ka rama mamu namammu."

Suka tashi suka shiga gari, suka samu gidan wota tsofuwa, suka shiga, suna nan suna zone har yamma ya yi. Suka kwana a garin. Da safi ya yi, sai suka ji kuka, ache "Uwan sariki ta mutu." Sai yaro ya tashi, ya che "Bar en taffi, en gani." Ya tashi, ya taffi wurinda akayi mutuwa. Ya zo, ya samu wanni, ya che "Ba ka yi mani magana da sariki ba?" Ya che "Sariki zuchiyansa ya bache, yanzu za'ayi magana da shi?" Sa'anan wanni ya che "Kai, ka sani abinda ya kawo shi? Taffi ka yi magana da shi manna." Sariki ya zo, ya che "Akirra shi yaro ya zo." Akakirra shi, ya zo. Ya che "Izan na yi uwanka rai kuwa ba ni mine?" Wanni ya che "Ka tabba gani wanni ya mutu ya komo?" Sariki ya che "Ku bar shi manna, ko shina da wanni dabara ne?" Ya che "Ina ba ka bawa goma," ya che ga gida kuma na ba ka, ga doki na ba ka." Ya che "To, adebo mani ruwa a koko." Akadebo, akakawo mashi. Ya kewoya bayan daki, ya kada gashin mikiya a ruwa, ya kawo. Ya che "To, abude bakin uwan sarikin nan." Da akazuba mata, sai ta tashi, ta zona. Akakawo dukiyanshi, akaba shi. Sa'anan kuma ya koma gida abinshi, ya yi zammanshi kuma a gari. Koenna kuma anyi mutuwa, sai azo akirraye shi ya ba su magani ya tashi.

Sa'anan bawan sariki yana neman yariniya da farika. Sa'anan ya che "Ainya Yariniya, tun da mun saba, maganin mijin ba kiya ba ni shi ba?" Ta che "To." Sa'anan ta kwanta, miji yana da magana tana kwanche shiru, yana da magana tana kwanche shiru. Mijinta ya che "Mine ya same ki?" Ta che "To, muna tare da kai, ka samu abu ba ka ba ni ajiya ba, sai kana aje a wurinka." Ya che "Shi kadai ya sa

kin kwanta shiru?" Ya che "To, ga shi, ki aje." Ya ba ta gashin mikiya. Da karba, sai ta daka tukuniya, ta che zata rafi. Sai ta taffi ta ba shi, bawan sariki. Ya karba, ya taffi da shi gidanshi.

Ran nan akayi mutuwa kuma, akakirra shi. Ya zo, ya che "Enna ajiyanda na ba ki?" Ta che "Yana nan, na aje nan." Suka duba—babu. Suka duba—babu. Sa'anan bawan sariki ya taffi, ya che "Izan na sa shi ya tashi mine kuwa ba ni?" Sariki ya che "To, abinda kana so duk sai em ba ka." Ya che "To." Ya sa shi wannan ya tashi. Da ya tashi, sai bawan sariki ya che akama mai-magani, aba shi ya zamma bawanshi. Sariki ya che "To, taffi ka kama." Ya taffi ya kama shi. Sa'anan matan kuma ta aure bawan sariki. Ya kama mai-magani, ya sa shi mari, ya kai shi daji, shina sheman daji.

Mikiya sai ta zo wurinsa. Ta che "Enna alkawalimmu?" Ya che "Na gaya maka mache ba ta ga gaskiya, ka che tana da gaskiya." Ya che "To, bar en kara maka wanni alheri kuma." Ya che "Da dare ka ja marinka har chiniya, ka taffi chikkin gari, ka samu mani kanwa." Ya taffi, ya samu kanwa, ya zo, ya aje kanwa har gari ya waye. Mikiya ta zo, ta che "To, abinda ya sa mu mu neme ki, ke, kanwa." Ya che "Muna so ki samu muna bera." Ta che "To." Nan da nan wurinda mutumen nan ya sare itache ta shiga wurin, ta samu bera. Ya che "Ke kanwa, da ke bera, kun sani warin gashina. Ku kama hainya ku taffi chikkin gari, ku shiga dakin bawan sarikin nan. Idan bera ta gani gashina, ke kanwa, ki daka, ki zo da shi."

Suka taffi chikkin gari, suka shiga gidan bawan sariki, suka shiga chikkin daki. Bera yana duba hakka, yana duba hakka achikkin tukane, achikkin kwore, ba ta gani ba. Ta taffi wurin kanwa awoje, ta che "Ga shi, ni ban gani ba." Sai kanwa ta che "Koma, ki taffi ki duba." Sa'anan kanwa ta shiga daki, ta yi kuka "Miyau." Suka che "Madallah, yanzu ta' a kasshe muna bera da tana hanna mamu barchi." Sai suka yi barchi, da bawan sariki da mata. Sa'anan bera ya zo, ya sansana bakin bawan, ya ji warin gashin. Ta che da magen "Ga shi, na gani." Ta che "Kin gani enna?" Ta che "A baki." Ta che "To, taffi ki chije shi." Ta zo, ta chije shi, ya yi "puf," gashi ya fadi. Mage ya daka, ya taffi, ya kai ma mai-magani a daji. To, da safi, mikiya ta zo, ta che "To, enna shi ke?" Ya che "Ga shi." Sa'anan ta che "To, bar en kara maka wanni." Sa'anan ta che "To, zani, wota rana ka'a biya mani namana."

Sa'anan akakwana, wanni dan sariki kuwa, chiwu ya kama shi, ya mutu. Sa'anan akazo, akakirra bawan sariki kuma, akache shi zo shi yi magani. Sai ya che magani ya bata. Sariki ya che "Ku kirra wanni ya zo," ya che "Ga doki, mazza ku taffi ku dauke wanda ya ke dajin nan, ku zo da shi." Akataffi mazza, akadauko shi, akazo da shi. Sariki ya che "To, mun kirraye ka, Allah ya sa maganinka ya komo maka." Ya che "Wanda shina dauji enna ya samu magani?" Sariki ya che "Du Allah ka taimake mu." Ya che "To, mi za'aba ni?" Sariki ya che "To iyakan wanda ya ke a gidan bawan nan duk na ba ka." Yaro ya yi magani, ya tashi wanchan mutuwa. Sariki ya che "To, ka taffi ka kama." Ya chiri marin nan ya sa ma bawa, ya dauke daya mari kuma ya sa ma matan. Ya taffi da su daji, wurinda shina saren itache, ya che su tara itache duk wuri daya. Sa'anan ya aike ma mikiya, ya che ta zo. Da ta zo, ya che "Taffi ki tara danginki duka, gobe mu gammu awurin sheman nan."

Da safi mikiya sun taru, tsuntsuwa duka sun zo; naman daji kuwa duk sun zo. Ya che "To, ku sa wuta awurinda antara nan." Suka sa wuta, ya chainye itache duk, ya barri garwashin wuta pal. Ya che da bawa da mata "Ku tashi ku fada a wutan nan." Suka gardama. Ya che samari su tashi, su dauke su, su jefe su a wutan nan. Suka dauke su, suka jefe su a wutan nan, har suka nuna. Ya sa samari suka ja su dagga chikkin wuta, sa'anan su aje su a sarari. Sa'anan ya che "Mikiya." Ta che "Um." Ya che "To, ga namanki." Shi kuma ya hau dokinsa, suka koma chikkin gari kuma.

Ashe mata ba su da gaskiya.

---

63

## The Two Half-Brothers and the Wicked Mother.

Wannan ne de, mata su biyu, daya da dukiya, daya ko babu. Suna nan, mijinsu kuma ya mutu. Da zaya mutu kuwa ya bar su da chikki. Ananan har mata suka haifu. Da suka haifu namazza, yayan kuwa kamansu daya, kaman yan tagwaye, ba wache ta rarabe da danta.

Shi ke nan, har yara har suka girima, sai uwar yaro, mai-dukiya, ta mutu, dukiya kuma ya zama na danta. Shi ke nan, sai wannan, kishiya, ta che mi zata yi ta kar wannan yaro ta samu dukiya.

Sai ta je gun mallami. Da ta je, sai ta che "Mallam, mi zan yi en kasshe daya yaro?" Sai ya che "Da zuwanki zaki che da yaro ki taffi daji da shi, en kun je, ki che ya hau sama. En ya hau sama ki kama shi ki kwakwali ido, ki taffo." Da ta taffo gida, sai ta che da yaro "Zo mu taffi daji." Sai suka taffi daji da yaro. Da suka je, sai ta che "To, hau sama." Sai yaro ya taka itache zaya hau, sai ta kama yaro, sai ta kwakwali idonshi. Sai ta taffo gida.

Sai daya yaro, dan-uwanshi, ya che "Enna dan-uwana ne?" Sai ta che "Op, ai na bar shi chan daji." Sai ya shiru. Sai ta yi wa danta abinchi, sai yaro ya ki chi. Da ya ki chi, sai ta che "Mi ya same ka?" Sai yaro ya ki magana. Sai shi ke nan, sai yaro ya taffi neman dan-uwanshi a daji. Shi ke nan, sai iya taffiya, iya kirra, iya taffiya, iya kirra, sai ya je, ya tarada dan-uwanshi achikkin rami. Sai ya dauke shi, ya yi kuka, ya fure masa kassa a ido, ya ba shi ruwa ya sha. Suna nan, sai Allah ya sauko ma yaro ido.

Shi ke nan, sai suka samu gari, suka chi sariki. Dagga nan sai wannan uwar ta ji labari yara sun samu dukiya. Shi ke nan, shi ta che "To." Sai ta taffi ta je gun yara, ta gaishe su, sun karba. Sai daya, danta, ya che "Mi kan yi da ma-kiye?" Sai fadawa suka che "Ai sai kissa." Sai dan ya dauke takobi, ya sare uwan.

---

64

## The Origin of the White-breasted Crow.

Wanni sariki kullum ya kan che da dan ba dansa ne ba. Dan kuma, ya yi kama da shi. Ya che "Akai shi bayan gari asare shi, sheggi ne." Yaron kuma, abokinsa dan Galadiman gari. Da mutanen gari sun taffi daji, sun yanka masa hanu, sun muna ma sariki, sun che sun kasshe shi.

Kuturta kuwa ta zo, ta samu yaro akwanche, ta che "Wane wannan kuma bil Adam?" Ta koma gida, ta deba ruwa ta kawo, ta yi mashi wankan hanunsa da anyanka, ta tsasi, ya koma kaman da. Ta sa shi agabba, sun je gida. Ya yi wayo, ya yi girima, ya isa gida, ta yi mashi gidan kansa, ya aure yar sarikin tururuwa. Ya samu fatake, ya sa su su taffi wurin ubanshi, ashe angaya masa "Ga shi, ya yi aure da yar sarikin tururua." Uban ya aike masa, ya che ba yar sarikin tururua ba, sai yar sarikin kurimi zaya yi aure da ita.

Ya yi ta kuka, ya yi ta kuka, sai kuturta ta zo wurinsa, ta tambaya shi, ta che "Mi ya same ka?" Ya che "Ubana ya che sai en aure yar sarikin kurimi." Ta che "Shi ke nan ya same ka kana kuka?" Ta diba kurdi, ta je kurimi zata daura aure. Akakawo mache daya. Ya aike ma ubansa, ya che "Ga shi ya aure yar sarikin kurimi kuwa." Sai ya che "Ba yar sarikin kurimi zaya aura, sai yar sarikin ruwa."

Sai yaro ya yi ta kuka, sai kuturta ta che "Dan-Gidan-Ubangijina, abinda ya yi maka chiwu duk ka gaya mani." Ya gaya mata. Ta je chikkin ruwa, ta samu sarikin ruwa, ta che "Ni bakuanka ne, na ji kana da yammata, ina son daya, ina da samari." Ya tara yayansa, ya che "Ki zabi wadda ta fi maki keyau." Ta zabi, sun ji gida tare, ta daura masu aure. Ya je, ya aike da ubansa kuwa, ya che ya aura. Sai uban ya che "Ba yar sarikin ruwa ba, sai yar sarikin samaniya."

Yaro ya yi ta kuka, ya dinga kuka, sai kuturta ta zo, ta che "Mi ya yi maka?" Ya che "Ubana ya che en aure yar sarikin samaniya." Ta che "Bissa nan wa zaya hau mani?" Muzuru ya che "Ki kama wuchiyana en haushe ki samaniya." Ta hau, ta same sarikin samaniya. Ta che "Na zo wurinka ne, ina da da, na ji labari kana da yammata na aure." Ya tara su, ya che "Ki zo ki zabi." Ashe sun yi hamsin. Ta dauke magajiyar gida. Sariki ya che "Kilga kurdinki, ki je da ita." Suka zo gida, akadaura masu aure, yaro ya aike da labari wurin ubansa. Ya che "Ba yar sarikin samaniya ba, sai yar sarikin Agaddaz."

Yaro ya yi ta kuka, sai kuturta ta tambaya shi, sai ta je wurin sarikin Agaddaz, ta che "Ina da da a gida, ka ba ni diyarka." Ya che "Ba na ba ki diyar ba sai na ga danki." Ta je ta kawo dan. Ya che "To, asa su dakin karifi sai sun kwana bakwai bakwai biyu, idan ba ya chi hatsi ba, shi ne mijinta." Suka shiga daki, anrufe masu kofa, ankuble. Kowanni dare uwar yaro ta kan kawo masa abinshi da ruwan sha, mache ba ta sani ba. Ta kan shiga hankali, ta tashe shi, da ya chi ya sha sai ta taffi da kwariya.

Sun yi rana kaman gobe zasu fitta, ta che "Na ji warin hatsi." Ya che "Enna zan samu? Goro ne." Da dare ya yi, ta che "Yau ni zan kwanta agabba kussa ga kofa." Kuturta ta shiga, ta tashe ta, ta tsamani danta ne. Ta tashi, ta buga hanunta chikkin miya, ta yarfe da hanu ajikkin bango, ba ta ga kuturta, ta che "Kana chin hatsi." Ya che "Enna zan samu achikkin wannan gari?" Shi ba ya sani kuturta ta tashe ta. Ta che "Gobe fa zaka mutu za'akasshe ka." Ya che "Sai akasshe ni kauwi, enna zan samu, Gimbiya?"

Suka yi barchi, kuturta ta komo woje daya, ta tashi danta ya chi abinchi. Ta je, ta koma gida, ta daka goro, ta zo da ruwansu tulli, ta komo ta kama hanun mache ta zubar ruwan goro, ta wanke hanun yaro. Ta bi jikkin bango wurinda yariniya ta yarfe miya ta zubar ruwan goro. Gari ya waye ambude gida, tana che "Ya chi hatsi, abude kofa." Da ambude daki, ansamu ruwan goro tulli a bango, ta gani, ta che ashe ba hatsi ba, goro ne, mijinta ke nan. Ya dauke ta, suka je gidansu kuwa. Sai ya aike da ubansa labari.

Da ya ji, ya zamma shiru, sai ya gaya arni, suka zo suka gewoya garin da. Da na chikkin daki ne, ya ga arni sun gewoya gari. Sai ya tashi, ya samu yar sarikin tururuwa, ya che "Ga ubana ya kawo mani yaki." Ta che "Sai ka je wurin yar sarikin kurimi ba?" Sai ya je wurin yar sarikin kurimi, ya che "Ga ubana ya kawo mani yaki, na rassa abinda zan yi." Ta che "Ba ka je wurin yar sarikin samaniya ba?" Ya taffi, ya durukussa, ya che "Mi zan yi yau kuma, ga ubana ya zo da yaki." Ta che "Ubanka ma haifenka?" Ya che "I." Ta che "Ka taffi wurin yar sarikin Agaddaz ko?" Ya je ya taffi, yar sarikin Agaddaz tana zone a kujera. Ya che "Gimbiya, ranki dadi," ya che "Ga ubana ya kawo mani yaki, ya gaya arna." Ta yarfe da zufa a goshinta, ta che "Ku chi su arna banza." Ya che "Banda ubana da dan galadiman gari."

Suka mutu duk mutanen nan, ya je ya kawo ubanshi da abokinsa, ya kawo riga da fula da rawani, ya gaida ubansa, ya bayar. Ya bada ma abokinsa kuwa, da riga da fula da komi. Ya je da ubansa awurin kofar fada, ya zare takobi, ya tambaya mutane, ya che "Idan mutum ya kan ki ka, akanyi mine da shi?" Akache "Sai akasshe shi." Ya dauke takobi ya sare kain uban, sai rawani ya fitta, ya naddi kainsa a wiyan kai. Ya tashi bissa kuma, ya zamma hankaka, yana che "Da! da! da!"

---

## 65

### The Brave Mother and the Cowardly Father.

Yaro shi daya uwansa ta haife shi. Lokachin nan sai ya komo, ya mutu. Sai uban yaro ya bi duniya ina ta neman magani. Sai wanni mallami ya kirro shi "Ya ka taffo, ga magani." Sai ya che "Je ka kasuwan bayin Filani da su ke daukawan itache, ka saye kaya dari."

Sai ya saye kayan itache dari, sai duk akazo, akatara su gu daya kaman adadan nan. Sai akazo, akasaka wuta. Sai wutan nan ya chi, ya fada, sai kuma gaushi ja wur ragas. Sai akache " Uban yaron nan ya tube, ya zo, ina fada wutan nan, dansa ina tashi." Sai uban yaro ya che shi zaya fada a wuta. Sai ya taffo aguje, ya ji zafi, sa ya kewoye. Sai ya che "Mallam, anakarawa so-biyu ne?" Sai mallami ya che " Anakarawa." Sai ya sake taffowa aguje, ya ji zafi, sai ya kewoye, sai ya gudu.

Lokachin nan sai uwansa, uwan yaro, sai ta yiwo fushi, sai ta che "Mallam, mache ta iya ne?" Sai mallam ya che "Ina yi." Sai uwan ta koma chan, sai ta rugo aguje. Da ta zo, ta tuma, sai fada a wutan nan fancham. Sai wutan nan, sai ya zamma gidan zinariya, shi kuma, uban yaro, akazamma da shi kurege. Dan kuma, ya tashi, ya yi rai. Sai akache " Wannan, ubanka akazamma da shi kurege." Sai akache " En ka kasshe shi, ka zamma da uwanka, en ko ba ka kasshe shi, uwanka ta mutu." Dan sai ya dauka kurege, ya mutu. Sai suka zamma da uwansa.

---

66

THE FIGHTING RAM.

Filani ke nan. Suka tashi suka manta da akwiya, tana da chikki. Sai ta kwanta gindin itache, sai ta haifu, ta haife da rago. Sai rago yana yawo, yana kiwo, ya taffi kaman Jagindi ya komo wurin uwanshi ya taffi kaman Kaffi ya komo wurin uwanshi, yana kiwo.

Sai gizzo ya zo, ya gani uwan. Sai ya taffi ya gaya ma sariki, ya che ya ga abu da ba akai a gidanshi ba, sai agidanshi, gizzo. Sai sariki ya che abinda ya kai gidanshi ya lalache. Sai gizzo ya che mashi asa shi da mutane, da mutum goma, ya taffi ya zo mashi da shi.

Suka taffi suka samu akwiya, iya, suka sa mata igiya. Sai tana kuka, ta che " Me," ta che " Me-e-e, Dan Zabarima, yaki zashi da ni, yakin masu-gari." Sai dan ya je chana, sai ya che " Na baushe bauna, na buge giwa, en girko da kafo." Sai da zuwanshi—gizzo ba ya tsaya ba, sai ya zo ya nuna masu, ya koma abinshi—sai dan ya zo ya kasshe mutane duka. Sai ya kama uwanshi, ya kai ta gindin itche chan.

Sai gizzo ya taffi, ya gaya ma sariki kuma, ya che waddanan

mutane ba karifi ne ba, ya che asa shi da masu-doki dari. Sai suka taffi, suka kama uwan, suka ja. Sai ta yi kuka, ta che "Me," ta che "Me-e-e, Dan Zabarima, yaki zashi da ni, yakin masu-gari, ya ka mazza, Dan Zabarima." Sai ragon ya je chana, sai ya che "Na passa mazza da kafo, na girko da kafo, na baushe bauna, na buge giwa." Sai ya zo wurin, sai ya kasshe masu-dokin nan duka.

Sai gizzo ya je, ya che ma sariki "Waddanan mutane ba karifi ba," wai sai asa shi da masu-doki metin kuma. Akasa shi da su, ya taffi, ya muna masu, sai ya komo. Da ya komo kuma, suka ja. Sai akwiya ta yi kuka, ta che "Me," ta che "Me-e-e, Dan Zabarima, yaki zashi da ni, Dan Zabarima, yakin masu-gari, ya ka mazza." Sai ragon ya je chana, sai ya che "Na kasshe masu-doki, na passa mazza da kafo, na girko da kafo, na baushe bauna, na buge giwa." Sai ya zo wurin. Da zuwanshi ya buge mutane duka, ya kasshe.

Sai gizzo ya taffi wurin sariki kuma, mutanen gari zasu kare kuma, sai wanni mutum ya che "Asaye kanwa guda uku," ya taffi kuma ya zo da ita. Sai ya che asa shi da mutum biyu. Sai akasa shi da su, sai ya taffi, ya sa ma ita, akwiya, igiya, shina ja. Yana ja, sai ta yi kuka, ta che "Me," ta che "Me-e-e, Dan Zabarima, yaki zashi da ni, Dan Zabarima, yakin masu-gari, ya ka mazza." Sai ragon ya je chana, ya che "Ni Mai-reru, ni Dan Zabarima, na kasshe masu-doki, na passa mazza da kafo, na girka da kafo, na baushe bauna, na buge giwa." Da zuwanshi wurin mutane—iskanshi shi ne shina kasshen mutane—sai da zuwanshi, mutumen nan ya taffi, ya dauke kanwa, ya jefa ma iska, sai iska ya daka ya kai ma rago, rago ya tsaya, yana chin kanwa. Sai kuma ya zo, sai mutumen nan ya dauke kanwa daya, ya jefa ma iska, sai iska ya daka ya kai ma rago, rago ya tsaya yana chin kanwa. Sai kuma ya zo, sai mutumen nan ya dauke kanwa daya, ya jefa ma iska, sai iska ya daka ya kai ma rago, rago ya tsaya yana chin kanwa. Sai suka ja uwan, suka zo da ita wurin sariki.

Da rago ya gamma chin kanwa, sai ya bi sawun uwanshi. Uwan, sai andaure ta a gidan sariki. Sai dan da zuwanshi sai ya passa katanga, sai ya shiga chikkin gida, sai akahalbe shi da kibiya. Sai ya mutu, akayanka duk da uwan.

Suka chi nama.

---

67

## The Lucky Foundling.

Ba-Auzene de, tun da ya ke ba ya tabba haifuwa, mutanen gari suna yi mashi gari. Sai ya che da mata tasa shi zashi taffo da danshi dagga wanni gari. Shi ke nan, sai mata ta che "Mu taffi manna." Sai ya che "To." Da suna taffiya, suka tarada yaro yana kwanche akan hanya, bakinsa ya chikka da kiyashi da kassa, komi ya kasshe shi oho! Shi ke nan, sai suka dauke shi, suka yi mashi wanka, suka fure kiyashi dagga baki. Shi ke nan, sai Ba-Auzene ya che "To, mu koma gida, abinda mu ke nema mun samu." Sai suka koma.

Da suka koma, ya che danshi ne, yan-uwan suka che ba nashi ba ne, ya sato dagga wanni gari ne. Sai ya che a,a, danshi ne. Sai suka che "To, en danka ne, mu hada rakuma kaman biyal biyal, mu ba yayammu, su je daji su kasshe." Sai akaba yara rakuma, suka taffi, suka kasshe, suka komo.

Shi ke nan, waddansu suna chewa dansa ne, waddanan suna chewa ba nashi ba ne. Shi ke nan, sai suka che "To, en danka ne mu hada dokuna kaman goma goma, su je su kasshe." Sai ya che "Op, wannan mai-sauke ne." Da suka ba yaransu goma goma, shi ya tashi ya ba dansa ashirin, ya hada masu kaya, ya che "En ka je, ka kasshe, ko surdi kadda ka dauko." Shi ke nan, sai yaro ya che "To." Sai ya hau kan wanni doki, shi yaron. Shi ke nan, da suka kakasshe, yan-uwansa suka dauke surduna, shi ba ya dauko ko daya, ya bar su.

Sai da suka koma, waddanan suna chewa danshi ne, waddansu suna chewa ba nashi ba ne. Suka che "En nashi ne, ga wata yariniya a gari chan, su je su nema." Ita kuwa, yariniya, ba mai-keyaunta duk duniya. En sarikai su zo sai ta ki su. To, sai ran nan, su yaran Auzenawa suka hada kayansu, kaman biyal suka taffi neman yariniya. Da yaro zaya taffi, sai ubanshi ya chikka masa aljifu da azurifa, wannan gu kuma, zinariya kuma ya zuba a baka, da azurufa. Shi ke nan, sai suka tashi, suka je gun yariniya.

Akayi, akayi, wannan ya yi ta zo, ta ki, wannan ya yi ta zo, ta ki, duk suka yi su biyal, ta ki. Saura wannan yaro. Shi ke nan, da yaro ya je, da ita ba ta magana, da yaro ya je sai ta yi dariya. Da ta yi dariya sai ya che "Alhamdu lilahi." Shi ke nan, sai ya zubar azurifa na bakinshi agabba. Ta che "Azurifa che, ba ko zinariya?" Sai ya bude aljifu, ya zubar mata. Sai ta rungume shi ta che shi ne mijinta.

Sai yaro ya koma gida, sai yan-uwan suka che "Ai, danshi

ne." Shi ke nan, sai ya gaya ma ubanshi, sai akakera masa gida. Shi ke nan, sai akadaura aure da yariniya. Sai yariniya ta tare a gidan yaro. Sai uban ya ba shi bawa ashirin, da dokuna, da rakuma, ita kuwa hakka.

---

## 68

### The Wicked Father and the Kind Stranger.

Wanni ke nan da danshi, matsiyachi, ba ya kama komi ba sai kurege. Anji labari kurege na faskara kamuwa, sai shi ya je ya kama. Shina nan, yana farauta da shi da danshi, sai suka zo, suka gina kurege. Sai kurege ya yi "burup," sai ya chere. Sai ya che "To, ni," en ji uban, "ni sarikin kaman kurege, to, ga shi, kurege ya chere, na ji kumiya." Sai ya buga danshi da guduma, sai ya fadi, jini yana fitta hanchi. Sai ya yi taffiyanshi, ya bar shi.

Sai wanni mai-dukiya ya zo, dukiyanshi ba shi da iyaka, sai ba shi da da. Sai ya zo, ya dauke shi, ya wanke shi da ruwan dami. Sai ya zamma da shi danshi. Ya kawo doki ya ba shi, ya hau, ya kawo riga ya ba shi, da wando. To, sai ya taffi da shi garinshi, sai ya che da sariki "Ga shi, na taffi taffiya, na samu da awurin taffiya." Sai sariki ya che kariyanshi, ba danshi ne ba. Ya che en danshi ne, su kwana goma anaba shi doki, da danshi da dan sariki, zasu yi sukuwa. Da sun yi sukuwa da dan sariki da dan mai-kurdi, sai su zware takobi, kowa shi kasshe dokinshi, har kwana goma. Doki goma goma ke nan. Ya che "To." Da suka yi hakkanan, sai sariki ya che "Ashe, danka ne." Sai sariki ya kawo yanshi na-chikkinshi, ya che "Aba shi, agamma su aure." Madakin gari shi kuma ya kawo yanshi na-chikkinshi, ya che "Aba shi, agamma su aure." Sai akazo akarufe masa kai da alkiba.

Dagga chan, ashe ubanda ya buge shi da guduma ya ji labarin dan, sai ya zo wurinshi. Sai ya zo da patan kurege agabba, da patan kurege abaya, sai ya zo ya sallama gidan mai-dukiyan nan, ya che mai-dukiya ya ba shi danshi. Ya che "Ni, ina rokon ka arziki, ga bawa goma, ga doki goma, sa goma, alfadari goma." Ya che "Duk na ba ka, amma danka danka ne ka rufa mani asiri, don na yi kariya wurin sariki, na che na samu da awurin taffiya. Ka kwashe kaya ka taffi da su gidanka. Kwanakinda danka yana son ganin ka ya zo, ba na kwache maka ne ba, ni

ko ba na saya ba ne." Sai shi ya che shi ba ya yarda ba, shi uban, mai-walkin kurege. Ya zo ya tona masa asiri.

Sai ya je da guduman nan awurin buki, ya zangare dan, ya che "Yar da alkiba ka chi kurege." Sai shi mai-kurdin nan ya kirra dan, ya kware takobi, ya ba dan ya rikke, ya che "To, ni yanzu na ji kumiya a garin nan, na che kai dana ne, ga shi ubanka ya zo ya che zashi da kai." Ya che "To, ni, ba ni so rai yanzu, ka dauke takobi, ka ko sare ni, ko ka sare ubanka." Sai dan ya sare ubanshi. Sai suka koma achikkin gari, da mai-kurdi da dan.

To, mu yi gardama da ni da kai, ko dan ya yi keyau ko ba ya yi keyau ba?

---

## 69

### The Woman who could not keep a Secret.

Wata kamacha ke nan tana nan ba ta da da ba. Sai wanni yaro ya zo, ya che shina son ta shi zona da ita, ta rikka che shi danta ne. Ya che kadda ta gaya sunanshi ba, sunanshi Mai-Duniya, randa ta fadi sunansa sai ba zata kara ganinshi.

En sun taffi sun hau doki, shi yaro shina sukuwa, sai sun che "Dan Kamacha." Sai wota tsofuwa ta taffi, ta tambaye ta, ta che "Sunan danki nan wane?" Sai ta che "Ba zan gaya maki sunanshi ba." Sai ta che du Allah ta gaya mata. Sai ta gaya mata, ta che "Sunanshi Mai-Duniya." Da zuwan dan, ya dauke doki da sukuwa, sai tsofuwa ta che "Mai-Duniya." Sai yaro ya komo da baya, ya zo, ya zage uwanshi, ya che Allah ba shi mata albarka. Sai yaro yana kuka, ya che sunanshi Mai-Duniya, ita zata mutu a toka. Sai ya che "Tatabarra wanni kambarra, sunana Mai-Duniya, na taffi, Allah ya gammu na, na taffi sai wota rana."

Sai yana waka, sai rairai wurinda yana tsaye nan ya kama dokinshi a gwiwa. Sai shina waka "Tatabarra wanni kambarra, sunana Mai-Duniya, na taffi, Allah ya gammu na, na taffi sai wota rana."

Sai shina waka, sai rairai ya kama doki, doki ya bata achikkin kassa. Sai yaron kuma, shina waka, sai ya che "Tatabarra wanni kambarra, sunana Mai-Duniya, na taffi, Allah ya gammu na, na taffi sai wota rana." Sai shi kuma ya bata.

Sai kamacha ta zona, ba ta da kowa, ta mutu a toka.

## 70

### The Boy who refused to Walk.

Wannan de, mache che, ba ta tabba haifuwa ba. Shi ke nan, sai ta che " Allah ba ka ba ni ko gurugu ko kuturu en haifu ba?" Sai shi ke nan, sai ran nan Allah ya sauko mata da chikki. Shi ke nan, ta haifu dan, sunansa Dan Kaddaffi.

Ananan, har yaro ya yi girima ya ki sauka. Shi ke nan, sai ta che "Mi zan yi da yaro ya sauka?" Sai ta taffi wurin mallami. Shi ke nan, da ta je, sai ta che "Mallam ba ka ba ni magani yaro ya sauko kassa ba?" Sai ya che "To, sai ki je ki sayo akwiya." Sai ta je ta sayo akwiya. Ya che "Ki taffi daukan daji," ya che "en kin je, ki yanka, en kin yanka, ki che 'Yaro ka sauka en je en yiwo ma itche en gassa ma nama.' Sai yaro ya sauka." Sai ta taffi daukan daji, ta yanke akwiya, sai ta che "Yaro ka sauko en je en yiwo ma itche." Sai ya sauko, da ya sauko sai mache sai ta gudu.

Shi ke nan, da ta gudu sai kura. Sai kura ta che "Yaro ka samu nama ne?" Sai ya che "I." Sai ya che "Amma namana na gwoiyo ne." Sai shi ke nan, sai ya che "en ba ki naman nan ki chainye, ki gwoiye ni?" Sai kura ta che "To, bawo." Sai kura ta chainye nama. Shi ke nan, da kura ta chainye nama, sai ta che "Yaro sauka, en je en yiwo bayan gida." Sai yaro ya che "Na ki, sai ki rama min namana da kika chi." Sai ta yi kaman zata chije shi, sai yaro ya koma wanni gu, ba ta iya ba. Sai shi ke nan, sai kura tana tare da yaro.

Har suka yi kwana kaman goma yaro iya bayan kura. Sai kura ta taffi gun mallami, sai ta che "Mallam ba ka ba ni magani yaro ya sauka ba?" Sai ya che "To, sai ki je ki sayo akwiya, ki taffi daji ki yanka, ki che 'Yaro sauko en taffi en yiwo ma itache.'" Sai kura ta che "To." Sai ta taffi daji, ta yanke akwiya. Sai ta che "Yaro sauko, en taffi en yiwo ma itache." Sai ya sauka. Da yaro ya sauko sai kura ta gudu. Da ta gudu kuma sai ta komo gun nama, ta hau itache. Shi ke nan sai ta yi maka ta, sai ta jawo nama, sai ta chainye. Yaro kuwa ba ya ganni ba. Shi ke nan, sai ta koma saukowa zata dauko sauran nama, sai yaro ya gani, sai ko ya fusgo kura. Sai kura ta subche dagga hanun yaro ta gudu.

Sai ananan, sai gizzo ya zo yawo. Sai ya ga yaro da nama. Sai ya che "Yaro, ba ka ba ni namanka ba?" Sai ya che "Namana na gwoiyo ne, en ka gwoiye ni ka chi." Sai gizzo ya

che "Op, don gwoiyo, ai gwoiyo ba wuya." Sai ya che "To, gwoiye ni tukuna ka chi." Shi ke nan, sai gizzo ya dauko yaro ya gwoiye shi. Da gizzo ya gwoiye shi, sai ya chainye nama. Da gizzo ya chainye nama, sai ya che "Yaro sauko," sai yaro ya ki. Sai shi ke nan, sai gizzo ya taffi da yaro a gidan koki. Sai ya che da koki "Dauko sandanki ki yi wa yaron nan duka." Sai shi ke nan, sai koki ta dauko sanda, sai ta zo zata duka yaro, sai yaro ya gwoche, sai ta samu gizzo. Sai da koki ta same shi, sai gizzo ya fadi, sai ya mutu. Sai koki sai ta gudu.

Sai yaro ya sauko dagga jikkin gizzo. Sai yaro ya je, ya fada a ruwa. Da ma, yaro dan ruwa ne. Ya koma gidanshi kuma.

---

## 71

### The Woman who bore a Clay Pot.

Wota mache ba ta da da, sai ta roke Allah, ta che "Ka ba ni chikki, ko na haife kasko." Allah ya ba ta chikki, har wata tara ta yi ta ko haife kasko baba. Ta dauka kuma, ta aje achikkin tukane.

Safi ya yi, uwan ta taffi dauji neman itache, shi ko, dan, shina achikkin kasko, ya fitta, ya taffi dauji, neman itache. Ya taffi, ya tarada enda naman daji suka yi shingi, sa'anan yana saran itachen. Barewa ta che "Kai, wa na saran itachen nan?" Ita, barewa, amba ta kumun gida sai sun komo, duk naman daji. Sa'anan yaro ya che "Bar en shigo ki gan ni." Sa'anan ya shiga, ya che mata "Ga ni, na zo." Ta che "Sunanka wane?" Ya che "Allah Keyauta." Sa'anan ya che mata "Ba kiya sa mani ruwa en sha ba?" Ta sa mashi ruwa ya sha. Ya che "Samu mani ruwa en shafa kai." Da amba shi, sai ya che "Tashi mu yi ta kukuwa." Suka yi kukuwa da ita, ya kada barewa, ya chiri gashin kainta, ya daure ta. Ya taffi ya sara itache, ya taffi gida, ya shiga kaskonshi.

Da yamma ya yi, naman daji suka komo, suka che "Barewa, mine kika yi akadaure ki?" Ta che "Wanni yaro ya zo, yana saren itache, na yi magana sai muka yi kukuwa, sai ya daure ni." Kura ta che "To, gobe ni zan zona en yi kumu."

Da safi ya yi, yaron ya komo, yana saren itache. Ta che "Kai wanene?" Ya che "Ni ne." Ya che "Kai wane?" Ta che "Shigo en gan ka." Yaro ya fitta fili, ya che "Ba ni ruwa en sha." Ta ba shi ruwa ya sha. Ya che "Samu mani ruwa

en shafa kai." Sai ya che "Tashi mu yi ta kukuwa." Sai kura ta che "Wannan yaro da renan wayo ya ke, ni da girima shi kankani kuwa." Sai ta zabura zata kama shi, sai ya dauke ta, ya fiyada ita a kassa, ya daure ta, ya bar ta, ya taffi kasko abinshi. Da yamma ya yi, suka zo, suka kwanche kura. Sun tambaya ta "Mi kika yi andaure ki?" Sai ta che "Wanni yaro ya zo, mun yi kukuwa da shi, ya fiyada ni a kassa, ya daure ni." Sai giwa ta che "To, gobe na zona, ni na yi kumu."

Sa'anan, safi ya yi kuma, yaron ya zo, ya sare itache kop, kop, kop, giwa ta che "Wanene?" Ya che "Ni ne." Sa'anan ya shiga, ya che da giwa "Sa ni ruwa en sha," sai ta sa. Ya che "Ba ni en shafa," ta ba shi. Ya che "Tashi mu yi ta kukuwa." Ya kashe giwa kuma, ya daure ta, ya taffi.

Da naman daji suka komo, suka che "Abin nan ya isa mu gudu tun da akadaure giwa." Tun da yamma suna daure kaya zasu gudu. Shi ko, yaro, ya bi dare, ya zo wurinsu, ya shiga chikkin tandan mai, ya kwanta. Safi ya yi, suka che "To, kowa ya dauke kayanshi, mu yi ta gudu, kadda shi zo shi same mu." Suka yi taffiyansu, suka shiga chikkin daukan daji chan da nisa.

Sa'anan kura ta ratse, ta che "Ku yi taffiya, na chi maku." Sa'anan ta bude tandu zata yi satan mai, sa yaro ya mare ta, ya che "Daka mu taffi." Sa'anan ta dauka aguje aguje, har ta tarada waddanan.

Sa'anan suka taffi, suka samu wurinda zasu gara, su zona. Sa'anan suka che "Kura, zo ki diba mamu mai." Ta che "A, a," tana jin tsoron yaro. Suka che "Du Allah zo ki ba mu." Ta che "A, a." Giwa ta yi fushi, ta kama tandun, ta bude, sai ko yaro ya ba ta mare pau, ya fitto. Da ya fitto, sai suku gudu, suka bar kayansu. Sai ya komo gari, ya gaya ma mutane, sunka zo, sunka kwashe kaya duka, sunka kai ma uwansa. Sa'anan ya fitto dagga chikkin kasko, ba ya kara zamma achikki ba. Kurumbus kan tadi.

---

72

## The Woman whose Offspring were a Mouse and a Cake.

Wanni mutum ne, matanshi biyu. Wata ta haife bera, wata ta haife dadowa. Dadowa, akasa shi a tukuniya, bera kuma, akasaka shi nashi wuri dabam a gangan keyauri.

Sai zuwa chan suka yi girima, akakai su kofar gida, akache su taffi dauji. Da suka taffi dauji, sai bera ta ga chiwo abissa,

ya che barri ya hau, dadowa ta rikka tara mashi a kassa. Bera ya che dadowa ta sha babakin, ta barri mashi jan. Sai dadowa duka ya shainye. Da bera ya sauka, sai ya che "Dadowa enna chiwona?" Sai ya che "Chiwonki ni na shainye." Sai bera ya che "Yanzu na yi fushi," wai zaya tsungule dadowa, ya chi. Sai dadowa ya che "Op, tsungule ni manna." Sai bera ya tsungule, ya chi, ya bar saura.

Sai suka tashi suka yi itache, sai bera ya che wa sauran dadowa "Sai mu taffi wurin igiya." Sai suka debe igiya, sai bera ya che "Bar en zo en kara sakye." Sai dadowa ya che "Kara sa manna." Sai bera ya chainye dadowa duk, ya kwashe itachen, ya gamma, ya daura, ya taffi ya jefa ma uwanshi.

Sai uwan dadowa ta tambaya shi enna danta ya ke. Sai ya che "Dadowa shina nan a kogi shina wanka." Har rana ya kare ba ta ga dadowa ba, sai uwan dadowa ta kama bera, ta kiriba achikkin turimi, ta gassa, ta sa a miya. Sai ta dauke sawun bera, ta sa ma uwan bera akan tuwonta. Da ta taffi ta chainye tuwo, sai ta zo ta tambaya uwan dadowa, ta che "Dana shina ungan ne?" Sai ta che "Minene kika chi a miya yanzu?" Sai suka kama kukuwa har kogi.

Gizzo kuwa shina nan, ya fura wutanshi. Da zuwan su da fadda, ya dauke wannan ya sa ta a wuta, ya dauke dayan kuma ya sa ta a wuta. Suka nuna, ya chi.

---

## 73

### How the Beautiful Girl escaped from Dodo.

Wannan de, duk duk gari ba mai-keyaunta wannan yariniya. Shi ke nan, sai iyayen ba su barrin ta tana fitta. To, duk ta fi yam-matan garin nan keyau. Shi ke nan, sai iyaye da zasu fitta sai su ke ba ta acha da kassa ta tsimi don kadda ta fitta.

Sai abokananta suka zo, suka che wai su taffi daji da yariniya. Shi ke nan, sai ta che "To." Sai da suka taffi chan daukan daji, suka che "Ai, ashiga rijiya, adebo ruwa." Shi ke nan, sai suka che da ita yariniya mai-keyau ta shiga, ta debo masu ruwa su sha. Rijiya kuwa na Dodo ne. Shi ke nan, sai ta che "To." Sai da ta shiga, duk ta debo masu ruwa, suka sha, shi ke nan, sai ta che "To, ku fitto da ni." Sai suka gudu.

Sai rana ya yi tsaka, sai Dodo ya zo zaya sha ruwa, sai ya sa guga achikkin rijiya. Shi ke nan, da ya sa, sai yariniya ta

rikka gugan Dodo. Da ta rikka, sai Dodo ya che "Kowanene achikkin rijiya ya sakke." Sai ita yariniya ta che "Bar en debo ma." Sai da ta debo, ya fitta da yariniya. Shi ke nan, sai da Dodo ya gan ta, sa ya che "Ga ruwana, ki dauka, ki kai mani gidana, kadda ya zuba." Shi ke nan, sai ta dauka, sai suka je gidan Dodo.

Sai Dodo ya che "Da en chainye ki da en aure ki wanni ki ke so?" Sai ta che "To, aure ni manna." Shi ke nan, sai ya aure ta. Sai en ya taffi daji, ya kasso nashi mutum, ya kasso nata naman daji. Sai ya tari mutane a hainya, ya kasshe, ya debo mata dukiya.

Shi ke nan, har yariniya ta yi chikki. Shi ke nan, sai yariniya ta haifu, rabi Dodo rabi mutum. Shi ke nan, har da ta haifu hakka. Sai ran nan, sai Dodo ya taffi daji, sai Dodo ya daure danshi kararawa a wiya. Da ya daura mashi, sai ita matar ta daka fura, sai ta dankare achikkin kararawa don kadda ta kara. Sai shi ke nan, sai ta tatara kaya ta gudu, sai ta taffi gidansu. Sai ta je ta kasshe dan. Shi ke nan, sai da ta kasshe dan sai ta barnatada dukiya.

---

## 74

### The Precocious New Baby settles his Father's Debts.

Wanni mutum ya taffi ya chi bashi, matansa da chikki. Kwana uku matan ta haifu. Da ta haifu, akadauke da, akasa shi a gado. Sa'anan shi wanda ubansa ya chi bashi awurinsa ya zo tambaya dukianshi. Da ya sallama, ba kowa a gida, yaro dankankani da akahaifu ya amsa, ya che "Mu taffi, ubana ba shi nan. Mu teffi, wurin shari'a, ni na karba bashi wurin wanni zam ba ka." Sa'anan ya dauke yaro a wiya, ya che "To, mu teffi wurin masu-mainyan baki su yi muna shari'a." Yaro da ya zo wurin korofi ya zona. Ya che "Tashi mu teffi." Yaro ya che "Ka che mu teffi wurin masu-mainyan baki, da bakinda ya fi wannan girima?"

Ya che "To, mu tashi mu taffi wurin masu-jan ido." Sa'anda yaro ya zo wurin barkono, ya zona. Ya che "Tashi mu teffi." Ya che "A, a, ka che a wurin masu-jan ido, da idonda ya fi barkono ja?"

Ya che da yaron "Tashi mu je wurin masu-mainyan kune." Da sun zo wurin gwaza, yaro ya zona. Ya che "Tashi." Ya che "A, a, akwai kunenda ya fi gainyen gwaza girima?"

Ya che "Mu taffi wurin masu-gari su yi mumu shari'a." Suka zo wurin sariki, ya che "Da na samu ma-yi mani aski, da na yi maku shari'a." Yaro ya che "Debo ruwa en yi maka." Da andebo ruwa, yaro yana da gero guda biyal, ya che "Ga gero atume mani."

Da ya karba aska, ya yi ma sariki aski. Sa'anan sariki ya che "Yaro." Ya che "I." Ya che "Amayar mani da gashi en yi maku shari'a." Shi, yaron, ya che "To, amayar mani da gero da antume, sa'anan en mayar maka da gashinka." Sa'anan sariki ya che "Kai, yaron nan, ba ni ba zan iya yin shari'ansa ba." Ya che "Kai, mai-bashi, akoma da shi gidan ubanshi, kadda akara tambaya bashi wurinshi." Sa'anan ya che "To, yaro, mu koma gida, ba na iya yin shari'a da kai."

Sa'anan suka koma, ya che da uban "Na barri maka dukiyanka saboda danka."

---

## 75

### Dodo's Debt.

Mata sun taffi rafi, su biyu, garin diban ruwa, daya tana da chikki. Da sunka diba ruwa, mai-chikki ta shiga garim bayi, maras-chikki ta zubar da yashi achikkin ruwanta. Sa'anan ta dauke nakanta, ta taffi gida. Mai-chikki ta komo, ba kowa.

Sai Dodo ya fitto dagga ruwa. Mai-chikki ta che "Ba kowa nan, kai zaka dauke ni." Dodo ya zo, ya dauke ta, ya che da ita "Abinda ke chikkin nan, idan namiji abokina ne, idan mache matana ne." Ta yarda.

Ta taffi gida, ta yi kwana uku ta haifu. Sai kishiyanta ta taffi wurin Dodo, ta gaya masa "Mata da ka dauke ta ta haifu." Ya che "Wanni iri ne?" Ta che "Mache ne." Ya che "To."

Har ta yi girima, har randa za'ayi aurenta, ba afadi ma Dodo ba. Sai ita kishiya ta yi gudu, ta taffi wurin Dodo, ta che "Za'adauke yarinya yau."

Dodo ya kama hainya, ya zo, biki ya taru dayawa. Sa'anan Dodo ya zo, ya che "Ga Kadindi ya zo." Ita yariniya kuwa, tana nan zone, ta che "Baba, Inna," suka amsa "Um." Ta che "Ga Dodo ya zo garim bim bashinshi." Uban ya che "Dokin nan na wanene?" Ta che "Nawa ne." Ya che "Kama, ki ba Dodo abakin bashi." Ta ba shi, Dodo ya karba, ya hadiye.

Ta che " Ga Kadindi ya zo garim bashi." Yariniya ta che " Ka ji Baba, kin ji Inna ? " Ubanta ya che " Shanun nan ba naki ba ? Ki ba shi ya chi." Sai ta ba shi, ya hadiye.

Ya che " Ga Kadindi ya zo." Sai uban ya che " Kama tarun nan duka." Ta ba shi. Ya sake yin magana, ya che ya zo bim bashi. " Tukuwanenki na tuwo aba shi," en ji uban. Ta ba shi, ba ya isa ba, ta kama ubanta ta ba shi. Dodo ya che " Ga Kadindi ya zaka." Ta che " Allah, ka ji, Dodo ya zo bim bashi." Ashe akajefa mata wuka dagga bissa, ta ba Dodo. Da ya sa bakinsa zaya hadiye, wuka ta yanke bakinshi har chikki. Dodo ya mutu.

Mutane sun fitta duk kuma, da shanu, da dowaki, da biki, da uban, duk sun fitta. Sai akarufe yariniya kuma, akakai ta wurin miji.

---

## 76

### How the Eagle outwitted the Townspeople.

Wanni mutum na gidan sariki shanunsa bakwai. Ya zo ya che da mutane " Ga shanu, wanni ya saye, randa uwar sariki ta mutu arufe su tare, duk da uwar da wanda ya chi sa." Wanni ya yarda, ya che " Ba ni shanu, randa uwar sariki ta mutu ran nan ataffi da ni."

To, ya karbe shanu. Da safi ya yanka daya, ya dibi nama, ya hau bissa itache, ya taffi ya aje ma yayan mikiya su chi. Mutane sun ki chi nama, sun che " Na mutuwa ne," ba suwa chi ba. To, ya chainye wannan sa ya kare, ya sakye yankan daya, ya dibi nama kuma, ya kai ma yayan mikiya abissa. Mikiya ta komo, ta che " Wanda ya kawo nama yana so ya kasshe min yayana ne."

To, sa'anan ya sakye yankan sa kuma, ya sakye daukan nama ya kai ma mikiya kuma. Mikiya ta che " To, kana kawo naman nan na mine ? " Ya che " Na karba shanu guda bakwai, anche randa uwar sariki ta mutu arufe mu tare da ni da ita. To, na rassa mai-taye mani chi, shi ne ya sa ina taya maki kiwon yayanki." Ta che " To, taffi gida, randa ta mutu ka zo ka gaya mani." Ya taffi gida.

To, ya taffi gida kuma, da safi uwar sariki ta mutu. Ya taffi wurin mikiya, ya che " Ta mutu." Mikiya ta che " To, taffi, izan suka gamma hakan rami zasu sa uwan sariki, sun kirraye ka, ka che ' To, ku barri tukuna manna, en zo.' Sa'anan ka debe ruwa a kasko, ka wanke ido, ka wanke kaffa, sa'anan ka

tashi tsaye, ka sa fuskanka gabas, ka kirra Allah so-uku." Ta che "To, Allah zaya yi magani. Sa'anan ka che 'Allah zan mutu, ba da saninka ba.'"

Suka haka rami, suka kirra mutumen nan, sai ya tashi, ya che "Allah huwa Allah," ya sakye chewa "Allah huwa Allah," har so-uku. Mikiya ta amsa chan abissa, ta che "O." Ya che "Zan mutu ba da saninka ba." Mikiya ta che "Bayan ka mutu barri ruwa, barri hatsi, ko fisari ba suwa samu su sha." Da mutane suka ji, sai suka che "Allah ne ya amsa." Sai suka che "Taffi abinka, mu gari duk muwa mutu don mutum daya?" Suka che "Taffi abinka."

---

## 77

### The Spider passes on a Debt.

Wota mache tana da yanta. Da za'adaure yariniya aure, ta che ba ta samu daru ba, ba ta samu tasa ba. Sai uwar tana da sa, ta taffi da shi wurin masu-hanta, wai su saye, wai daru goma tasa goma, wai biyan sa ke nan. Suka che su ba zasu iya ba.

Sai gizzo ya ji, ya zo, ya che shi zaya saye sa, en de aure ya tashi shi ya kawo tasa goma da daru goma. Sai mache ta bar ma gizzo sa, ya zo gidansa, ya yanka.

Sai da ya daffa, ya dauke romo achikkin tukuniya, ya zo, ya aje a turaba. Shi ya hau itache ya boya sai bunsuru kishin ruwa ya kama shi. Sai ya zo, ya sa baki a tukuniya, sai tukuniyan romo ya kama shi a baki. Sai gizzo ya shirko, ya che "To, gizzo mai-sayen san tsofuwa daru goma tasa goma, biya akan ka, Bunsuru." Sai bunsuru ya che "To, na yarda."

Sai ya taffi za ya sha ruwa a rafi, sai kaguwa ta kama bakin bunsuru. Bunsuru ya che "Bunsuru ma-tanden romon gizzo, gizzo mai-sayen san tsofuwa daru goma tasa goma, biya akan ki, Kaguwa." Sai kaguwa ta che "To, na yarda."

Sai ga zuwan yariniya a rafi, ta taka kaguwa. Sai ya che "Yariniya ma-takar kaguwa, kaguwa ma-kaman gemun bunsuru, bunsurn, ma-tanden romon gizzo, gizzo mai-sayen san tsofuwa daru goma tasa goma, biya akan, ki Yariniya." Sai yariniya ta che "To, na yarda."

Sai yariniya ta dauke ruwa, sai tsuntsi ya kashe ta. Sai ta che "Tsuntsi ma-kadar yariniya, yariniya ma-takar kaguwa,

kaguwa ma-kaman gemun bunsuru, bunsuru ma-tanden romon gizzo, gizzo mai-sayen san tsofuwa daru goma, tasa goma, biya akan, ka Tsuntsi." Sai tsuntsi ya che "To, na yarda."

Sai tsuntsi yana nan, gara ya zo ya yi gini akan tsuntsi. Sai tsuntsi ya che "To, gara mai-ginin tsuntsi, tsuntsi ma-kadar yariniya, yariniya ma-takar kaguwa, kaguwa ma-kaman gemun bunsuru, bunsuru, ma-tanden romon gizzo, gizzo mai-sayen san tsofuwa daru goma tasa goma, biya akan ki Gara." Sai gara ya che "To, Na yarda."

Sai wanni tsuntsu ya zo, ya sauka a gara, ya yi gini abissa gara. Sai gara ya che "To, tsuntsu mai-sheka akan gara, gara mai-ginin tsuntsi, tsuntsi ma-kadar yariniya, yariniya ma-takar kaguwa, kaguwa ma-kaman gemun bunsuru, bunsuru, ma-tanden romon gizzo, gizzo mai-sayen san tsofuwa daru goma tasa goma, biya akan ka, Tsuntsu." Sai tsuntsu ya che "To, Na yarda."

Sai tsuntsu shina nan, shina zone, shina nan, shina zone, sai wota rana wanni yaro ya zo shina halbe. Sai ya ga wannan tsuntsu akan gara, sai ya halbe shi. Sai tsuntsu ya che "Yaro ma-halben tsuntsu, tsuntsu mai-sheka akan gara, gara mai-ginin tsuntsi, tsuntsi ma-kadar yariniya, yariniya ma-takar kaguwa, kaguwa ma-kaman gemun bunsuru, bunsuru ma-tanden romon gizzo, gizzo mai-sayen san tsofuwa daru goma tasa goma, biya akan ka, Yaro." Sai yaro ya che "To, na yarda."

Sai ya taffi gida. Da ya bude baki zava gaya ma uwanshi, sai uwan ta rufe shi da duka. Sai yaro ya che "To, uwar mai-dukan yaro, yaro ma-halben tsuntsu, tsuntsu mai-sheka akan gara, gara mai-ginin tsuntsi, tsuntsi ma-kadar yariniya, yariniya ma-takar kaguwa, kaguwa ma-kaman gemun bunsuru, bansuru, ma-tanden romon gizzo, gizzo mai-sayen san tsofuwa daru goma tasa goma, biya akan ki Uwa." Sai uwar ta che "To, na yarda."

Sai wanni makeri ya kone zannen uwar, sai uwar ta che "To, makeri ma-konan zannen uwar, uwar mai-dukan yaro, yaro ma-halben tsuntsu, tsuntsu mai-sheka akan gara, gara mai-ginin tsuntsi, tsuntsi ma-kadar yariniya, yariniya ma-takar kaguwa, kaguwa ma-kaman gemun bunsuru, bunsuru ma-tanden romon gizzo, gizzo mai-sayen san tsofuwa daru goma tasa goma, biya akan ka Makeri." Sai makeri ya che "To, na yarda."

Makera suka tashi, suka kera tasa goma daru goma, suka kai ma matan. Mata ta karba ta ba yaro. Yaro ya karba ya ba tsuntsu. Tsuntsu ya karba ya ba gara. Gara ta karba ta ba tsuntsi. Tsuntsi ya karba ya ba yariniya. Yariniya ta karba

ta ba kaguwa. Kaguwa ta karba ta ba bunsuru. Bunsuru ya karba ya ba gizzo. Gizzo ya karba ya ba tsofuwa.

Shi ke nan ya kare, rikichin gizzo ke nan. Shi ya chi naman sa, ya sa waddansu su nema mashi biya, shi ba ya yi komi ba.

---

78

## The Spider Pays his Debts.

Gizzo ne, ya karba bashi dayawa, awurin naman daji duk ya karbe. Sai ya yi dabara abinda zaya yi, ba shi da kurdinda zaya biya ba. Sai ya che to, ran aljimuwa su zo su samu bashinsu.

Da ran aljimuwa ya yi, da sasafi, sai kaza ta zo, tana bim bashi. Da ta zo, sai gizzo ya che "To, zam biya yanzu yanzu, amma sai ki zona kadan, ina yi maki abinchi." Sai tana zone achikkin daki, sai muzuru ya zo. Sai gizzo ya che "To, ga biya tana daki, taffi ka kama." Sai muzuru ya taffi ya shiga daki, ya kama kaza, ya murde wiyanta.

Sai da zaya taffi sai kare ya zo. Sai gizzo ya che "To, ga biya tana daki, taffi ka kama." Sai kare ya taffi ya kama muzuru, ya morde shi, ya kasshe. Sai da zaya taffi, sai kura ta zo. Sai gizzo ya che "To, ga biya tana daki, taffi ki kama." Sai kura ta yi gudu ta kama kare, ta chainye. Sai da zata taffi, sai ga damisa ta zo. Sai gizzo ya che "To, ga biya tana daki, taffi ki kama." Sai damisa ta damfaro kan kura, ta kasshe. Da zata taffi, sai ga zaki ya zo, ya tarada damisa.

Sai suka yi ta fadda, suka yi ta fadda, suna fadda, sai gizzo ya dauke barkono ya zuba a idanunsu. Da ya zuba sai ya dauko baban sanda, ya yi ta dukan su, yana dukan su har ya kasshe su duka biyu. Sai gizzo ya tara nama a gidanshi kuma, ya che ya biya bashi ke nan.

---

79

## The Youngest Son and the Wise Ewe.

Wanni yana da dukiya. Achikkin dukiyansa akwai wanni tsofuwan tunkiya. Yaranshi kuma uku, biyu yana so, daya ba ya so. Da zaya kwanta mutuwa, ya kirra baban dan, ya che

"Ko na mutu, kadda ka che kana son wanni dukiya sai tsofuwan tinkiyan nan." Sai ya che "Kai, ga dukiya maiyawa, mi zan yi da tsofuwan timkiya?" Sai ya che "To." Sai ya kirra ma-bi-maki, wanda yana bin baba, ya che "En na mutu, kadda ka che kana son komi, sai ka kama tsofuwan tinkiyan nan." Sai ya che "Ina ganin dukiya maiyawa, mi zan yi da tsofuwan tinkiya?" Sai ya che "To." Sai ya kirra Auta, wanda ba ya so, sai ya che ma Auta "To, ka gani, ko na mutu, kadda ka che kana son komi sai tsofuwan tinkiyan nan." Sai ya che "Baba, tun kana da rai dukiyanka ba ya ampana mani komi ba, barri ka mutu." Sai ya che "Tinkiya ta ishe ni." Sai ya che "To, amma komi zaka chi sai ka ba tinkiya ta fara chi, sa'anan ka chi." Sai ya che "To."

Da ya gamma mashi magana, da ya shiga daka, da ya mutu. Sai kuma ana ta kuka, ana ta kuka, ana ta kuka. Sai Auta ya kama tinkiya, ya fitta dagga gida. Sai mutane suka che "Op, wannan da anyi mashi baki. Ga dukiya maiyawa, duk ya barri, sai ya kama tsofuwan tinkiya."

Sai yana taffiya da tinkiya, yana taffiya da tinkiya, sai da ya dibo ruwa ya ba ta, ta sha, sa'anan shi ya sha. Sai suka je suka sauka a gidan wanni masaki, matsiyache, ba su da abinda zasu chi. Da ya sallama, sai masaki ya che "Ai, Bako, zaka sauka nan?" Sai ya che "I." Ya che "To, ni ba ni da abinda zani chi, barri em ba ka." To, shi, masaki, shina da matan-sonshi, uwar-gida, ita kuma, uwar-gida, tana da yanta, mache. Ita kuwa, kishiya da ba ya so, ita kuma tana da yar-mache. Sai masaki ya che da matan-sonshi "Uwar-Gida, debo ma bakon nan ruwa ya sha." Sai ta che "Kai, ba ni da ruwa a daki, ba ni da komi da za'aba bako." Sai ya che da matanda ba ya so "Ke, ki debo ma bako ruwa ya sha." Sai mata da ba aso da dan dawa a dakinta, tafi daya, sai ta nika, ta sa achikkin ruwa, sai akakai mashi. Sai ya ba tinkiya. Sai akache "Op, sha manna, za'aba tinkiya nata dabam." Sai ya che "A, a, wannan ya ishe mu duka." Sai ya ba tinkiya ta sha, shi kuma ya sha.

Sai dare ya yi, rana ya fadi, sai matansa ta che "Op, bakon nan zaya kara kwana a gidan nan ne?" Sai ya che "I." Sai masaki ya che mata "Kina da sauran dawa da za'ayi kunu aba bako?" Sai ta che "Ni, sauran dawa tafi daya zan yi kunu zan ba yariniya, ba ni ba bako ba." Sai ya che ma matanda ba ya so "Akwai dan dawa asa ayi kunu, aba bako?" Ta che "Sauran dawa tafi daya ne, amma na yi em ba shi hakkanan." Sai ta yi kunu na tafi daya, ta kawo ma bako. Da ya dauke

kunu, ya ba tinkiya ta sha, shi kuma ya sha. To, sai gari ya waye kuma.

To, ran nan tinkiya zata yi magana da shi. Sai ta che "Tashi mu taffi, ka raka ni bakin daji." Sai suka tashi. Sai mai-gida ya che "Kun tashi ke nan?" Sai ya che "A, a, en je bakin daji zamu komo." Da suka taffi bakin daji, tinkiya ta che "Tsaya nan." Sai ta je ta zaga chikkin chiyawa, ta komo wurin yaro, ta che "Je ka, inda ka ga na fitto ka bi." Da ya taffi, sai ya iske doki metin da sirdinsu da linzaminsu da kayan doki na saurauta duk. Sai ya komo ya che "Na iske doki metin, da sirdinsu da linzaminsu da kayan doki na saurauta duk." Sai ta che "To, tsaya nan." Sai ta zaga chiyawa, ta zaga chiyawa. Da ta komo, sai ta che "To, je ka, inda ka ga na fitto ka bi." Sai ya taffi, ya iske zagi metin, kowanni da bargo a wiya. Da ya komo ya gaya mata. Sai ta che "To, je ka, kowanni ya kama doki dede." Da suka kama, sai ta che "To, mu koma gidanda muka sauka."

Da suka zo, masaki ya duba doki suka kewoya bayan gida, sai ya che "Op, wanni bako ba ya tashi ba, masu-dowaki sun zo." Sai ya duba, sai ya ga tinkiya nan agaba. Sai tinkiya ta che "Ai, mu ne, ba mun tashi ba." Sai tinkiya ta che "To, duk dowakin nan akai gidan mata da ba aso."

Da akaaje dowaki, sai ta che "Zo mu koma bakin daji." Da ta je bakin daji, sai ta tsaya, ta che "Duba gaba da mu." Sai ya duba, ya ga bayi da kwangi kaman dari uku, kowanni yana da kayan dami. Sai kuma ta che "To, mu koma gidanda muka sauka." Sai ta che "To, duka bayi da kwangi da damunan nan," ta che "duk akai dakin mata da ba aso."

Da akakai, sai matan-so ta che sai Auta ya aure yanta. Sai tinkiya ta che "A, a, Auta ya aure yar mata da ba aso." Shi ke nan, sai akaba shi, akadaura mashi aure. Da ubanta, masaki, da uwanta da ba aso sai suka shiga achikkin dukiya.

To, suna nan suna zamma, suna nan suna zamma, sai ya yi ma tinkiya dakinta. Sai ya hau doki ya hada kaya, ya hada kaya, bayinshi suka bi shi. Sai ran nan sai ya che ma tinkiya yana so aure. Sai ta che "To, en zaka aure kadda ka aure karuwa." Ta che "To." Sai ran nan ya hau doki zashi kilisa, sai ya ga wota karuwa mai-keyau ba kamanta. Sai ya zo ya che shi ya samu machen aure. Sai tinkiya ta che "To, shi ke nan." Ba ta sake tuna mashi ba. Sai ya auro ta, karuwa, ya aje ta a gida.

Yana nan da karuwa, sai ran nan ya hau doki zashi kilisa. Da ya taffi, sai ya bar karuwa a gida da samari magudante.

Sai karuwa ta che "Kai, yau ba nama a gida, sai ayanka tinkiyan nan." Sai magudanche ya che "A, ni na zo na iske tinkiya a gida." Sai ta che "En ba ka yanka tinkiyan nan ba sai en sa asaishe ka." Sai ya che "To," sai ya kama tinkiya, ya yanka.

To ina fidan tinkiya, ina fidan tinkiya, sai yaro ya dawo dagga kilisa. Sai ya che "Enna kuka same nama?" Shiru. Sai ya che "A, na tambaya ku, ba ku gaya mani?" Sai karuwa ta che "Ai ni ma na rassa nama, na sa anyanka tinkiya." Sai ya che "To." Sai ya karbe nama duka, sai ya kumche nama achikkin pata, ya daure. Sai ya che da matanshi buduruwan nan, yar matanda ba a so, ya che "Ba ni parin wando, da para riga, da parin rawani, da wuka." Sai ya sa parin wando, da para riga, da parin rawani, ya dauka naman tinkiya, ya je daji, ya shara wuri, ya aje naman tinkiya agabban shi. Sai ya dauko wuka, ya che "Tun da tinkiya ta mutu ba da sanina ba, ni kuma en soke chikkina en mutu." Da ya dauko wuka zaya soke chikkinshi, sai nama ya che "Barri." Da ya ga nama ba ya tashi ba, ya che "A, a, ban barri ba, sai en soke chikkina." Ya sake dauke wuka zaya soke chikkinshi sai tinkiya ta tashe tsaye. Sai ta che "Ai na gaya maka kadda ka aure karuwa."

Sai ya che ma tinkiya "To mu taffi gida." Da zuwanshi gida sai ya kore karuwa, ya che "Matana guda ta ishe ni."

---

## 80

### The Lucky Youngest Son.

Wanni mutum mai-arziki ne, Ahmadu mai-kurdi, yayansa uku, matansa kuma uku. Kowache tana da da dede. Sai ya kwanta chiwu ya sani zai mutu. Sai ya kirra baban dansa, ya che "Kaddan na mutu, achikkin dukiyan nan kadda ka dauke komi, sai sanda da takalami." Shi kuwa ya che "Baba, halinka ke nan? Achikkin dukiyanka duk kadda en dauka komi sai sanda da takalami? To, ni ba zan dauka sanda da takalami ba." Sai ya che "To, taffi wurin uwarka ka zona." Sai ya kirra na biyunsu kuma, ya che "Ka ji Mohamma, kaddan na mutu, kadda ka dauka komi sai butar salla." Sai ya che "Halin Baba ke nan, ni ba zan dauka butar salla ba." Sai ya kirra Auta kuma, ya che "Kaddan na mutu, kadda ka dauka komi sai sanda da takalami." Sai ya che "Baba, na fison

rainka da komi," ya che "abinda ka che en dauka shi zan dauka." Ya che " To, ka dauka takalami da sanda."

To, da Auta ya dauka kuwa, ya tashi, sai uban ya mutu. Sai matan gida suka kuka suka kare. Sai suka taffi wurin sariki da rabon gado. Da akadiba, akaba shi baban dan, akaba nabiyunsu kuwa nashi. Da akaba Auta dukiya, ya ki, ya che takalami da sanda ya ishe shi. Sai uwar ta zo ta yi ta zagen Auta. Da ta zage shi, shi kuwa ya che shi ba ya dauka ba. Da ya gaji da zage kuwa, sai ya taffi daji.

Da ya kama hainya, ya gamma da wanni ya hada itache, ya sa wuta. Ya che "Samari enna zaka?" ya che "Enna ruwanka?" Sai ya wuche, sai ya tarada mahalbe, ya che "Samari ba zaka ba ni sandanka ba?" Ya dauke sanda ya ba shi. Sai ya duba tsuntsu asama, ya jefada sanda. Sanda ko ya maki asamma, sai ya dauke tsuntsun, ya ba yaro.

Yaro kuwa ya taffi, sai ya tarada wanni ya fura wuta ba shi da abin gassawa. Ya che " Samari ba ka ba ni tsuntsu da na kan gassa?" To, da ya ba shi, ya gassa ya chinye, sai ya debo toka ya kwunsa mashi a riga.

Yaro kuwa ya taffi, ya tarada wata mache. Tana tuwo ba ta da toka da zata zuba achikkin tuwo. Ta che " Samari ba zaka ba ni toka ba?" Ya ba ta. Ta dauke mara daya ta ba yaro, sai ya taffi.

Sai ya je ya tarada masu-fuda a gwona, sai sun che "Samari ba ka ba mu tuwonka mu chi ba?" Sai ya dauke ya ba su. Sai suka chinye. Sai suka dauka galma daya suka ba shi.

Sai ya je ya tarada makeri ya hada wuta da zugazugi ba shi da karifin kira. Sai ya che "Samari ba ka ba ni galma en kera wukaki ba?" Sai ya dauke ya ba shi, sai makeri ya kera wukaki. Da ya kera, ya ba shi daya.

Da yaro ya karba, ya yi ta taffia kuwa chikkin daji. Sai ya je ya tarada masaki, ya tara zugun fari. Sai ya che " Samari bu ka ba ni wukanka en yanke zugun farin nan ba?" Da ya ba shi ya yanke fari sai ya che "To, ka biya mani wukana." Sai ya dauke fari duka ya ba shi yaron.

Yaro yana taffiya sai ya tarada enda yariniya buduruwa ta mutu. Su ko, ba su da fari da zasu kai ta rami da shi. " Yaro ba ka ba mu farin nan da zamu kai gawa rami ba?" Sai ya dauke ya ba su, sai suka yanyanka, suka dinka, suka rufe yariniya. Da zasu kai ta rami, sai yaro ya rikke yariniya, sai ya che "Sai ku biyo ni farina." Sai suka dauka gawan suka ba shi, sai ya dauka aka.

Yana taffiya, sai ya fitta dagga chikkin daji, ya je ya tarada

baban gari. To, kuma da kogi fa a kofan gari. Ananan, matan sariki su kan zo su dauka ruwa. Shi ko, da ya zo da matachiya, sai ya tona rami biyu, ya sa sawunta, ya mika, ta tsaya. Sai ya kawo farin zannen nan duka, ya rufe ta har kassa, sai ya koma chan wojen ennuwa ya zona. Sai da matan sariki suka zo diban ruwa awurin, ya che "Du Allah ba ku ba matata ruwa ta sha ba? Ni na ba ta ta ki sha don alfarma." Sai daya, ita baban matan sarikin, sai ta debo ruwa a kwariya, ta zo, ta che "Ungo." Shiru—ba ta karba ba. Sai wota achikki matan sariki ta zabura, ta kwache kwariya, ta zo, ta che "Ungo" Shiru. Sai ta buga mata a goshi, sai gawa ta fadi. Sai yaro ya tasso dagga ennuwa, ya yi ta kuka, ya che matan sariki sun kasshe mashi mata a rafi, sai kururuwa ta kai har chikkin gari. Sai sariki ya che kariya ne, matansa ba suwa fadda. Sai akache "Aje, agani."

Da akazo, akagamma da gawa akwanche, akazo, akache da sariki "A, gaskiya ne, matanka suka yi kissan kai." Sai ya che "To, adauko ta." Da akadauko ta, akakai wurin sariki, sai ya che "Kai Yaro, Enna ka fitto da matan nan?" Sai ya che da sariki "Enna ruwanka?" Sai Alkali ya che "Yaron nan abin tsoro ne, ku sallame shi ya tashi." Sai sariki ya kawo mata biyu abakin nashi, ya ba shi. Sai yaro ya fitta ya taffi chikkin daji kuma, ya je ya zona achikkin dají, ya yi gida. Da ya yi gida ya tura mata biyu da sariki ya ba shi, ya che shi ya zona shi kadai.

Sai kwado ya che "Auta en zo gidanka en zona?" Ya che "Zo ka zona manna." Sai biri ya che "Auta en zo gidanka en zona?" Ya che "Zo ka zona manna." Doki ya che "Auta en zo gidanka en zona?" Ya che "Zo ka zona manna." Rakumi, jaki, chinaka, tururuwa, sa, gwano, alfadari, machiji kato, gauraka, hankaka, duk suka zo suka zona.

Suka yi chikki, duk gabba daya. Sai sa ya zo, ya che duka yai rumbu achikkin gida. Sun yi talatin. Ya zo yai rafoniya achikkin daki talatin. Kuma ya zo ya yi rami da zurfi talatin achikkin gida. Sai sa ya chikka rumbu duka da zinariya, haifuwansa, ke nan. Alfadari ya zo ya haifi azurfa, ya chikka rami duka nan talatin. Rakumi ya chikka rafoniya da farin kurdi. Sauran kuwa, yan-kankanana nan, suka haifi bayi, suka chikka gidan bayi.

Sai gizzo ya zo garim bara achikkin gida, sai ya debo dawa ya ba gizzo. Gizzo kuwa ya taffi wurin sariki, ya che "Albishirinka?" Ya che "Goro." Ya che "Kunenka nawa?" Ya che kunenshi biyu. Ya che "Kara biyu kuma ka sha labari."

Ya che ya kara. Ya che "Yaron nan yana nan achikkin daji, duk duniya nan ba mai-arzikinsa." Sai sariki ya che "Kariya ne." Ya che "To, ka sa ni da fadawa su je su gani." Sai ya sa shi da fadawa, suka taffi. Sai suka je suka ga dukiya, dukiya suka fi na sariki yawa. Suka je, suka che "Yaron nan da dukiya."

Shi kuma sarikin, akwai farin kuturu a gidansa. Maganan farin kuturu ita sariki ya ke ji. Sai ya che "To, Farin Kuturu, mi zamu yi mu kwache dukiyanshi?" Sai farin kuturu ya che "Adauko yakuwa, asa achikkin teki, adauko kwayan dawa fa, asa achikkin teki." Dayawa kuwa, akasaka achikkin teki, sai akadebo iburo kuwa akasa achikkin teki, sai akadebo dauro kuwa akazuba achikkin teki, akadebo gero akasa achikkin teki. Akadebo acha akasa achikkin teki. Sai akasa shinkafa da wake achikkin teki. To, teki kuma ya chikka, sai akadaura, akakai gidan yaro. Akache kaman gari ya waye ya tsinche dawa daya daya. Sai yaro ya ga ba ya iya ba, ya yi kuka, ya dinga kuka. Sai tururuwa ta zo sai chinaka, da kiyashi da gwano sun zo suka ba shi hakuri. Ya dauka kworiya duk ya ba su. Wanni ya dauka ya saka nan, wanni ya dauka ya saka nan. Kaman gari ya waye sai suka raba shi dabam dabam. Sai fadawan sariki suka zo garin dauka, sai ya dauka ya ba su. Sai sariki ya kirro farin kuturu, ya che "To, kakka zamu kasshe yaron nan?"

To, akwai wanni baban kogi baatabba shiga achikki ba. To, da giginiya kuwa atsakan kogi. Sai farin kuturu ya che da sariki "Ka gaya ma yaro ya kamo yayan giginiya guda biyu." To, angaya mashi. Sai yaro ya ga ba ya iya shiga ba, sai ya dinga kuka. Sai biri da kwado suka zo wurin yaro. Suka che "Yi shiru, don hakka muka che da mu zo gidanka mu zona." Sai biri ya tashi yana tsale har bakin kogi. Dagga gefin kogi ya tuma, ya hau kan giginiya. Kwado kuwa ya nutsa, ba ya fitta ba sai da ya kama giginiya. Sai kwado ya hau giginiya, shi kuma. Da biri ya tsunko, sai ya tsale sai woje, shi kuma kwado ya fitta da nashi, ya fado ruwa, ba ya fitto ba sai woje. Sai suka kawo yayan giginiya biyu, sai yaro ya zo ya aje. Sai fadawan sariki suka zo karban yayan giginiya da safi, sai ya dauka ya ba su. Suka kai ma sariki.

Sariki ya che "To, Farin Kuturu, mi zamu yi mu kama dukiyan yaron nan?" Ya che "Yanzu ga shi rani ne, babu ruwa, sai ka gaya mashi kaman gari ya waye ya kawo dainyen gero." Sariki ya che "To." Sai yaro ya zo ya dinga kuka, sai hankaka da gauraka suka zo, suka che "Yaro, kukan mi

ka ke yi?" Ya che "Sariki ya che en kawo masa dainyen gero yanzu achikkin rani." Suka che "To, share hawayenka ka yi shiru." Sai hankaka ta yi ariwa, gauraka ta yi kudu. Suna taffiya suna che "Da, da, da," en ji hankaka. Sai ta je enda ta tarada gero ya yi tsawo, sai gauraka ta tarada enda gero ya soma zubar ido. Ita kuwa hankaka ta tarada enda isa tumu, sai ta tsaya kuma, ta daura dami guda. Ita kuwa, gauraka ta tarada enda ya yi kwari, shi kuma ya daura dami guda. Hankaka ta dauko, gauraka ta dauko. Sai suka kai ma yaro. Da gari ya waye, ya kai gidan sariki.

Shi ko, dá machiji ya gani ankussa kasshen yaro, sai ya che "Samari," ya che "Um," ya che "Akwai yariniya, yar sariki, sariki yana son ta dayawa." Sai machiji ya che "Sai en shiga chikkin chikkinta, amma za'atara mallamin duniya duka su yi yariniya magani, amma ba ta warike ba. Amma kai en ka je, zaka warike ta." Ya che "Ni ne zan ba ka magani da zaka warike ta da shi." Ya che "Kaddan ka je wurin sarikin nan, ka che maganinka da wuya, sariki kuma zaya che 'Wanni abu zaya yi mani wuya?' Ka che 'zaya yi maka wuya manna.' Zaya che 'Samari komi wuyanshi na yi.' 'To, hantar Farin Kuturu ina so akawo mani yanzu.'" Ya che "To, kaddan ankawo hantar Farin Kuturu, ka zuba ruwa, ka sa kasko, aba yariniya nan ta sha. Sai ta warike." Sai yaro ya che "To."

Sai yariniya tana wasa achikkin yam-mata yar-uwanta, sai ko machiji ya tashi, sai ya shiga chikkin chikkinta. Sai yariniya ta che ma yar-uwanta chikkinta ta yi mata chiwu, zata gida abinta. Sai yam-mata suka che "Sai mu tashi, yar sariki ba ta da lafiya." Da ta taffi gida sai ta kwanta, sai chikki yana hawa, yana hawa, yana hawa, sai ya yi kaman rumbu. Sai sariki ya tashi, yana kuka, yana kuka, yana kuka, yana faduwa, yana komi. Sai Farin Kuturu wanda sariki ya ke so, ya zo yana ba shi magana. Akakirra mallamin gari duka, kowanni ya yi magani ba ya yi ba, yariniya ba ta warike ba. Akaje Faki Fatatika, akakirra mallamin garin suka zo suka yi magani, yariniya ba ta warike ba.

Sai yaro mai-arzikin nan ya zo da tsuma daya, ba shi da riga mai-keyau. Sai ya zo wurin sariki ya che "Rainka ya dadi." Sai Farin Kuturu ya tashi ya mare shi, ya che "Yar sariki ba ta da lafiya kai mai-tsuma ka zo?" Sai ya che "Ni, na zo garim magani ne." Sai ya che mallami "ba su yi ba, kai Mai-tsuma zaka yi magani?" Sai sariki ya che "A, a, ku bar shi, kowa da rataya da Allah ya ba shi." Sai sariki ya che "Ka taffi da Farin Kuturu wurinda yariniya ta ke." Da ya zo wurin

sariki kuma, ya che "To, sariki, ina da magani, amma maganina da wuya." Ya che "Ka gaya mani, komi wuyanshi azo agamma." Sai ya che "Ina so ka samu mani hantar Farin Kuturu yanzu yanzu. To, ga Farin Kuturu awurinka, za'ataffi chikkin gari garin nema?" Sai fadawa suka bubuga Farin Kuturu a zaure, sai suka yanka shi, sai akasa hanu, akatsage, akafitta da hanta, akaba yaro. Yaro ya che adebo mashi ruwa asa kwasko. Da akadebo ruwa a sabon kwasko, akakawo mashi, sai ya sa hanta achikkin ruwa, ya kada. Sai ya che "Aba yariniya ta sha." Da akaba yariniya ta sha sai zawo, zawon da ya gudu dagga nan ya ke kaman Birnin Gwari. Machijin nan ya fitta achikkin zawon nan, ya taffi, ba wanda ya gan shi.

Yariniya sai ta tashi, ta che aba ta tuwo ta chi. Ta che aba ta fura ta sha. Akaba ta, akaba ta goro kuwa ta chi. Nan da nan kuma sariki ya dauke shi yaro, ya kawo doki biyal ya ba shi, ya kawo alkiba biyal ya ba shi, ya kawo wanduna da bakka riga ashirin, ya ba shi. Sai ya tsaga rabin gari kuma ya ba shi. Sai ya che "Ni, ba ni so zamma a gari ba, za ni gida."

Sai ya kama dowakinshi da kaya da ya ba shi, sai ya taffi daji, ya tarada machiji ya taffi gida. Sai ya che "Yaro, rikichi ya kare, sai namu da kai kuma," en ji machiji. Ya che "To, ga shi za ni en zona chikkin sure." Sai ya che "Izan ka zona achikkin sure, enna abinda zan yi maka achikki?" Ya che "Kaddan lahidi ya yi, tsokar nama daya zaka ba ni." Ya che "To, na ji." Randa lahidi ya zo, yaro ya tashi dagga barchi, ya fitta woje, sai ya ga tsokan nama daya atsakan gida, sai ya dauke, ya kai wurin sure, sai ya komo gida.

To, kullum lahidi hakka akeyi mashi. Ran nan ya fitta dagga dakinshi da safi ba ya ga tsokan nama atsakan gida ba. Ashe, kwado ya zo ya dauke da sassafi. Da ba ya samu tsokan nama ba, sai machiji ya tashi ya zo wurinshi. Ya che ma yaro "Ran lahidi yau, ban ga tsokan nama ba." Ya che "Ina kain nema ke nan, sai ka tasso ka zo?" Ya che "Enna wanda ka ke dauka dagga tsakan gida?" Ya che "Da ina da su atsakar gida, yau da na tashi ban gani ba, babu wanni kuma." Ya che "Ashe, da munafukai achikkin gidanka?" Ya che shi, ba ya sani ba, shi. Ya che "Ka ba ni munafukai en zo, en kama?" Ya che "To." Ya duba, duka mutane suka yi mashi rana, ya che "To, wanene zaya biya achikki?" Machiji ya che "To, ni na koma gida, na samu munafuki yana yawo." Da ya fitta sai ya rabi achikkin kofar gida.

Shi kuwa mai-kurdi, ba ya iya zamma agidanshi, sai ya je ya ba machiji magana. Ya fitto kofar gidda, sai machiji yana kofar gida ya sare shi. Da ya sare shi ya komo chikkin gida, shi Auta, ya kwanta. Kaffa na chiwu. Sai kwado ya zo ya che "Mi ya same ka mai-kurdi?" Ya che "Wanni abu ya same ni a kofar gida." Ya che "Kominene na je na gani." Sai ya fitto, yana tsale, sai ya zo kofar gida, sai machiji ya sare shi, sai ya ji, ya kwanta. Shi kwado ya mutu. Shi kuma mai-kurdi ya mutu.

Iyakachinta ke nan ita wannan. Kwado ya ja mashi wannan, don shi ya dauka nama ya yi mashi sanadi.

---

## 81

### The Division of the Inheritance.

Wanni mutum yayanshi uku, biyu mata, daya namiji. Namijin sunansa Karrambanna. Daya kuma Kumburin Dammo, daya kuma Mai-hakuri.

Sai ya mutu uban nasu. To kurdinsa kuma zambar ashirin da wuri daya. Da za'araba gado akache "Mi za'ayi da wuri daya? Sai aba Karrambanna, shi ne baba." Sai Kumburin Dammo ta che ba ta yarda ba, ta che "Sai araba wannan uku, kadda kowa ya yi zalinchi." Sai akache "To, wa zaya iya raba wuri dedede?"

Sai wanni tsofo ya che "Akwai wanni mai-rabar gado dede, sunansa Atteyu, shi kuma jikkinshi hanta ne." Sai akaje akakirra shi, akache mashi "Ga kurdi zambar ashirin da wuri daya anrassa wanda zaya raba su dede, shi ya sa akanemo ka." Sai ya che "Op, ai wannan mai-sauke,' sai ya che "yayanshi nawa ne?" Sai akache "Su uku." Sai ya che "Aba su hamsa hamsa"—to achikkin zambar ashirin da wuri daya ya rage hamsa da wuri. Ya che "Abasu dubu dubu"—ya rage alfin da wuri. "Achikkin alfin da wuri aba su dari biyal biyal"—ya rage biyal da wuri. Ya che "Aba su dari dari"—ya rage metin da wuri. Ya che "Achikkin metin da wuri aba su hamsin hamsin"—ya rage hamsin da wuri. Ya che "Achikkin hamsin da wuri aba sa goma goma"—ya rage ashirin da wuri. Ya che "Achikkin ashirin du wuri aba su biyal biyal"—ya rage shida, "To sauran shidan nan," ya che "aba su biyu biyu. Ba wanda ya yi ma wanni zalinchi." Shi ke nan, ya che "Na raba maku gado."

82

## The City of Women.

Wanni goro ke nan, ba shi da mata, sai ya taffi ya yi noma. Sai wanni kunkuru ya zo, ya che " Noman goro tashi birikicha."

Sai goro ya zo ya gani, ya che " A, wanene yana yi mani wannan aiki?" Sai ya che " To, na tsaya en gani wanda yana sa nomana yana tashi." Da ya yi noma ya boya a bakin daji, ya tsaya. Da zuwan kunkurus, sai ya che " Noman goro ki tashi birikicha," sai noma ya tashi. Sai goro ya zo, ya dauke fatainya, ya buge shi abaya. Sai kunkurus ya che " Goro! barri, barri, na ba ka mata." Sai ya che " To, je ka goro ka yi sema." Da ya yi sema, ya che " To, ga shi, na yi." Ya che " To, shiga chikki, ni ko en dauke ka," en ji kunkurus. Sai ya che " To."

Kunkurus ya dauke shi wanni garinda sai mata, ba miji ko guda daya. Da kunkurus ya kai shi garinda ba mazza, ya che " Ga kuka." Sai ya kwanche sema. Da talakawan mata suka gani miji, suka che " A, wannan miji ya fi karifinmu, sai akai shi wurin sariki kuma." Da ta gan shi ta yi masa riga, ta yi masa wando, ta yi masa alkiba, ta saye mashi doki. Duka abin dadi na sarauta ta ba shi.

Sai ta che " To, amma zani taffi yaki," sai ta che " Ka ga dan kwotachen nan, kadda ka bude shi." Amma ta che " Duk kayan da ya ke chikkin gida naka ne, amma dan kwotachen nan idan ka bude shi zuchiyanka zaya bache." Sai ta tashi ta je yaki, ta bar shi a gida. Sai ya che " To, duk kayan yana gidana sai em bude dan kwotache." Da ya bude shi sai ya gani tsakan gwonanshi, sai dan walki, sai fatainya, ba ya kara gani gida ba. Sai ya yi kuka, ya che " To, enna zan samu kunkuru zaya kai ni."

Sai ya taffi bakin daji, ya samu dan kunkurus kankani, sai ya aje shi, ya che " To, da na yi noma sai ka che ' Noman goro tashi birikicha.' En na zo zan dauke fatainya en buga ka, sai ka che ' Barri, barri, en kai ka garin mata.' " Akayi hakkanan ya che " To, ka che mani en yi sema." Sai dan kunkurus ya che " Yi." Da ya yi, ya shiga chikki, ya che " Dan kunkurus ka dauke ni." Sai ya che " To." Da ya shiga, dan kunkurus da ya dauke shi shina nishi ba shi da karifi, sai ya che " Wayo, wayo!"

Sai ya gamma da kura, kura ta che " Dan kunkurus mi ka ke dauka?" Sai dan kunkurus ya che " A, goro ya che en dauke shi." Sai kura ta che " Ayarda dan durinuwa en chainye shi." Sai dan kunkurus ya yarda sema, sai kura ta zo ta keta sema, ta dauke goro ta chainye.

83

## The Town where None might go to Sleep.

Wata mache ke nan, ta haife yaya biyu duka mata. Sai ta kai daya aure a garinda ba abarchi, ta dauke daya ta kai ta garinda ba akashi.

Sai ran nan ta yi dadawa ta dauke wurin yanda ta kai a garinda ba abarchi. Sai ta dauke, ta taffi. Da ta zo, sai gida duk suka yi mata "Marhaba, Marhaba." Sai akayi mata abinchi, mai-gida ya che "Ga sarakuwata ta zo." Sai yan ta che ma uwar "Iya, ba abarchi nan ba, kadda ki chi dayawa ki koshi, barchi ya kama ki." Sai ta che "Tun ba anhaife ki ba na san garin nan ba abarchi." Sai yan ta che "To, shi ke nan, na yi shiru." Akakawo mata tuwo, ta chi, ta koshi.

Sai ran nan ta kwana da dare ba ta barchi ba. Da gari ya waye sai yan ta dauke tulu zata rafi. Sai ta che ma uwar "Ga shi, na yi samwan tuwo, ki izza mani wuta." Da ta taffi rafi, da tana izza wuta, sai barchi ya kama ta, ta kwanta. Sai wota tsofuwa ta zo deban wuta, sai ta duba, ta gani tana barchi, ta che "Wayo Allah! sarakuwar wane ta mutu."

Sai akasamu masu-ganga, duk gari ya taru gida, akagini rami. Sai ganga yana che "Birrim, birrim, taka rimfa, mutuwa a gidan sarukai." Sai yan dagga chan ta ji, sai ta che "Barri, barri taka rimfa, barchi gadon garim mu." Da ta zo, sai ta buge ta, ta che "Tashi, tashi." Sai ta tashi pirigiji, mutane suna wa'atse. Sai gari suka koyo barchi.

Sai ta koma gida, ita uwar, sai ta daffa dadawa zata kai ma yanda ta kai garinda ba akashi. Da ta taffi, sai mutanen gida sun che "Marhaba, marhaba." Sai mai-gida ya che "Sarakuwana ta zo." Sai ya yanka kaza, akakai mata tuwon shinkafa. Sai yan ta che ma uwar "Kadda ki chi dayawa, kin san gari duk ba akashi ba." Sai ta che "Op, tun ba anhaife ki ba na san garin ba akashi." Sai ta che "To, ta kiyale ta." Sai ta chikka chikki da tuwo.

Da dare ya yi tamatsun kashi ya zo, ta rassa wurinda zata yi. Sai ta je wurin turikin doki ta yi, ta rufe da chiyawa. Sai kassan gari ya tashi, yana nishi, ya che "Um, um, ban saba ba, um, um, ban saba ba."

Sai mutanen gari suka che "To, wane ya yi kashi a garin?" Sai akache "Sai afitta da goran tsafi, da yaro da baba, kowa ya zo ya ketare goran nan, wanda ya yi kashi gora ya kama shi." Sai gari duka ya ketare, ba wanda gora ya kama. Sai wanni ya che "A, ga shi, anyi bakuwa, ta zo ta ketare gora." Da ta

zo ta raba kaffa zata ketare goran nan, sai gora ya kama ta. Sai duk gari ya che "Ita ne ta yi kashi, ita ne ta yi kashi." Sai goruna suka yi waka, suna chewa. "Ta rungu rungun, sarakuwa ta samu." Ba dama ta zona kuma, suna nan a jikkinta.

Sai gizzo, mai-karambani, ya gammu da ita, ya che "A, Sarakuwa, kina da gora mai-dadin waka hakka? Ni ina son su." Ita ta che "To, sai ka yi kashi, ka che ba ka yi." Da ya yi, ya che "To, ba ni na yi kashin nan ba, en ni ne ya yi, goruna ku zo ku kama ni." Sai goruna suka bar mata, suka kama shi. Sai suna waka, suna chewa "Ta rungu rungun, gizzami ya samu." Gizzo yana jin dadi yana rawa.

Da ya gaji da rawa, sai ya che "O Sarakuwa, Abin Kumiya, zo ki karba goranki." Sai ta ki, sai ya hau bissa itache. Da ya hau itache, ya fado kassa a gindi yana so ya passhe goruna. Su suka ki, suka koma woje daya, sai gindin gizzo ya passhe, gizzo ya mutu. Sai goruna suka koma gida. Sai gari duk suka yi ta kashi, suka gani ba komi.

---

## 84

### The Mender of Men.

Yam-mata suka taru, suka taffi daji tsinan gainye. Lokachin nan sai ruwa ya dauko, dagga gabas ina zuwa, sai suka gudu, suka shiga kogon kuka. Sai Iblisi ya zo, ya rufe. Da ruwa ya dauke, sai Iblisi ya che duka su kawo dutsin wiya da zanne afishe su. Suka bayas sai guda daya ta ki bayaruwa. Kingis ya zona, saura suka fitta. Kuka da dan kofa karami asamma. Sai akaje, akagaya wa uwan yariniya. Sai ta taffo, ta zo, ta ga enda yanta ta ke. Sai kuma ta koma gida, sai ta yiwo abinchi. Ta taffo da almuru, ta zo, ta che "Yariniya, Yariniya, miko hanunki ki karbe tuwo." Sai ta mika hanunta dagga dan kofa, ta karba, ta chi. Uwan yariniya ta koma gida.

Ashe, kura ya ji. Kuma da almura ya dawo, ya che "Yariniya, Yariniya, miko hanunki ki karbe tuwo." Ta che "Wannan ba muriyan uwata ba ne." Sai kura ya koma wurin makeri, ya che "Kera min muriyana." Sai ya che "En na kera maka muriyanka, har kafin ka je gindin kuka komi ka samu zaka chi." Sai ya che "To, bar en kera." Ina taffiya, sai ya samu buzuzu, sai ya che "Abin safi da rena ko ne?"

Sai ya samu buzuzu ya chainye. Sai ya taffi gindin kuka, ya che "Yam-mata, Yam-mata, miko hanunki ki karbe tuwo. Sai ta che "Wannan ba muriyan uwata ba ne."

Sai kura ya yiwo fushi, ya koma wurin makeri kuma zaya chainye makerin. Sai ya che "Tsaya, tsaya, tsaya, kadda ka chainye ni." Sai ya che "Domi zaka chainye ni?" Sai ya che "Domin ba ka kera mani muriya dakeyau ba." Sai ya che "Tsaya en kera ma dakeyau." Sai ya kera masa muriyansa dakeyau, sai ya komo wurin yariniya. Sai ya che "Yariniya, Yariniya, miko hanunki ki karbe tuwo." Sai ta mika hanunta. Da ta mika, sai kura ya kama, sai ya jawo yariniya, sai ya chainye yariniya, sai ya bar kasshi. Sai ya taffi.

Sai kuma da uwan yariniya da almuru ta kawo tuwo, da ta zo, sai ta ga kasshin ya tata, sai ta yi kuka anan. Sai ta koma gida, sai ta je ta dauko masaki, ta zo, ta debi kasshin, sai ta kama hainyar garin kerar mutum.

Tana taffiya sai ta tarada tuwo ina tukuwa da kansa. Sai ta che "Tuwo, nuna min hainyar garin kerar mutum." Sai ye che "Zona nan ki chi ni." Sai ta che "Enna nima balle en chi ka." Sai ya che "En kin je, ki dauke hainyan dama ki barri na hagun."

Da ta taffi sai ta tarada nama ina soyewa da kansa. Ta che "Nama, nuna min hainyar garin kerar mutum." Sai ya che "Zona nan ki chi ni." Sai ta che "Enna nima balle en chi ka." Sai ya che "En kin je, ki dauke hainyan dama ki barri na hagun."

Sai ta taffi, tana taffiya sai ta tarada fura ina damuwa a mudu. Ta che "Fura, nuna min hainyar garin kerar mutum." Sai ya che "Zona nan ki chi ni." Sai ta che "Enna nima balle en chi ka." Sai ya che "En kin je, ki dauke hainyan dama ki barri na hagun."

Tana taffiya sai ga ta a garinda anakeran mutum. Sai akache "Mi ya kawo ki inna?" Sai ta che "Kura ya chi dana." Sai akache "Enna kasshin?" Sai ta sauke masakinta, sai ta che "Ga kasshin." Sai akache "To, sai gobe akera maki yarki."

Da gari ya waye sai akache da ita "Ki je kiwon shanu." Sai ta tsinche shanu ta taffi kiwo, shanun kuma ba su da abinchi sai aduwa. Da ta dauke aduwa asama, in sun zubo, sai ta debe nunanu ta bai shanu, ita kuwa sai ta debe dainya sai ta chi. Da hakka har mareche ya yi, sai suka koma gida. Da suka zo shingi, sai bajimi baban kukansa ya kan che "Matan nan mai-keyaun hali ne, akera ya tata dakeyau."

Sai akakera yar dakeyau. Ita kuma ta komo gida. Sai akache " Kwana, sai gobe ki taffi garinku." Sai da safi akafido ya tata, akagamma ta da uwanta. Sai suka kama hainyan gida.

Da ta komo garinsu, tana da kishiya, kishiya kuwa da yanta, amma mumuna che. Sai ta che ita kuma zata kasshe yanta ta je garin kerar mutum.

Sai ta dauko yanta, ta saka a turimi, sai ta yi ta kiribawa. Tana chewa " Iya zaki kasshe ni ? " Ita kuwa tana kiribawa, sai ta fida kasshin, sai ta kawo masaki ta zuba kasshin, sai ta kama hainyar garin kerar mutum.

Tana taffiya sai ta tarada tuwo ina tukuwa da kansa. Sai ta che " Tuwo, nuna min hainyar garin kerar mutum." Sai ya che " Zona ki chi ni tukun." Sai ta che " Op, sai ka yi mani tayi en chi ka ? " Sai ta zona ta chainye tuwon.

Da ta taffi sai ta tarada nama ina soyewa da kansa. Ta che " Nama, nuna min hainyar garin kerar mutum." Sai ya che " Zona ki chi ni tukun." Sai ta che " Op, sai ka yi mani tayi en chi ka ? " Sai ta zona ta chainye nama.

Sai ta taffi, tana taffiya, sai ta tarada fura ina damuwa a mudu. Ta che " Fura, nuna min hainyar garin kerar mutum." Sai ya che " Zona ki chi ni tukun." Sai ta che " Op, sai ka yi mani tayi en chi ka ? " Sai ta zona ta shanye fura.

Tana taffiya sai ga ta a garinda anakeran mutum. Sai akache " Mi ya kawo ki inna ? " Sai ta che " Kura ya chi dana." Sai akache " Enna kasshin ? " Sai ta sauke masakinta, sai ta che " Ga kasshin." Sai akache " To, sai gobe akera maki yarki."

Da gari ya waye sai akache da ita " Ki je kiwon shanu." Sai ta tsinche shanu ta taffi kiwo, shanun kuma ba su da abinchi sai aduwa. Da ta dauke aduwa asama, in sun zubo, sai ta debe dainyen ta bai shanu, ita kuwa sai ta debe nunanu sai ta chi. Da hakka har marechе ya yi, sai suka koma gida. Da suka zo shingi, sai bajimi baban kukansa ya kan che " Matan nan mai-mumunan hali ne, ku kera yar da muni."

Lokachin nan sai ta daure shanu, sai ta komo gida. Sai akache " Kwana, sai gobe ki taffi garinki." Sai da safi akahalita yar sau daya, gusunta bari daya ne, hanunta daya ne, duk halita woje daya ne ; hanchi rabi, rabi babu. Sai da safi ta fitta ta che zata taffi gida, akafido mata yanta, sai suka kama turaba.

Da suka fitta daji, sai uwar ta che " Ni ba uwanki ba ne." Sai uwar ta ruga aguje, sai ta je ta yi kwanche achikkin bunu.

Sai yan nan tana bin sau, tana bin sau, tana bin sau, sai ta che "Tashi mu taffi." Sai ta che "Taffi, ke ba yana ba ne." Sai ta che "A, ke ne uwana."

Sai uwar ta gudu, ta makye a wanni itache, ta boya. Sai yan nan tana bin sau, tana bin sau, tana bin sau, sai ta che "Tashi mu taffi." Sai ta che "Taffi, ke ba yana ba ne." Sai ta che "A, ke ne uwana."

Sai uwar ta gudu ta shiga kozozobo ta boya. Sai yan nan tana bin sau, tana bin sau, tana bin sau, sai ta che "Tashi mu taffi." Sai ta che "Taffi, ke ba yana ba ne." Sai ta che "A, ke ne uwana."

Komodo sai uwar ta gudu sai garinsu, sai ta shiga chikkin daki, sai ta rufe kofa. Sai yar ta je kofan daki, ta che "Iya, na zo." Ta yi shiru. Sai ta bude kofa, ta shiga, ta je wurin uwar. Shi ke nan, sai suka zona tare. Kishiya tana gani yar wanchan dakeyau, tata mumuna.

---

## 85

### The Porcupine becomes a Step-Father.

Wata tsofuwa kowanni tari ta yi da ne, ta haife da kaman garin nan duka. Da ta haife su sai ta mutu. Su kuma su yayan duk suka mutu, suka je kiyama, suka tashe ta, suka che "Enna ubammu?" Sai ta che "Ku tsaya kowai, na nema maku ubanku." Sai ta che "Gobe ubanku ya zo." Suka kwana, garin Allah ya waye, sai suka zo, suka che "Iya, enna ubammu?" Sai ta che "Ubanku ba ya zo ba tukuna."

Kullum hakka, kullum hakka, sai beguwa ya ji labari. Da beguwa da gari ya waye, sai ya taffo, ya che da tsofuwa "In de yaran nan sun zo," ki che da su "Ga ubanku ya zo." Sai da safi yara suka zo, sai ta che "Ga ubanku na chikkin daki." Sai beguwa ya fitto woje, sai ya che "Kowanni ya zo ya kama kaya daya daya, en kun ga kaya ya yi dede da ku kun san ni ubanku ne." Duk suka zo, suka kama kaya, sai kaya suka yi dede da su. Sai suka che "Baba, in ka mutu, gadon mi zaka barri mamu?" Sai ya che da gadonda ya barri masu. Sai ya che kayan nan da suka kama, randa ya mutu kowa ya zo ya chiri daya daya, da sun chiri kowa shi birni a rami.

Suna nan, suna zone, sai uba sai ya mutu, kowa ya zo ya chiri kaya. Sai rabi suka birni, rabi kuwa suka aje a daki.

Waddanan da suka birni nasu, da kwana bakai ya yi kayan nan suka zamma shanu, suka fitta. Su kuwa da suka che ba suwa birni, kayan nan suka che ba suwa zamma a fili, kowanene ya tashi ya shiga jikkin dan, sai suka mutu.

Ba suwa tashi har abada, sun kiyale maganan ubansu. Su kuwa waddansu, suka yi arziki.

---

## 86

### How Auta killed Dodo.

Wanni Dodo ya zo gari, yana kuka, yana chewa "A garin nan wane ni?" Duk gari sun boya. Sai dare ya yi kuma, su duk sun boya achikkin rafoniya.

Sai wanni yaro, wai shi Auta, ya ji labari, ya zo, ya kwanta a gidan wota tsofuwa. Dare ya yi, Dodo ya che "Wane kamana a gari nan?" Yaro ya che "Ni ne kamanka." Kamacha ta che "Kai yaro, ka hauka ne? Shiga daki ka boya, ga Dodo ya zo." Ya che mata "Ki yi barchi abinki." Ya tsinsti dutsi guda bakwai, ya sa wuta. Dodo na magana, yaro na amsa, har Dodo ya zo kussa ga kofan zaure.

Dodo ya che "Wane ni?" Yaro ya che "Ga ni." Dodo ya sunkwiya, zaya shiga zaure kaman yaro. Yaro ya dauke dutsi daya ya jefa mashi a baki. Dodo ya hadiye, ya koma awoje ya tsaya.

Ya che "Wane ni?" Yaro ya che "Ni ne ka." Dodo ya sake shiga zaure, yaro ya dauke wanni dutsi kuma, ya jefa, Dodo ya hadiye, ya koma woje. Dodo ya sake zuwa, yaro ya sake jefawa, har dutsi bakwai sun kare. Dodo ya koma woje, ya zamma har gari ya waye, ya mutu.

Mata suka fitta da safi zasu rafi, suka taffi, suka ga Dodo ya mutu. Suka sa hanu suka yi kururuwa "U, U, U." Yaro ya tashi da da dare ya yanke wuchiyar Dodo, ya zo ya boye ta a gida.

Sarikin gari da safi ya sa masu-ganga su yi kiddi gari duk su taru. Ya che da masu-yakinshi "Ku taffi wurin Dodo, ku duba ko shina da rai, wanda ya kissa shi, em ba shi bawa goma." Kowanni ya zo dokinsa da ya ga Dodo sai ya koma aguje. Sai sarikin karma, mai-takobi, ya zo, ya duba, ya ga Dodo ba rai, sai ya taffi ya che da mutanen gari "Ku zo, ga shi ya mutu." Sa'anan suka tashi duk da dokinsu, suka taffi wurin Dodo.

Sa'anan sariki ya nema achikkin gari duk, ba ya samu mai-kissa ba. Sa'anan wanni ya che "Ina ji wanni yaro shina amsa ma Dodo magana a gidan kamacha." Ya che "To, ka taffi gidan, ka duba, idan yaro na nan, azo da shi." Aka taffi, akazo da yaron. Sa'anan yaro ya zo da wuchiar Dodo. Ya mika ma sariki. Sariki ya kama bawa goma ya ba shi, ya kawo yarshi ya ba shi, ya nema gida ya ba shi. Wannan ya kare.

---

## 87

### How the Zankallala killed Dodo.

Zankallala ke nan, Dodo mai-hadiyen mutane. Sai ya kore wanni yaro abakin ruwa, sai yaro yana gudu sai ya gamma da zankallala. Zankallala ya che "Enna zaka?" Ya che "Ina gudun Dodo." Ya che "Zona abinka, Dodo ba zaya yi komi da kai."

To, itachen rimi ya chiro a kainshi, tsuntsaye akan rimi suna mashi waka, suna chewa "Zaki na tsoron Zankallala, Kura na tsoron zankallala, Dodo na tsoron zankallala."

Suna waka, suna fadi hakka, sai Dodo ya zo, ya ji, ya che da zankallala "Enna ajiyana?" Ya che "Wanni ajiya ka ba ni?" Ya che "To, en ba ka ba ni ajiyana, kai ka zamma namana." Sai ya kama zankallala, ya hadiye, sai zankallala ya fitto dagga chikki, ya tsale, ya che tsuntsaye su yi mashi waka. Sai ya sake kama shi, ya hadiye, sai ya fitto dagga tsakkan baya, ya che tsuntsaye su yi mashi waka. Sai ya sake hadiye shi, sai ya fitto dagga tsakkan kai, sai Dodo ya fadi, da ya fadi ya mutu.

Zankallala ya che da yaro "To, taffi, ka ga wanni ya fi wanni, ka chira saboda ka gamma da ni."

---

## 88

### The Wrestlers and the Devil.

Awudu, Sarikin Karifi, ubanshi da shanu dari daya da guda hamsin, ya yanke su duka ya yi burgami da pata, ya taffi fatauchi da su. Sai ya taffi zashi yawon karifi.

Sai shina taffiya, ya gammu da wanni, wai shi Hambari, shi kuwa mai-karifi ne. Shi, dan karifi, ya iske rijiya sai ya karkada baki ya sha ruwa. Sai Awudu ya zo ya iske shi a rijiya. Sai

suna taffiya tare, su biyu ke nan. Sai suka je suka iske ruwa a kogi ina gudu. Sai Hambari ya buga ruwa da hanu, sai ruwa ya rabu biyu. Sai Awudu ya che "Kai, Hambari, kana da karifi."

Suna taffiya, sai suka gammu da Dashira, shi kuma mai-karifi ne. Sai ya che masu "Zaku yawon karifi ne?" Suka che "I." Sai ya che to, shi kuwa zashi. Su uku ke nan.

Suna taffiya, suna taffiya, sai suka gammu da Tankoko, shi kuma mai-karifi ne. Ya che "Enna zaku?" Suka che "Zamu yawon karifi." Ya che shi ko zaya bi su. Su fudu ke nan.

Sai suka taffi daji, suka sauke a gusun kuka, su fudu. Sai suka che "To, gari ya waye yanzu zamu farauta, amma abar Hambari ya yi jiran gida." Sai suka taffi su uku farauta.

Ashe gusun kukan da Iblis. Sai Iblis ya zo, ya che "Kai, Hambari, anche karifi gare ka, tashi mu yi kukuwa." Sai suka tashi, suka yi ta kukuwa, da Iblis, da Hambari, sai Iblis ya kada Hambari, ya daure. Sai da suka komo sai Awudu ya che "Op, mi ya same ka Hambari?" Ya che "Mun yi kukuwa da Iblis ne, ya kada ni, ya daure ni." Shi ke nan, sai akache "To, gobe abar Dashira sarro."

Sai suka tashi suka taffi faraunta, da Awudu da Tankoko. Sai Iblis ya fitto, ya che "Kai Dashira, anche karifi gare ka, tashi mu yi kukuwa." Da suka yi kukuwa, sai ya kashe shi, ya daure. Shi ke nan, da Awudu da Tankoko suka komo, sai Awudu ya che "Op, mi ya same ka Dashira?" Ya che "Mun yi kukuwa da Iblis ne, ya kada ni, ya daure ni." Shi ke nan, sai Awudu ya che, "To, Tankoko, gobe kai ne da kumun gida."

Sai Awudu ya taffi shi kadai farauta. Sai Iblis ya fitto, ya che "Kai, Tankoko, anche karifi gare ka, tashi mu yi kukuwa." Da suka yi kukuwa, sa ya fiyada shi a kassa, ya daure. Da Awudu ya komo, ya iske Tankoko, andaure shi. Ya che "Op, Tankoko, mi ya same ka?" Ya che "Mun yi kukuwa da Iblis ne, ya kada ni, ya daure ni." Shi ke nan sai Awudu ya che "To, ni kuwa, gobe ba ni zuwa farauta, Iblis ya zo ya iske ni."

Sai Iblis ya zo, ya che "Awudu." Ya che "Um." Sai Iblis ya che "Kun zo yawon karifi ku fudu," ya che "To, ni kadai na iske ku." Ya che "Ka ga na yi da uku, saura kai kadai." Sai ya tashi, sai suka yi ta kukuwa, da Awudu da Iblis suka kama kukuwa. Suna kukuwa, suna kukuwa, suna kukuwa, ba wanda ya kada wanni. Suka tashi sama, suna yin rugumi. Da Hambari da Dashira da Tankoko suka wa'atse. Awudu da Iblis suka yi rugumi, har yanzu ba su barri ba, dalilin rugumi ke nan.

## 89

### The Two Girls and the Demons.

Da yar gata da wanda ba aso. To, gwonansu yana chikkin daji da nisa. Sai akadauke wanda ba ason nan, akakai ta gwona, akache "Kadda ki kara zuwa gida," ta zona ta yi jiran biri. Shi ke nan, ta zona, tana jira, en dare ya yi sai ta shiga dakinta, ita daya, ta yi ta barchi.

Lokachin nan aljannu suka zo, su ke tarawa a kofan dakinta. In sun tashi da safi zasu taffi, sai su kawo mata dukiya, su barri mata a kofan daki, su kan taffi. Sai ta aiki a ubanta a gida, ta che ubanta ya zo ya debe dukiya dagga gidanta. Sai ubanta ya zo, suka debe dukiya, suka taffi gari. Sai ta koma gida.

Sai uwar yar gata ta ga dukiyan, sai ta che "Enna wannan ta samu?" Sai akache "A gwona ta samu." Sai ta che ita ma zata, yar gata. Da ta zo gwona sai dare ya yi, sai ta shiga daki. Tana kwanche, sai aljannu suka zo, suna tarawa da dare. Ita kuma, sai ta fitto daki, ta shiga chikkinsu. Sai suka fifige naman jikkinta, suka chi, suka wa'atse.

Ta mutu.

---

## 90

### The Three Youths and the Three Demons.

Samari kuma guda uku suna zuwa wanni gari su dauko mata su zo garinsu, su kwana. Kullum suna zuwa, ashe akwai iblisai a hainya. Sai mata aljannu guda uku suka che "Barri mu yi dabara mu kasshe yaran nan."

Sai suka yi kayan ado, sai yaran nan suka tashi dagga wanchan gari zasu dauko mata, sai suka chikaro da mata aljannu guda uku. Sai suka che "Op, ga shi, mun zo neman mata, ga shi mun samu." Sai mata suka che "Mu zamma nan kadan, mu yi hira tukuna, mu koma tare da ku." Suka zamna suna hira, su ke kwakwanche akan chiniyan mata, sai baban nasu ya mika kaffa, sai ya tabba sawun mata, sai kofato kaman na doki.

Lokachin nan sai ya tsoratta a jikkinsa, zuchiyansa ya yanke. Lokachin nan achikkin yaron nan su guda uku, sai ya kirra autansu, ya che barri ya aike shi gida, ya manta da wanni abu. To, suka koma woje daya, sai ya che "In ka je gida, kadda ka komo, matan nan matan iblis ne." Autansu da ya je, sai ya yi zammansa a gida. Sai kuma ya kirra ma-bin Auta, sai ya che "Na aike Auta ya dauko mani wanni abu, ba ya zo ba, taffi

massa ka kirro shi." Da ya koma woje daya, sai ya che "In ka je gida, kadda ka komo, matan nan matan iblis ne." Shi kuma ya bi Auta. Kuma dagga shi sai matan aljannu uku.

Sai ya che shi gumi ya dame shi. Sai ya tube rigansa, sai ya nadde rigansa dakeyau. Sai ya che gumi ya dame shi. Sai ya tube wandonsa. Sai ya dauko rigan nan sai ya sa shi achikkin wandonsa, sai ya aje kussa da shi. Lokachin nan da ya tashi, ya zare wandonsa, ya rataya, sai furima aguje. Sai matan iblisi suka bi shi.

Da ya zo, ya samu dangan shingin gidansa, ya tuma asama zaya fada achikki, sai suka kama kaffansa. Kuma kainsa yana reto achikkin gida, kaffansa kuma sun rikke. Lokachin nan sai ya che "Op ba kaffana kuka kama ba, sai darni kuka kama." Da suka sake sawunsa, sai ya fado, sai ya gudu achikkin gidansu.

Sai mata aljannu sai suka koma kuma.

---

## 91

### The Ungrateful Men.

Wannan kuwa mache che de, sai ta je gunda maiya ta ke deban abin miya. Ita kuma yar, bakinta tara ne. Sai ta je ta debo yakuwa, sai ta je ta yi giriki da shi. Da ta yi giriki, sai ta deba, ta kai wa mijin. Da ta kai wa mijin, ta deba ta kai wa uban mijin. Ta kai wa uwan mijin, ta bai wa kishiya.

Sai mijin sai ya bude tuwo. Da ya bude, sai tuwo ya che "Rufe ni, rufe ni, im ba ka rufe ni ba yanzu ka mutu." Uban miji ya bude zaya chi, sai tuwo ya che "Rufe ni, rufe ni, im ba ka rufe ni ba yanzu ka mutu." Sai ya rufe. Sai ya je ya dauko tuwon uwa tasa, ya gangamma tuwo da na uwan da na uban da nashi, sai ya tara duk, sai ya je ya zubar ma mata a ka. Sai mache baki ya fitta kaman tara. Sai ta passa garin, ta zamma maiya. Da ita ba maiya ba che.

Shi ke nan, sai gari duk ya passu, duk suka gudu sai makafo da gurugu. Sai makafo ya che "Um, wota mache shegiyar mache de, mijinta ya che kadda ta je ta debe yakuwa, sai da ta debo." Sai shi ke nan, ashe sai mache tana kussa da su. Shi ke nan, sai gurugu ya che "Kai, Makafo, ni ba ni da sawu, ka gwoye ni, ni da ni ke da ido, en na gan ta na gaya ma, mu gudu." Sai makafo ya che "To." Sai ya gwoye gurugu. Shi ke nan, da ya gwoye shi, sai ya ga maiya. Sai ta zo, ta che "Makafo, tabba bakina ka ji," sai gurugu ya che "Ita che."

Sai makafo ya che "In ji," sai ya mika hanunshi. Sai ta gwundile hanun makafo. Sai shi ke nan, sai makafo ya yarda gurugu, sai ya shirga aguje. Sai ya je ya shiga achikkin kaya. Sai gurugu ya tashi aguje, sai ya je ya shiga kogon kuka.

Sai shi ke nan, sai gurugu ya samu kaffa, kaffansa ya mike, iya taka kadan kadan. Shi ke nan sai gurugu ya che "Makafo, na samu kaffa." Sai makafo ya che "Gurugu, na samu ido." Yana gani kadan kadan. Sai shi ke nan, sai makafo ya fitta dagga chikkin kaya, gurugu ya fitta dagga kogon kuka. Da suka fitta, sai suka che su koma sai su samu sosai. Sai makafo ya komo achikkin kaya, sai gurugu kuwa ya koma kogon itache. Da sun koma, sai kaffan gurugu ta dada gurumadewa. Shi makafo da ya koma, sai ido ya dada dakilewa. Shi ke nan, sai gurugu ya mutu achikkin kogon kuka, makafo ya mutu achikkin kaya.

Allah ya ba su sauken abin, ba su gode ba, sai suka che su je su wari wari sarai.

---

## 92

### The Man and his Wives who were Witches.

Wanni mutum ya aure matanshi uku, dukansu na dabbo. Daya dabbonta ba na chin mutum ba ne, biyu suna da dabbo na irin chin mutum.

Su kan taffi daji, suna rawan dabbo da makaddinsu, suna rawa, shi shina yi masu waka, ya che "Uwar-Gida, ba ki iya rawan turu ba?" Sai ta che rawan turu ya gagara, har ta baida mijinta wurin rawan turu. Sai makadin ya che "Mai-biya da Uwar-Gida ba ki iya rawan turu ba?" Sai ta che rawan turu ya gagara har ta baida mijinta wurin rawan turu. Sai makaddin ya che "Amariya ba ki iya rawan turu ba?" Sai ta che rawan turu ya gagara har ta baida zanne wurin rawan turu.

Sai makaddi ya taffi, sai ya kirra mijin, wai zaya nadi shi a tabarima. Ya che shi zona anan, shi ji abinda matanshi zasu gaya. Sai mijin shina zone achikkin tabarima, makaddi ya zo ya dauke ganga, shina kiddi, kiddin rawan turu. Sai mata biyu suka che zasu kama mijinsu, su ba masu-rawan dabbo. Sai miji ya tashi ya gudu. Da ya gudu sai ya kama matanshi daya ya kasshe. Ya zo kuma ya kama daya ya kai bissa itache, ya daura. Sai ya bar daya, ita che wanda ta che ta baida zannenta wurin rawan dabbo.

Sai suka yi zammansu da mijinta, sai dabbo ya kare ke nan

## 93

### How the Ill-treated Maiden became Rich.

Wanni mutum shina da mata biyu, suka haife yaya, duka mata, kowache ta haife yariniya. Sai uwar daya ta mutu, uwan, sai uban ya che ma wanchan "To, ga uwar wannan ta mutu," ya che "sai ki rikke su duka, da naki da nata." Ta che "To, na rikke su."

Sai suna nan, sai yam-mata sun yi girima. Sai tana dukan wadda ba yanta ba. Sai uban ya zo yana mata fada. Sai ta che "To, saboda ita kana yi mani fada, sai en kai ta inda za'achainye ta."

Akwai wanni rafi, wai shi Rafin Bagajun, kowa ya taffi awurin sai mainya ta chainye ta. Ta che yariniya ta yi fisari a kirigi, sai ta taffi Rafin Bagajun ta wanke shi. Tana taffiya achikkin dauji, ita yariniya, sai ta ga kogin nono yana gudu achikkin dauji. Sai kogin nono ya che "Ke Yar-Mata, zo ki debe ni ki sha." Sai ta che "A, a, enna anfani?" Sai ta wuche. Sai ta iske kogin zuma, sai zuma ya che "Ke, Yar-Mata, sai ki zo ki debe ni, ki sha?" Sai ta che "A, a, enna anfani?" Sai ta wuche. Sai ta iske kaji suna daffa kansu. Sa ta zo sai kaji suka che "Ke, Yar-Mata, ga shi, muna daffa kammu, sai ki zo ki debe daya ki che." Sai ta che "A, a, enna anfani?" Sai ta wuche.

Sai ta yi kussa ga Rafin Bagajun, sai ta tsaya ta makye da itache, tana kalon wota mache achikkin rafi, tana wanka. Duka jikkinta baki ne, baki suna chewa "Nan kin ba ni, nan ba kin ba ni ba."

Sai yariniya ta fitto fili. Da ta fitto, sai mache ta mare jikkinta da hanu biyu, sai bakinta ya koma daya kaman na kowa. Sai ta che "Marhaba Yar-Mata." Sai ta che "Mi ya kawo ki Rafin Bagajun yau." Ta che "Don na yi fisari a kirigi akache en zo en wanke shi a rafin nan." Sai ta che "To, sai ki zo ki chuda ni." Sai ta zo, tana chude ta a baya, sai baya ya burime. Sai ta tsaya shiru, ita yariniya. Sai ta che "Minene?" Yariniya ta che "Baya ya burime." Ta che "Mi ki ke gani ackikki?" Ta che "Dan kwotache kankani." Sai ta che "Danko," ta che "je ki na ba ki." Ta che "En kin taffi kin che 'Apassa nan?' en kin ji 'apassa mu raba' kadda apassa."

Sai ta taffi, tana taffiya, sai ta che "Apassa nan?" Ta ji "Passa mu raba," sai ta wuche. Da ta yi taffiya da nisa ta che "Em passa nan?"—Shiru. "Em passa nan?"—Shiru. Sai

ta passa. Sai dukiya suka fitto, da shanu, da bayi, da rakumi, da awaki, da dowaki. Sai ta aike garinsu wurin ubanta, ta che kadda shi ji tsoro shi gudu, ita ne ta dawo dagga Rafin Bagajun.

Da ta zo, da kishiyan uwanta ta gani, haushi ya kama ta. Sai ta che wa yanta "Ki yi fisari, ki taffi Rafin Bagajun." Tana taffiya, tana taffiya, tana taffiya, sai ta iske kogon nono. Kogon nono ya che "Ke, Yar-Mata, ki debo ki sha." Ita ta che "Ka chikka gigiwa, sai ka che en debe ka?" Sai ta debo ta sha, ta chikka chikkinta, ta wuche. Ta iske kogon zuma, sai kogon zuma ya che "Ke, Yar-Mata, ki zo ki debe ni, ki sha." Sai ta che "Ka chikka gigiwa, sai ka che en debe ka?" Sai ta debo ta sha, ta chikka chikkinta, ta wuche. Sai ta zo ta iske kaji suna daffa kansu. Sai suka che "Ke, Yar-Mata, ki zo ki debe daya ki chi." Sai ta debo ta chi, sai ta wuche.

Sai ta zo Rafin Bagajun, ta ga tsofuwa achikki, tana wanka, bakuna suna chewa "Nan kin ba ni, nan ba kin ba ni ba." Sai ta fitto bup. Sai mata ta buga jikkinta, sai baki ya koma daya. Sai mata ta che "Kin gan ni?" Sai ta che "Op, na gan ki manna, da baki kaman dubu." Sai ta che "Mi ya kawo ki Rafin Bagajun? Sai ta che "Op, na zo wankan kirigi." Sai ta che "Ki zo ki chuda ni." Sai ta che "Gasa, ni na zo wankan kirigi." Sai ta che "Zo de." Sai ta che "To." Da ta zo ta chuda, baya ya fuji. Sai ta che "To, gigiwan ke nan, na che ba ni chuda ki." Ta che "Mi kin gani?" Ta che "Mi zan gani banda dan kwotache?" Sai ta che "Dauko, na ba ki." Ta che "En kin taffi, kina taffiya kin che 'Em passa?' in kin ji 'Passa mu raba,' ki wuche." Sai ta che "Gasa, en na ji 'passa mu raba,' zan passa."

Da ta taffi, ta che "Em passa?" Ta ji "Passa mu raba." Sai ta passa. Sai kutari suka fitto kaman dubu, da gurugu, kaman dubu, da geyambu, da makafi. Sai ta iza su su taffi gari. Sai uban ya ji labari, ya che kadda ta tako gari, ta zona chan daji da iyalinta masu-wari.

---

## 94

### Dan-Kuchingaya and the Witch.

Waddanan yara ne su uku, daya yaro sunansa Dan-Kuchingaya da yan-uwanshi su biyu. Shi ke nan, sai suna neman yan-mata, yan-mata kuma yayan maiya ne. Su kuma ba su sani yayan maiya ne, sai yara suka taffi gidan yan-mata.

Da suka je, sai akayi masu abinchi, sai yara suka fitta zasu yawo su mazza. Sai suka tarada maiya tana sasauke kainiyar yanta tana duban kwarikwata. Shi ke nan, sai yara suka zo, suka che "Salla'am aleikum." Sai suka che "Aleikum salla'am." Sai shi ke nan, sai maiya ta mayar da kain yar. Shi ke nan, sai da ta mayar, sai yara suka zo suka zona. Shi ke nan, sai da dare ya yi akakawo wa yara wanni abinchi, suka chi.

Sai dare ya yi, sai maiya ta kasa barchi, sai ta dauke wuka, tana wasawa. Shi ke nan, sai yaro, Dan-Kuchingaya, sai ya chiri maman yayanta, ya sa wa yeyenshi. Shi ke nan sai maiya tana wasawa wuka, da tana wasawa sai ta taffo zata yanka yara. Sai Dan-Kuchingaya ya yi tari, ya che "Um." Sai ta che "Yaro, mi ka ke so?" Sai ya che "A, a, ina so kwai, zan yi wanni abu." Shi ke nan, sai maiya ta taffi ta kawo mashi. Sai ta taffi ta kwanta. Sai ya zo, shi Dan-Kuchingaya, ya kunche zannuwan yayan maiya, sai ya daura wa yan-uwanshi. Shi ke nan, sai ya kunche banten yan-uwanshi sai ya daura ma yayan maiya.

Da ya sa, ya kwanta, sai maiya ta zo. In ta lalaba ta ji mai-bante, sai ta yanka. Duk ta yanka yayanta. Da ta yanka sai ta koma, ta kwanta abinta. Shi ke nan, sai yaro ya yi rami a daki, ya yi rami har garinsu. Sai ya tashi yeyenshi, sài suka taffi. Sai shi Dan-Kuchingaya kadai ya zona achikkin gidan maiya.

Sai gari ya waye sai maiya ta zo, ta che "Ku Yaya, ku tashi, ga gari ya waye." Sai Dan-Kuchingaya ya fara fitto dagga daki, sai ya che "Ni ne Dan-Kuchingaya, na kuta maki aiki nawa." Sai ta je ta tarada yayanta duk ta yanke. Shi ke nan, sai maiya ta che "Ni ma na rama abinda ka yi mani." Sai yaro ya taffi gida, sai ya je ya gaya wa yeyenshi. Shi ke nan, sai ya che "Ku, in kun ga wata mache ta zo karuwa, kadda ku neme ta."

Sai maiya ta taso, ta zamma karuwa. Sai ta zo ranan kasuwa ta chi. Shi ke nan, sai wan Dan-Kuchingaya ya gan ta. Ita ta sa alura arabain a hanu. Sai wan Dan-Kuchingaya ya gan ta ya che yana son ta. Shi ke nan, sai ta che "To." Sai Dan-Kuchingaya ya zo ya gan ta, sai ya kirra wan woje daya, ya che "Kadda ka nema matan nan." Sai ya zage yaro. Sai ya che "To je ka, ka nema." Sai ya kirra mache woje daya, suna zanche, shi ke nan, sai mazza, sai ta chiri ido, ta taffi. Shi ke nan, sai Dan-Kuchingaya ya che "A, abinda ni ke gaya ma, kadda ka neme ta." Shi ke nan, sai ya che "To, bar en taffi en karbo maka idonka." Sai ya che "To."

Sai Dan-Kuchingaya ya rikidda, ya zammi mache Ba-Filata. Sai ya dauke nono. Ba ya tashi tala ba sai kofar gidan maiya. Sai shi ke nan, sai maiya ta che "kawo." Sai ya kawo, sai ta saya. Sai ya tambaya ta, ya che "Ba ki san maganin chiwun ido ba?" Sai ya che "Dan-Kuchingaya, wanni mugun yaro, ya je ya chiri mani idanu na shanu." Sai ta che "To, je ki, ki neme idon bakar akwiya, en kin nema sai em ba ki wanni kitsi, ki je ki gamma da ido, sai ki ga idon shanu sun komo." Sai ya che "To."

Shi ke nan, sai Dan-Kuchingaya ya tashi. Sai da ya kai wojen chan da nisa, sai ya rikidda namiji, sai ya che "Ni ne Dan-Kuchingaya," sai ya che "idon wana da kika chiri, shi ne na zo na tambaya." Sai ta che "Ka je ka nemi barkono ka sa." Sai ya che "Op, ai na ji ko!" Shi ke nan, sai ya je, suka saye bakar akwiya, sai suka yanka, sai suka sa idanu achikkin idon wan. Sai shi ke nan, sai ido ya komo.

---

## 95

### The Boy, the Witch, and the Wonderful Horse.

Wanni mahalbe yana halbinshi, yana halbe, yana halbe, har ya haife dan, shi kuwa mahalbe. Sai dan ya taffi chan daukan daji, ya ga buka, ya che "Sai na ga mai-buka," sai ya hau bissa itache. Da ya hau bissa, yana zone, sai zuwa chan mata ta fitto dagga buka. Da ta fitto ta kawo katon randa, ta girika. Da ta girika, tukuniya ta tosa, ta fitto da buriman acha, sai ta ruda, ta ruda, sai ta kwashe. Ta mamare jikkinta, sai zuwa chan jikki duk ya zamma baki. Sai ta kwashe tuwon tana ba bakuna, suna chi. Sai wannan baki ya che "Iya, ba ki ba ni ba?" Sai zuwa chan tuwon duk ya kare, duk da kamzo. Sai ta buga jikkinta, bakuna sun komo daya. Ta kwashe tukuniyan tuwo, ta shiga da shi buka. Sai zuwa chan ta fitto da tabarima, ta shimfida a gindin itache wanda yaro ya ke bissa gare shi, sai ta kwanta.

Sai yaro yana zone chan, ya sinke gainye, ya jefa mata. Sai ta che "Ya Allah, tun de mu ke da itachenkai, gainyenshi ba ya tabba fadi ba. Minene ya samu gainyen?" Sai ta gadda idanu ta ga yaro. Sai ta che da yaron "Sauka." Sai yaro ya sauka. Sai ta che "Yaro, ka gan ni?" Sai ya che "Ban gan ki ba, Iya." Sai yaro ya soma taffiya, sai ta che "Komo."

Ya komo. Ta che "Yaro, ka ganni?" Sai ya che "Ban gan ki ba, Iya." Sai ta che "Taffi." Yaro ya zo kofan garinou sai ya sa kafo, sai ya yi busa. Da ya yi busa, ya che "Yau na ga mache da bakuna, wannan ina che 'kin ba ni,' wannan na che 'Ba kin ba ni ba.'"

Sai matan ta ji chana, da ta ji chana sai ta chiji hanu, wai yaro ya taffi ya falasa ta achikkin gari. Sai mache ta yi shiri dagga chana, ta zamma mache kekeyauwa da gaski. Da ta zamma kekeyauwa ta zo kofan sariki. Sariki ya che ina son ta da aure. Sai ta kawo dan lefenta, ta aje a kofan sariki. Ta che wanda ya halbe lefe ya bude, shi ne mijinta. Sariki ina halben lefe, sariki ya halbe lefe ba ya bude ba, sai ya ba madaki wuri shi yi. Madaki ya halbe lefe ba ya bude ba. Akaba fadawa wuri su yi, fadawa sun yi ba ya bude ba.

Yaron kuma, mahalbe, shina dauji. Sai abokinshi ya tashi zashi gida. Da ya tashi zashi gida sai ya gammu da shi, yaro, ya komo dauji. Sai ya che "Zo mu taffi ka yi halben lefe." Ya che "Na mine?" Ya che "Na wota mache ne, kekeyauwa da ita" Sai ya che "Sariki ba ya halbe ba?" Sai ya che "Ya yi." Sai ya che "Da ya yi ba ya samu ba?" Sai ya che shi sariki ya yi ba ya samu ba, shi ne zashi ya samu. Sai aboki ya che "Mu taffi, ka shina ne?"

Sai suka taffi. Da sun taffi yaron ya dauke dan dutsi kankani, ya jefa. Da ya jefa sai lefen ya bude. Sai ta che ashe ta samu miji. Akadaura masu aure. Yaro ya taffi ya bar dakin da da shina kwana achikki, sai suna zone da matan. Sai ya ki mata wachanchana, yana son sabuwa. Sai uban ya che ma wachanchana ta zona kawai. Sai suna zona da yaro.

Sai ran nan ta che zata garinsu. Da da dare suna tadi. Har ta che "Ku kan taffi halbe da magani ne?" Sai ya che "Um." Sai shina gaya mata, sai uban ya zage shi. Da ya zage shi sai ya yi shiru. Sai safi ya yi ya tashi zaya daura ma dokinshi sirdi. Sai mata ta che "Zaka taffi ka kasshe ni a dauji da doki?" Sai ya bar dokin. Sai ya dauke takobi. Sai ta che "Zaka taffi ka sare ni a dauji?" Sai yaro ya koma ya aje takobin. Ya kwashe gurayenshi. Ta che "Zaka taffi ka yi mani magani ne a dauji?" Sai ya barri kayanshi duk a gida. Sai zashi kana. Sai uban ya yi mashi fada, sai ya che "Kwashe kayan dakinka duk ka taffi da shi," sai ya kwashe. Sai uban ya che "Dokinka ya che zaya bi ka daji." Sai ya che "To, zan sa mashi sirdi." Sai ya sa mashi, ya hau, sai ya sa ta gabba, suna taffiya.

Sai ta che ma yaron "Ka san wurinkai?" Ya che "Na shina

manna, muna yawon halbe." Suka taffi bukanta, sai ta che "Ka san bukankai?" Sai ya che ya shina. Sai ta che "Ka ga mine achikki?" Sai ya che ya ga mache ne mai-bakuna. Ta che "To." Sai suna taffiya, suna taffiya, suna taffiya, suka yi taffiya kwana shida. Sai ta che "Ka san wurinkai?" Sai ya che ba ya shina ba. Suna taffiya, suna taffiya kuma, suka yi taffiya kwana goma, sai ran nan suka sauka a garin.

Da suka sauka sai ta yi dabbonta, sai ta samu tuwo ta kawo ma yaro, ya chi. Da dare ya yi ta wasa hakorinta zata shiga ta chi yaro. Sai dokin yaro ya yi magana, sai yaro ya che "Wanene nana?" Ta che "Ni ne." Sai yaro ya che "Mine ya kawo ki?" Sai ta che "Ina che ko wutanka ya mutu ne." Sai yaro ya che "A, a, taffi abinki." Sai ta fitta. Da ta fitta ta taffi dakinta.

Kwana uku yaro yana garin, ba kowa a garin sai su. Sai yaro ya che ma dokinshi "Safi ya yi kadda ka chi chiyawa ba." Doki gari ya waye ba ya chi chiyawa ba. Sai ta che "Mine ya samu dokinka?" Sai ya che "Chikki ya yi ma doki chiwu." Sai ta che "Minene maganinshi?" Sai yaro ya che "Kwandonda akedebo ruwa da shi, en de ya sha, chikkinsa ya warike." Sai ta dauke kwando, ta taffi rafi. Yaro ya sa ma dokinshi sirdi, ya hau, sai shina gudu.

Sai matan ta yi, ta yi ta dibar ruwa, ruwa ya ki tsayawa a kwando. Sai ta yi dabbonta tukuna, sa'anan ruwa ya tsaya a kwando. Ta zo gida ba ta ga yaro ba, sai ta yarda ruwa, sai ta kama hainya ta bi yaro. Sai ta hangye yaro chana, sai ta che "Alli sauraye da woba, bantenka na gadona, rawaninka na gadona." Sai yaro ya wega, ya che "Na barri maki taushi." Sai ta che "Taushin tsoro ne." Sai ta taffi zata kama sawun doki, sai wutsiyan doki ya zamma aska, ya yanke ta a hanu. Sai ta zona tana lashe jini.

Sai ta tashi, tana bin sa kuma, sai ta che "Alli sauraye da woba, bantenka na gadona, rawaninka na gadona." Sai ya wega, ya che "Na barri maki taushi." Sai ta che "Taushin tsoro ne." Sai ta taffi, ta kama sawun doki daya. Sai yaro ya ji tsoro, sai ya che "Habba dokina," ya che "Kai ni gida, ba kussa ba," doki ya che "Ko da kaffa daya sai en kai ka garimmu." Sai doki ya che zaya kai shi ba don rainsa ba. Sai mache ta tashi, tana bin su kuma, ta che "Alli sauraye da woba, bantenka na gadona, rawaninka na gadona." Sai ya wega, ya che "Na barri maki taushi." Sai ta che "Taushin tsoro ne." Sai ta taffi, ta kama sawun doki daya. Sai yaro ya ji tsoro, sai ya che "Habba dokina; Dan Lele." Sai ya che

"Kai ni gida, ba kussa ba," doki ya che "Ko da kaffa daya sai en kai ka garimmu." Sai doki ya che zaya kai shi ba don rainsa ba.

Suka zo kofan garinsu. Sai matan ta kama sawun doki kuma, doki ya mutu. Uban kuma ya shina sarai, sai suka bude karnuka a daki, sai suka bi bayansu, suka zo, suka kore matan. Dakar ne ta tsere. Uban ya che "Abar, don gobe akara." Sai zuwa chan yaro ya sauka abissa, sai ya kama turaban gida. Ya taffi ya saye fari. Akazo akarufe dokin da shi, akakai rami.

Sai suka zo suka kwana biyu. Sai matan ta zamma fure bakin chariki, sai mata suna taffiya, suna diba. Sai abokinshi ya, zo wurinshi kuma, sai yaro ya che "Matan nan ne." Sai abokin yaro ya che "Kai de, ka ji tsoron matan nan ne?" Sai ya che "To, mu taffi." Sai sun taffi. Yaron ba ya shiga wurin furen ba. Sai da suka koma gida, sai ya che "Na che maka matan nan ne." Kaman safi, antaffi annemi fure a rafi, anrassa. Sai ya che ma abokinsa. "Ai, na gaya ma."

Kaman kwana biyu ne, sai ta zamma doki. Sai ta che zata kasshe yaro. Samari sai suka taffi kaman doki su hau, suka yi sukuwa. Sai abokin yaro ya zo wurinshi, ya che su taffi su kama doki, su hau. Sai yaron ya ki, sai ya che "Matan nan ne." Sai aboki ya che "Kai de, ka ji tsoron matanka ne?" Sai ya che "Mu taffi." Sai sun taffi wurin doki. Abokin ya kama ya hau. Da ya hau ya yi sukuwanshi, ya taffi, ya komo da shi. Sai shi wannan yaro ya hau. Da ya hau, shina sukuwa, sai ta zamma iska zata taffi da yaro. Sai yaro ya samu wanni rashin itache, ya kama. Da ya kama, ita matan ta taffi. Sai yaron ya sauka bissa itachen. Sai ya zo wurin aboki, sai ya che "Ai na gaya maka matan nan ne." Sai ya che "I, gaskiya ne." Sai suka komo gida.

Sai mata ta zo, ta rikidda takobi, ba kamanshi duk garin. Sai samari suna zuwa, suna daka. Sai abokinshi ya zo wurinshi kuma. Da ya zo, ya che sai su taffi wurin takobi. Sai yaro ya che "Matan nan ne." Sai aboki ya che "Kai de, kana tsoron matanka ne?" Sai yaro ya che "To, mu taffi." Suka tashi suna taffiya, sai ya kirra karnukanshi. Da zuwanshi, sai ya sare wannan takobi da nashi, ya che barri ya gwoda kaifinshi da nashi. Sai ya sara, sai ya ga matan nan ne. Sai karnukanshi suka bi, suka chi nama. In de dan jini ya sauka a chiyawa sai ya che su chainye. Sai duk karnuka suka bi, suka lashi jini.

96

## The Boy who cheated Death.

Wanni ke nan mai-kurdi da gaski, duk gari ya fi kowa dukiya. Yana da da. Sarikin gari kuwa yana da da. Sai Dan Sariki ya che yana son Dan Mai-Kurdin nan aboki. To, abokin nan da su ke yi kuwa, Dan Sariki ba ya chikka son Dan Mai-Kurdin. Shi kuwa, Dan Mai-Dukiya ba ya chikka son Dan Sariki. Shi, Dan Sariki shina son abuta da shi saboda dukiyan ubanshi. Shi kuma, Dan Mai-Kurdi, yana abuta da shi saboda shi dan sarikin garinsu.

Akwai wanni gari Mutuwa tana nan duk da yayanta. Kowa ya taffi gidan ba ya komowa. Shi Dan Sariki ya che ma Dan Mai-Kurdin nan "To, kana alfarma ubanka yana da kurdi," ya che "To, ka je gidan Mutuwa ka chi tuwonta ka kawo mani saura."

Sai Dan Mai-Kurdi ya gaya ma ubanshi, ya che "To, ka ga abinda Dan Sariki, ya gaya mani muna achikkin wasa, gabban mata, gabban mutane. Ya che ubana yana da kurdi sai en je en chi tuwon Mutuwa en kawo masa saura." Sai uban ya che "To, em ba ka bawa goma sha biyu ka taffi da su, kafin ta kasshe su ka gudu ka tsere." Sai ya che "A, a, ni ma, adaura mani sirdi a dokina en taffi." Sai akadaura mashi sirdi a doki, sai ya taffi.

Yana taffiya, yana taffiya, yana taffiya, sai ya iske wanni yana sasaka kujira. Sai ya che "Dan Mai-Kurdi, enna zaka?" Ya che "Zani gidan Mutuwa ne." Ya che "Barri em ba ka kujira guda daya ta yi maka rana." Sai ya karba, ya taffi.

Yana taffiya, yana taffiya, yana taffiya, sai ya iske makeri. Sai ya che "Dan Mai-Kurdi, enna zaka?" Ya che "Zani gidan Mutuwa ne." Ya che "Barri em ba ka masaba ta yi maka rana." Sa ya karba, ya taffi.

Yanna taffiya, yana taffiya, yana taffiya, sai ya iske mata tana itache. Sai ta che "Dan Mai-Kurdi, enna zaka?" Sai ya che "Zani gidan Mutuwa ne." Sai ta che "Barri em ba ka kayan itache guda daya, ya yi maka rana." Sai ya karba, duka ya sa bayan doki.

Sai ya je ya iske yayan Mutuwa suna noma. Sai suka che "A Dan Mai-Kurdi, marhaba, marhaba." Sai ya che "Enna Mutuwa?" Sai suka che "Ai, tana gida." Sai ya zo, ya sallama. Da ya sallama, Mutuwa ta fitto, ta che "A Dan Mai-Kurdi, marhaba." Sai ta che ma yayanta "Ku daffa ma Dan Mai-Kurdi shinkafa, ku yi mashi tuwo." Suka daffa shi, suka

yi tuwo. Sai ta che "To, ku ba shi ya chi, zani rafi wurin mijina."

Da yaran suka ba Dan Mai-Kurdi tuwo, da ya chi ya koshi, sauran ya zuba a zabira. Sai ya sa dokinshi kaimi, ya gudu. Sai Mutuwa ta zo, ta tambaya yayan "Enna Dan Mai-Kurdi ya ke?" Sai suka che "A, ya taffi ko." Ta che "Kariya ne, wanda ya zo gidana ya koma?"

Sai ta bi shi da gudu, ta bi shi da gudu, ta bi shi da gudu. Da ta yi kussa zata kama wuchiyan doki, sai ya sake kujira, ta zamma baban itache ta kare hainya. Sai ta koma gida ta dauke gatari, ta zo ta yi ta sara, ta yi ta sara, ta yi ta sara. Kafin ta sare Dan Mai-Kurdi ya yi nesa.

Da ta sare, sai ta yarda gatari awurin, sai ta gudu, ta bi Dan Mai-Kurdi. Da ta kussa kaman wuchiya, sai ya sake masaba, ya kare hainya. Mutuwa ta che "To, barri en dauko dundurusu en gina, en tuge, en yas."

Sai da ta tuge, Dan Mai-Kurdi ya yi nesa. Sai ta gudu, ta bi shi. Da zata kama wuchiyan doki sai ya sake itache, ya kare hainya. Sai ta che "To, barri en koma wurinda na yarda gatari."

Kafin ta koma, ta sare, Dan Mai-Kurdi ya kai kofan garinsu. Da ta sare, ta yi gudu, ta zo ta kussa iske shi. Ta tsaya, ta che "Dan Mai-Kurdi kana da arziki, ba zaka mutu ba sai Allah ya kasshe ka tun da ka zo gidana ka koma."

Dan Mai-Kurdi da ya koma, ya je wurin Dan Sariki, ya che "Ga tuwon Mutuwa na rage maka." Sai Dan Sariki ya che "A, kariya ne, ka yi mata wayo, en gaskiya ne sai ka zo ka je gidan rago." Achikkin gidan rago, wanda ya zo yau akan yanke masa wanda ya zo jiya. Shi kuwa za'ayanke saboda mai-zuwa gobe.

Sai Dan Mai-Kurdi ya je, ya gaya ma ubanshi, ya che "Ka ji abinda Dan Sariki ya che, ya che en je gidan rago." Sai uban ya che "To, barri em ba ka bawa goma sha biyu ka taffi da su, kafin rago ya chi su ka gudu ka tsere." Sai ya che "A, a, ni ma, adaura mani sirdi a dokina en taffi."

Sai ya taffi gidan rago, sai ya sallama. Sai rago ya che "A Dan Mai-Kurdi, marhaba." Dan Mai-Kurdi ya sauka, sai akayanka bako wanda ya zo jiya. Da akayanka, akayi miya, Dan Mai-Kurdi da dokinshi suna chikkin gidan rago. Da akagamma tuwo, akachi, sai matan rago ta bude masa kofan bayan gida, sai ya gudu abinshi. Rago kuma yana zaure, ba ya san Dan Mai-Kurdi ya gudu.

Lokachin nan kuma wanni ya zo, ya sallama. Da ya

sallama, ya che "Marhaba, marhaba." Da ya yi mashi marhaba, ya shiga gida, ya che "Enna Dan Mai-Kurdi?" Yana so ya yanka shi ya ba bako. Sai mata suka che "Op, mu, ba mun ga Dan Mai-Kurdi ba, ya gudu." Sai ya che "Kariya ne, zan bi shi." Sai ya bi shi, yana che "Dan Mai-Kurdi tsaya nan." Sai ya che "A, a, ni ba zan tsaya ba, ka zo da gudu en ka iya ka kama ni." Sai ya bi shi, yana gudu, yana gudu, sai Dan Mai-Kurdi ya tsira. Da ya tsira ya zo kofan gidansa, sai Rago ya che "Dan Mai-Kurdi kana da arziki, ba zaka mutu ba sai Allah ya kasshe ka."

Da ya shiga garin ya je wurin Dan Sariki, ya che "To, na taffi gidan Rago." Sai Dan Sariki ya che "Kariya ne, gobe ka hau doki da ka ke so, ni kuma zan hau doki da ni ke so, muwa yi sukuwa a kofar Fada, kofan ubana."

Da gari ya waye, sai Dan Mai-Kurdi ya che ma uban "Ka ji abinda Dan Sariki ya che, ya che gobe en hau doki da ni ke so, shi kuwa ya hau doki da ya ke so, mu yi sukuwa a kofar Fada, kofan ubanshi." Sai Dan Sariki ya hau doki na bawa goma, Dan Mai-Kurdi ya hau doki na bawa ashirin. Da suka je fage, a kofar Fada, sai Dan Sariki ya che "Dan Mai-Kurdi ka fara yin sukuwa." Dan Mai-Kurdi ya che "A, a, kai ka fara yi, ai kofan ubanka ne." Sai Dan Sariki ya fara yin sukuwa. Da ya yi sukuwa, ya komo da dokinshi, ya che "To, na yi, kuma ka yi." Ya che to, ya yi. Da ya komo, yana komowa wurin Dan Sariki, sai dokin Dan Mai-Kurdi ya yi haniniya. Da ya yi haniniya kuwa Dan Sariki da dokinsa sun bata, haniniya ta taffi da su. Ba wanda ya sani wurinda suka taffi, da shi da dokinshi.

Sai Dan Mai-Kurdi ya je wurin ubanshi, ya che "To, mun yi sukuwa da Dan Sariki, amma ya bata, ni ban gan shi ba."

Sai Sariki ya yi ta kuka danshi ya bata.

---

## 97

### The King with the Cannibal Taste.

Sariki ke nan, shina nan. Ana tuwo a gidanshi sai shiruwa ta dauke naman mutum. Da tana wuchewa abissa, sai nama ya kubche, ya fadi achikkin miya, uwar miya (1) ba ta gani ba. Sai akakwashe tuwo, akasa ma sariki, sai akasa mashi miya. Sai akadauke naman nan akasa mashi, ya chi.

Sai ya chi nama, ba ya tabba jin zakin nama kamanshi ba. Ashe naman mutum ne, shi ba ya shina ba, yana so akara masa.

Ya sa akayanke akwiya, ba ya ji zakin nama kaman wannan ba. Sai ya sa akakama sa akayanka, ba ya ji zakin nama kaman wannan ba. Sai ya sa akataffi akakama naman daji duk, akakawo mashi, ya chi, ba ya ji zakin nama kaman wannan ba.

Sai ya sa akakama bawanshi, ya yanka, ya chi. Sa'anan ya ji zaki kaman na wannan. Sai ya rikka kaman mutanen gidanshi, shina yanka, sai mutanen gidansa duk ya kare. Sai mutanen gari duk suka gudu, suka bar shi, shi kakai. En 'ya ji kwadayen nama sai ya debe naman jikkinshi ya chi, har jikkinshi ya zamma kasshi. En shina gudu ka ji kasshin suna "gwarrang, gwarrang."

Sai ya taffi turaba bukan fatake, ya kwanta, yana so ya yi masu passhe. Sai da zuwansu sai ya bi wanni da gudu zashi ya kama shi, ya zo ya chi nama. Ya taffi ya kama shi, ya kasshe, sa'anan ya che zashi dauke nama. Sai ya fadi, ya kasa daukan nama, ya mutu. Shi ke nan.

(1) Mother of the soup, *i.e.*, the cook.

---

## 98

### The Many Headed Cannibals.

Girringa ke nan, masu-chin mutum masu-yawan kai. Wanni girringa, mai-kai biyu, ya taffi wanni gari ya yi aure. Sai suna zuwa da matan, da shi da ita, suka gammu da mai-kai uku. Sai ya che. "Mahabbi Girringa." Sai wanchan ya che "Um, um, Girringa." Ya che "Mahabbi Girringa." Sai wanchan ya che "Um, um, Girringa." Sai ya che "Ka fitta angani?" Ya che "Na fitto a Kano." Sai ya che "Ka taffi neman mene, Girringa,?" Ya che "Neman mata Girringa." Sai ya che "Mata tana angani?" en ji mai-kai uku. Ya che "Ga ta a baya." Sai ya che "Tana kukan mene?" ta che "Tana kukan kai." Sai ya che "Magaji ba ya tuku zuwa ba."

Sai suka wuche, suka taffi suka gammu da mai-kai fudu. Sai ya che "Mahabbi Girringa." Sai wanchan ya che "Um, um, Girringa." Ya che "Mahabbi Girringa." Sai wanchan ya che "Um, um, Girringa." Sai ya che "Ka fitta angani?" Ya che "Na fitto a Kano." Sai ya che "Ka taffi neman mene, Girringa?" Ya che "Neman mata Girringa." Sai ya che "Mata tana angani?" en ji mai-kai fudu. Ya che "Ga ta a baya." Sai ya che "Tana kukan mene?" Ya che "Tana kukan kai." Sai ya che "Magaji ba ya tuku zuwa ba."

Sai suka taffi, suna taffiya sai suka gammu da mai-kai biyal. Sai ya che "Mahabbi Girringa." Sai wanchan ya che "Um, um, Girringa." Ya che "Mahabbi Girringa." Sai wanchan ya che "Um, um, Girringa." Sai ya che "Ka fitta angani?" Ya che "Na fitto a Kano." Sai ya che "Ka taffi neman mene, Girringa?" Ta che "Neman mata Girringa." Sai ya che "Mata tana angani?" en ji mai-kai biyal. Ya che "Ga ta a baya." Sai ya che "Tana kukan mene?" Ya che "Tana kukan kai." Sai ya che "Magaji ba ya tuku zuwa ba."

Sai suka zo gari, suka zo gidan magaji, mai-kai goma. Ya che "Mahabbi Girringa." Sai wanchan ya che "Um, um, Girringa." Ya che "Mahahbi Girringa." Sai wanchan ya che "Um, um, Girringa." Sai ya che "Ka fitta angani?" Ya che "Na fitto a Kano." Sai ya che "Ka taffi neman mene Girringa?" Ya che "Neman mata Girringa." Sai ya che "Mata tana angani?" en ji mai-kai goma. Ya che "Ga ta a baya." Sai ya che "Tana kukan mene?" Ya che "Tana kukan kai."

Akaba ta daki, ta ki shiga, tana kuka. Anayi da ita, anayi da ita har ta shiga. Sun taffi sun yanke mata awaki, akwiya uku, ta chi ta koshi.

Tana nan, tana nan suna kiwonta har ta yi kibba. Randa zasu yanke ta suka ba ta tukuniya ta dauko ruwa su wanke ta. Ta taffi rafi ta ji tsoro gamma ba suka yarda ta fitta woje ba. Da ta taffi rafi sai ta rikidda ta zamma kututuri.

Da ta dadi ba ta komo ba, wanni garringa ya taffi bim baya, ba ya gan ta ba. Sai ya komo da baya, sai ya zo ya gaya masu ta gudu. Sai suka che "To, sai mu hakuri." Suka zona abinsu. Da da dare ta komo mache ta taffi garinsu.

---

## 99

### Why the Young Giant lost his Strength.

Wanni sauraye ne kato, mai-tsawo kaman dagga nan zuwa Kano ko zuwa Bauchi, duk babu kamansa. Shi kuwa, mallami ya ba shi laya, ya che kadda ya chi mache. En kato ya fitta ko dagga enna, en de ya zo sai ya kasshe shi da dambe.

Da kuma wota yariniya, buduruwa, tana kaman Sokoto, mazza su kan tashi kaman Damaghera, su kan taffi kalon yariniya sabilida keyauwunta. Kaman Sarikin Damaghera ya che ina son ta sai ta che ba ta so. Kaman Sarikin Zango (Mallam Yarro), ya je gunta sai ta che ba ta so.

Sai ta jiwo labarin yaron nan, sai ta che ita sai ta je wurin yaron nan. Sai ta tashi, ta fara taffiya, ta yi wata biyu tana taffiya. Sai ta zo wurin yaro, sai yaro da ya gan ta yaro ya che ina son ta. Sai ya dauke ta, ya kai ta dakinsa. Tana nan tana zone, suna tsaranchi. Lokachin nan, sai ran nan, shi yaron nan, sai yana so ya chi ta. Sai ya chi ta ran nan. Da ya chi ta sai da washen gari akakaffa wasa dayawa. Shi ke nan, sai saurayen nan sai ya fitto ya yi tsawa. Sai wanni kuma ya fitta dagga wanni wuri, shi kuma ya yi tsawa. Sai suku zo, suka hadu. Da ya ja hanunsa, da ya duba hamatansa, da ya duke shi, ya kasshe shi, ya mutu.

Lokachinda suka gani sai suka zo, suka che "Yariniya, ga wanda kin zo wurinsa ga shi akakasshe shi awurin wasa?" Lokachin nan sai yariniya ta che "Enna maganin abin nan?" Lokachin nan sai akache da akwai maganinsa. Lokachin nan yariniya, akatone rami, akache en de ta zo ta shiga ramin nan, en akabirne ta achikki, yaron nan sai ya tashi. Shi ke nan akabirne ta achikkin ramin nan, yaron nan sai ya tashi. Da yaro de ya tashi, da yariniya da akabirne ta achikkin kabari. Sai kabarin nan ya zamma dakin karifi. Achikkin dakin karifin nan abinda achikkin duniya duk ba abinda babu achikki. Lokachin nan suka yi zammansu, suka yi aure kuma.

## 100

### The Boy and the One-Sided Giantess.

Wanni yaro, dan sariki, ya che zashi yawon duniya. Sai ya tashi, yana taffiya, yana taffiya achikkin daji, sai ya je ya tarada baban rafi. Sai ya kewoya bakin rafin nan duka ba ya ga sawun komi ba. Sai ya debe ruwa hanu daya ya sha, sai ya debe daya ya bai karensa. Sai ya che shi yau zaya ga abinda yana shan ruwan nan. Sai ya hau itache, sai karensa ya kwanta a gindin bishiya. Ruwa kuma kaman dagga nan zuwa baraki fadinsa.

Sai wanni lokachi chan da la'asa, ya ga wota mache, doguwa, hanunta daya, sawunta kuma daya, ido daya. Sai ta zo bakin rafin, sai ta shainya ruwan nan pap, du ya kare. Sai ta dinga kuka, ta che kishiruwanta ba ya mutu ba. Ashe ruwa ya kare. Sabilida yaro ya debe na hanu daya, ya bai karensa na hanu daya.

Lokachin nan sai ta hakura, ta mika gidanta. Sai ta je ta

fidda rumbun hatsi dami kaman metin, sai ta sasaka, sai ta daffa tuwo da hatsin. Sai ta je ta kamo bijimi biyu, sai ta zo ta yanka ta yi miya.

Shi ko, yaron, dagga chan sai ya tashi, ya bi gidanta. Da ya zo, da dan bishiya a bakin kofanta, sai ya hau, ya aje karensa a gindinsa. Matan kuma, sai ta fidda miyanta, sai ta zo kuma, ta fidda tuwonta. Sai ta shiga daki zata dauko zannenta na chin tuwo. Shi kuwa, yaro, sai da dan mashinsa, sai ya soke tuwon nan kadan, sai ya daga, sai ya fusi a bakin mashin. Sai ya raba biyu, ya sa daya achikkin bakinsa, daya kuma ya jefa ma karensa a kassa.

Kuma machen ta fitto chikkin daki, ta zo kuma, ta zamna zata chi tuwo, sai ta fara chin tuwonta. Da ta kare chin tuwo sai ta dinga kuka, ta che yau wanni abu ya tabba mata tuwonta. Har tsakan dare tana kuka, sai ta hakura, ta shiga daki.

Shi kuwa yaro, ya sauko, ya kirra karensa, ya furima aguje. Ba ya tsaya ba sai garinsu. Da ya je, ye che " Ubana na ga abinda ya ke ackikkin duniya."

# PART III.

# Hausa Text of Stories in Other Books and Journals.

## (*a*) FOLK-LORE, June, 1910, to December, 1911.

---

### 101

### THE SPIDER, THE HIPPOPOTAMUS, AND THE ELEPHANT.

Gizzo ya tashi, ya taffi kogi, ya che " Dorina, giwa ta che ta fi ki karifi." Ta che " Ba ta fi ni ba." Ya che "To, gobe muwa gamma da ku a hainya (1).

Ya dauka kiri ya daure giwa. Ya taffi kogi ya samu dorina, ya daure ta da igiyar (2). Ya koma tudu ya kama igiyar, ya motsa, ya ja. Giwa ta che " Dorina tana ja na " (3). Dorina ta che " Giwa tana ja na." Gizzo ya ja da karifi, suka zo, suka ga junansu a tudu. Sa'anan dorina ta che " Ashe, gizzo ya gamma mu da fada da ni da ke." Sa'anan suka kunche kiri, suka che " Mu yarda igiya, mu nema gizzo."

Da gizzo ya ji ananeman sa, ya tashi, ya nema tsofan (4) fatan gada, wanda ya bushe, ya shiga. Ya zona a rana, pata ya bushe sosai. Sa'anan ya tashi, ya zo wurin giwa. Da ta gan shi, ta che " Gada, mi ya same ki kin lalache?" Gizzo ya che " Mun yi fada jiya da gizzo, ga shi, ya nuna mani farichi, ya yi mani baki (5) na lalache."

Giwa, ba ta sani gizzo yana magana, ta tsamani gada che, sai ta ji tsoro, ba ta kara neman (6) gizzo ba.

(1) I shall meet you, plural used for singular.
(2) The " r " here is the definite article.
(3) Possessive pronoun instead of personal.
(4) The " n " here is euphonic.
(5) Lit. " he showed me nails, he made to me mouth." The first may mean also " he pointed at me," *i.e.*, made the sign of the evil eye. The latter probably refers to the evil mouth.
(6) A verbal noun.

## 102

### The Spider, the Hyæna, and the Corn.

Naman daji duk sun taru. Suka yi shingensu suka tara dawansu achikkin rumbunsu. Suka che "Mu taffi garin yawo, da damana ta yi kuma mu komo wurin ajiyammu." Bayan tashinsu, gizzo ya zo yana deban dawa. Izan safi ta yi yana deba har ya chainya dawa na rumbun nan duka. Sa'anan ya nema kwariya yana kwashen kashin kura, ya kan chikka rumbu da shi. Sa'anan naman daji sun che "Mu koma gida kuma." Duk sunka komo, ba su ga gizzo ba. Shi ne sarikinsu. Suka rikka kirra "U Gizzo, U Gizzo," ba suka gan shi ba. Shi ma, shina da kussa, amma ya amsa da hankali "I" kaman shina da nisa. Sai wanni kwanaki (1) ya amsa da karifi "I." Sa'anan ya zo. Sunka che "Mun zo tun da safi, yunwa ta kama mu, sai ka debo muna dawa mu chi." Sa'anan ya kama rumbu ya hau. Da ya hau ya duba, sai ya che "La Allah." Suka che "Mine?" Ya che "A, a," ya shido. Sai ya che "Kura ki hau, ki debo dawa." Kura ta kama ta hau, da ta bude ta ga kashi achikki irin nata, ta che "Allah ba ni ne ba." Suka che "Mine?" Ta che "Ba ni ne ba." Wanni ya che "Bar en zo en gani." Da ya hau ya ganni, ya che "Kura ta lalata mu." Sa'anan suka turo ta, kowa ya dauke sandansa za'abuge ta. Sa'anan ta gudu ta shiga daji. Rashin dadinta (2) ke nan da ita da naman daji, ita ba ta son su, su kuwa ba su son ta ba, su sun yi mata laifi, gizzo ya daura mata magana (3).

(1) "Until after a time," a strange use of kwanaki.

(2) "The loss of her enjoyment," trans. "that was the end of the friendship between her and the other beasts."

(3) "Tied to her the words," *i.e.*, "brought the trouble upon her."

---

## 103

### The Mallam, the Spider and the Hyæna.

Wanni mallami ne da dokinsa. Ya tashi dagga Zaria zashi Birnin Kano, sai ya sauka a gusun tsamiya yana futa. Sai kura ta zo, ta che "Mallam," ya che "I." Kura ta che "Ga

nama chan ya mutu a daji, ba ka ba ni aron dokinka en yi saure wurin ba?" Sai mallam ya che "Hau manna, Kura." Sai ta che "To, barri en kwashi surdi en aje." Da ta kwashi ta aje, sai ta ja doki. Da ta ja wurin yayanta sai suka chinye. Mallami ba kura ba doki, yana zona kurum. Sai gizzo ya zo, ya che "Mallam mi ka ke yi anan?" Ya che "Ina zone ne, na rassa doki da zan hau en taffi Kano." Sai ya che "Ga surdi, yaya ka rassa doki da zaka hau." Sai ya che "Kura ta zo ta janye doki zata gidanta." Sai gizzo ya che "To, yanzu na kawo maka kura, na daura mata surdi, na sa mata linzami, ka hau kura ka je Birnin Kano. Kai ma, izan na yi maka hakka, kai zaka ba ni layan farin jini?" Ya che "Na ko ba ka laya Gizzo." Sai gizzo ya tashi, ya taffi wurin gidan kura, ya che "Ke Kura, kina aiki banza ne. Ga nama chan, kina nan akwanche?" Sai ta che "Ai nama ya mutu gizzo?" Sai ya che "Fitto mu taffi mazza mazza." Sai ta fitto suna taffiya. Sai ya tarada mashimfidi akan hainya, sai ya che "Kura, izan na dauke mashimfidin nan en sa bayanki en hau, muwa fi saure." Sai ta che "Gizzo, dauke ka sa manna." Sai ya dauka ya sa, ya hau. Sai ya je ya tarada surdi kuma, ya che "Kura, bayanki da suka, sai en daura surdi en ji dadin hau." Sai ta che "Dauke ka sa manna." Ya dauke, ya hau. Sai ya je ya dauke linzami kuma, ya che "Kura, en na sa maki wannan, en tsamtsi zaya kashe ki en na ja, ai ba ki faduwa." Sai kura ta che "Dauke ka sa manna." Sai ya sa mata linzami, ya hau. Sai yana taffiya, ya dauke kaimi, ya che "Bar en sa wannan, en na tabba ki muwa fi saure." Da ya daura kaimi ya hau kura, sai ya dinga shirga mata kaimi chikki, tana zawo, sai ya kai ta wurin mallami. Ya che "Mallam ka hau, ga kura na kawo maka ita." Sai ya yi layan farin jini ya ba gizzo, sai mallami ya taffi wojen Kano. Gizzo ya che "En ka je Kano, kadda ka daure ta da kiri, ka sa mata sarka." Sai mallami ya che da kura "Ki tsaya, gizzo na (1) magana abaya." Sai ta che "Na ji, ya che en ka kai Kano ka daure ni da pata, wai kadda ka daura ni da sarka. En ka daura ni da sarka na mutu." Sai ya sa mata kaimi, suka yi ta gudu. Da ya je Kano ya sauka, sai ya daure ta da pata. Sai dare ya yi, sai kura ta chinye pata, ta shanya ruwan gida, ta chinye każan gida, sai ta kama akwiya daya ta fitta da ita, ta kawo ma yayanta akwiya na gida. Sai ta fitta neman gizzo. Gizzo, amba shi layan farin jini, kowanni naman daji ta tambaya, ya che "Mu ba mu ga gizzo ba." Har ta gaji da yawon daji ba ta

gan shi ba. Sai chiwun chikki ya murda ta, ta mutu a daji· Masoman gizzo ya yi farin jini ke nan. Kowanni tatsuniya sai anche gizzo.

(1) "Na" is short for "yana." "Yin" is understood.

---

## 104

### How the Spider outwitted the Snake.

Sago yana da sa. Salla ta yi kussa, ran jajibari ne. Sai yana taffiya da sanshi, ya che na sayararuwa ne, amma ba abiya shi da kurdi ba, sai adebi kwanakinda za'abiya ya zo ya sare mutum, ya biya ke nan. Sai ya yi yawo da shi, duka ba wanda ya karba. Sai ya je gidan gizzo, sai gizzo ya che "Sa naka nawa?" Sai ya che "Sa na ba na sayar da kurdi ne, sai adebi kwanakinda za'abiya na zo na sare ka." Sai gizzo, barawo, ya che ya yarda. Ya che to, ya chi sa, amma da salla ta wuche da kwana goma sha biyu sai ya zo ya sare shi. Sai gizzo ya che "To, shi ke nan," Sai ya taffi. Da kwana goma sha biyu ya yi kwana daya, (1) sai gizzo ya che ma matansa ta barza garin gero. Akadebo tsamiya, akazuba achikkin garin geron nan. Sai gari ya waye (2) kwana goma sha biyu ya chikka ke nan. Sai sago ya zo. Ya che "Marhaba, marhaba," en ji gizzo. Sai ya che ma mata "Ki dauko ruwa ya sha." Zaya dauko gari mai-tsami ke nan. Ta dauko. Sai sago ya sha ruwa, sai gizzo ya che "To, tsomi tsake ka chi." Sai ya deba, ya chikka bakinshi, sai hakorinsa suka mutu duka. Sai gizzo ya che "Sha manna," ya che ba zaya kara sha. Sai gizzo ya che "Sha daya ba keyau." Sai ya kara deba, hakori suka yi sainyi, ba su yi motsi, ba karifi kaman na da. Sai ya mika mashi kaffa, ya che "To, sare." Ya che "A,a, ba na iya ba." Ya che "Ai, yau ne mu ke yi wokachi ya chikka, sai ka sara de." Ya che ba zaya iya ba. Ya che "To, en ba ka sara yau ba, na biya sanka ke nan, en na kara ganin ka, sai bugan sanda." Sai sago ya ga gizzo mai-wayo ne, sai ya che "To, mun debi kwanaki sun chikka, ni ba na iya saren ka ba, ka biya, ba na kara zuwa ba."

(1) Means when only one of the twelve days was left.
(2) Lit. "the town became distinct"; another form is "washen garri." See Story 139.

---

## 105

### The Snake and the Dove outwit the Spider.

Sago ke nan, shina kiwon sanshi. Ya kirra mahauta su zo su saya. Sai suka che "Na mini?" Ya che "Wanda en ya saye, en taugana ya kone en zo en shigga chikkin chikkinshi." Sai Sarikin Pawa ya che "A,a, ba zamu iya ba." Sai gizzo ya zo, da ya zo, akagaya mashi, sai ya che shi ma ya saya, en taugan ya kone shi zo shi shigga chikkin chikkinshi. Sai gizzo, ya che ya yarda, ya kama sa, sai sago ya koma achikkin ruwa, gizzo ya taffi ya chi namanshi. To, kaka ya yi, kwanaki ya yi. Sai gizzo ya tashi, ya haka rami, akadaka mashi gari, ya shiga da shi rami. Matanshi ta rufa shi. Sai ya che ma matan "En de sago ya zo ache ma sago ya mutu. Da sago ya zo kuma koki ta che mashi gizzo ya mutu." Sai sago ya che ta taffi ta nuna mashi kusheya. Koki ta taffi, ta nuna mashi. Sai sago ya koma. Kurichiya ta zo wurin sago, tana bissa itache ta ga sago zaya mutu. Sai ta che "Mine ya same ka?" Sai ya che "Gizzo ne ya yi mani rikichi. Ya chi mani sana." Sai ta che "Yanzu ka ba ni nawa en kai ka wurin gizzo?" en ji kurichiya. Sai ya che ya ba ta alfin. Sai ta che ta ki. Ya che ya ba ta zambar goma. Sai ta che ta ki. Sai ya che ya ba ta zambar ashirin. Sai ta che "To." Sai ta zo ta dauke shi, ta zo da shi wurin gizzo. Tana waka, tana che "Akanbi bashi a kusheya mu masu-biyan bashin gizzo mun zo." Ta che "Kunun tamba darimana, hakka tsuntsai." Sai gizzo ya amsa chana, ya che "Hakkanan ne kurichiya? Shiggo dakina ki sha ruwa, kunun tamba darimana, hakka tsuntsai." Sai gizzo ya fitto woje, ya ga sago. Ya che "Habba, Mutanen Duniya, ka chainye mani sa, ina neman ka, ban gan ka ba." Sai gizzo ya che mashi "Zamu yaya kuma?" Sai ya che "To, ka shigga." Sai sago ya shigga chikkin gizzo, sai gizzo ya kwanta nana, har ya zo ya mutu. Sai sago ya fitta abinshi.

---

## 106

### The Spider has a Feast.

Da kwalima ya kama gizzo ya rassa nama da zaya chi. Sai ya che to, zaya yi dabara. Ya che zaya tara naman daji duka su kuka mutuwa. Da sun taru duka, zaya tashi bup, mainya zasu ji tsoro zasu tataka kankanana. To, akagaya ma giwa gizzo ya mutu, akagaya ma bauna, akagaya ma gwanki,

akagaya ma kanki. Achikkin kankanana kuma akagaya ma barewa gizzo ya mutu, akagaya ma gada, akagaya ma baziya, akagaya ma kwanta-rafi, akagaya ma zomo, akagaya ma kurege, akagaya ma makaruwa. Sai suka zo duk, suka taru a gidan. Kowanni ya zo sai ya duba ga idonshi, ya yi ta kuka, ya che "Wayo gizzo ya mutu." Duka naman nan suka kuka, sai ya ragi makaruwa kadai. Ta fi su wayo. Da ta zo ta duba, ta ga dan ido kil kil kil (1), sai ta je ta hau bissa, ta sa (2) waka. Shi kuwa gizzo ya sa guduma kussa ga wiyanshi. Makaruwa zata yi ma kankanana wayo, ta che "Kurege, Zomo, gizzo ya mutu, amma mutum a garinsa en ya mutu ijiya kilu? Guduma a wiya?" Ta che "Kurege, Zomo, ku gudu." Ita ta chira, ta tashi hakka turrrr. Da ta tashi gizzo ya ji, ya ga sauran nama zasu gudu, sai ya tashi bup. Da ya fitto, da giwa da bauna da gwanki da kanki sun gudu, sai suka taka barewa da baziya da zomo da kurege, duk suka mutu. Sai gizzo ya zo ya debi nama. Ya che ya yi wayonda ya samu nama.

(1) The bright eyeball, the eyelids were blinking.
(2) "Yi waka" is much more common.

---

## 107

### How the Spider obtained a Feast.

Gizzo ne de. Kwadaye ya kama shi, sai ya sa wa dakinshi wuta, ya kone. Da ya kone, sai ya je dakin kaza, ya che "Gobe ina gaya," dakinshi ya kone. Sai kaza ta che "To, kadda ka gaya wa muzuru." Sai ya che "A, a, habba." Da ya tashi, sai gidan muzuru. Da ya je gidan muzuru, sai ya che "Salla'am aleikum" (1). Shi kuwa ya che "Aleika salla'am." Shi ke nan sai ya che "To, dakina ya kone, gobe ina gaya." Sai ya che "To, amma kadda ka gaya wa kare." Ya che "A, a." Da ya je, sai ya je gidan kare. Ya che "Gidana ya kone, gobe ina gaya." Ya che "Gayar mi?" Ya che "Gayar yanta." Ya che "To, amma kadda ka gaya ma kura." Ya che "A, a, ba agammuwa da ita." Da ya tashi, sai gidan kura. Ya che "Gobe ina gaya." Ta che "To, amma kadda ka gaya ma damisa." Ya che "A, a." Ya taffi, sai gidan damisa. Ya che "Gobe ina gaya." Ya che "To, Allah ya kai mu, amma kadda ka gaya ma zaki." Ya che "A, a." Ya taffi, sai gidan zaki. Ya che "Salla'am aleikum." Ya che "Aleika salla'am."

Ya che "Gadanga Wandawa," ya che "Gobe ina gaya." Ya che "To." Sai gizzo ya komo gida. Da ya komo gida, da sasafi ga kaza ta zo yanta. Tana yanta, sai ga muzuru. Sai muzuru ya che "Gizzo, salla'am aleika." Sai kaza ta che "A, Gizzo, na che kadda ka gaya wa muzuru, sai da ka gaya mashi?" Sai gizzo ya che "To, shiga chikkin chiyawan nan." Sai muzuru ya je ya kama kaza, ya kasshe. Shi ke nan, sai gizzo ya che "To, kawo en aje ma." Sai muzuru ya che "To." Shi ke nan, sai ga kare, sai ya che "A, Gizzo, enna yantar?" Sai gizzo ya nuna mashi gunda muzuru yana boya, sai ya che "A, ga ta nan." Sai kare ya kama muzuru ya kasshe. Sai gizzo ya che "To, kawo en aje ma." Shi ke nan, kare iya yanta sai ga kura. Da ta zo, sai ta che "Enna yantar?" Sai ya nuna mata enda kare ya ke. Sai ya che "A, na che kadda ka gaya mata." Sai kura ta kama kare ta kasshe. Sai gizzo ya che "To, chainye abinki, ni ba ni so." Sai ta chainye. Shi ke nan, sai ga damisa ta zo, sai gizzo ya che "Ga gun yantan nan." Sai ta je ta samu kura, tana kudandina achikkin chiyawa. Sai ta kasshe, ta ba gizzo ya aje. Sai ga zaki ya tarada damisa. Suka yi ta fada. Suna fada, suna fada, suna fada. Gizzo ya dauko baban sanda iya (2) ta duka, iya ta duka, iya che "A, Zaki barri, A Damisa barri, fadanku na mainya wa ika (3) shiga?" Sai gizzo ya bubuge su da sanda, ya kasshe su. Sai ya tara nama a gidanshi dayawa. Duk ya chi nama, ba ya bai (4) koki ba, kwadayen gizzo ya chikka yawa.

(1) The Hausas love introducing Arabic, no matter whether correct or not.
(2) Iya = yana.
(3) Ika = iya, uncommon except in such phrases.
(4) Bai = ba, baiwa, &c.

---

## 108

### The Spider outwitted by the Tortoise.

Kunkuru ke nan. Da shi da gizzo zasu yi fatauchi. Kowanni gida suka sauka, sai ya che ma kunkurus (1). "To, idan ankawo tuwo anche 'na baki,' to nawa ne; en anche 'na bako' naka ne." Kunkuru, ba ya san hausan garin wurinda zasu. Da yamma akakawo tuwo, akache "na baki ne." Gizzo ya che "To, Kunkuru, ka gani nawa ne." Ya chainya tuwo, ya bar shi da yunwa. Da safi kuma suka taffi wanni gari,

akakawo tuwo, akache "na baki." Sai gizzo ya che "Nawa ne." Sai kunkuru, yunwa ya kama shi, ya rami. Da ya rami, tsakan darre ya yi ya dauke kwariya na masu-gida, yana chin kamso. Sai mai-gida ya fitto da sanda zaya buge shi, sai ya che "A, a, ni ne, kunkuru." Sai mai-gida ya che "To, tuwonda akakai maka fa?" Sai ya che "A, a, gizzo ya che idan 'na baki' nasa ne, idan 'na bako' nawa ne." Sai mai-gida ya che "Ashe, hakka gizzo ya yi maka?" Ya che "Barri, da safi arama maka." Sai da safi mai-gida ya sa akayi tuwo. Akakawo kaji biyu, sai akasamu yaro, akache mashi "Ga shi, sai ka che 'Ga tuwo na bako'." Da yaro ya kawo, ya che "na bako ne." Sai gizzo ya che da yaro "Kariya ka ke yi, ai mu biyu ne, zaka che 'ga tuwo na bako'?" Sai yaro ya che "A, a, anche akawo ma bako tuwo ne." Sai gizzo ya che "To Kunkurus, chi, Allah ne ya ba ka." Sai gizzo ya yi fushi, ya che "Gobe muwa tashi." Da zasu sallame su, su mutanen gida sun sa bunsuru da sa achikkin daki. Sai akadaura ma sa igiya, akadaura ma bunsuru kiri. Akarufe kofa, sai igiya suka barri awoje. Sai mai-gida ya che "Kowa ya zo ya kama igiya, abinda ya kama nashi ke nan." Sai gizzo ya zo ya ture kunkuru, ya kama kiri yana che ko sa ne (2). Sai akache "Kun kama?" Akache sun kama. Da akabude kofa akache kowa shi ja nashi. Da gizzo ya ja kiri bunsuru ya fitto "ba'a." Sai kunkuru ya ja nasa igiya sai sa, kato. Sai gizzo ya ji zafi a zuchiyanshi, ya che zaya rama a mugunta. Suka yi taffiya sai ya yanka bunsurunshi, shi gizzo, sai ya ba kunkuru hanta, sai ya sa shi achikkin jekka. Suka taffi kadan, sai gizzo ya che "Kai Kunkuru, ba ni hantana" en ji gizzo. Sai kunkurus ya sa hanu ya fitto da ita, ya ba shi. Sai gizzo ya che "Op Kunkuru, ba ka san wasa ba?" Sai ya che "Ina yi maka wasa ne, chainye, na ba ka keyauta." Sai kunkurus ya chainye hanta. Da ya ga ya chainye, da suna taffiya, sai ya che "Kunkuru, ba ni hantana." Sai ya che "A, a, babu hanta." Sai gizzo ya che "Kariya ka ke yi, ka yanka sa ka ba ni hanta." Sai ya yanka sa, shi kunkurus, ya ba gizzo, sai gizzo ya che hantanshi ya fi hakka yawa. Sai kunkurus ya yi fushi, ya raba sa, ya ba shi rabi. Sai gizzo ya che "A, a, hantanshi ya fi hakkanan." Sai ya ba shi sa duka. Sai ya dauke nama duka, shi gizzo, sai ya che ya rama. Kunkurus ya che "To, ni ma na rama." Sai kunkurus ya kiyale gizzo, sai ya taffi hainya dabam, ya samu alli da shuni, ya sa a jikkinshi rode-rode. Sai ya je, ya kwanta akan hainya. Rana ta fadi, almuru ya yi ke nan. Sai gizzo ya zo ya yi ganin shi (3), sai

tsoro. Ya buga kiriji, ya che "Rode-Rode, ba ni wuri en wuche." Ya zamma shiru. Sai ya che "Kana son sa ne?" Kunkurus ba ya yi motsi ba. Sai ya dauke chiniya ya jefa mashi, kunkurus ba ya yi motsi ba. Sai ya sake jefa mashi, sai shiru, ba motsi. Sai ya che "Ko kana son naman sa duka?" Ya dauke. Ya jefa mashi naman duk. Kunkurus ya ki motsi. Sai gizzo ya che "Kana son riga da wandona?" Sai ya tube, ya ba shi duka, ya zamma tsirára. Sa'anan kunkurus ya jirga, ya bashi hainya, ya wuche. Sai kunkurus ya tashi ya dauke nama, duka kayan ya kwashe, ya che "Ni ma na rama."

(1) The "s" is apparently a definite article used instead of "n" when not followed by the word "nan."
(2) He thought, he said to himself.
(3) This more complicated construction is more emphatic than "ya gan shi."

## 109

### The Spider and the Rubber Baby.

*See* No. 15.

## 110

### The Jackal's Revenge on the Spider.

Gizzo ke nan. Yana aboki da dila. Sai dila ya che "To Gizzo, zani taffiya, amma bazara ya yi." Ya kawo iri na gero, ya che "En ya yi ruwa ka taffi gwonanka ka shuka, ka shuka mani nawa." Sai gizzo ya che to ya ji. Da akayi ruwa, sai gizzo ya shuka gero a gwonanshi. Da ya gamma kuma, sai ya zo gwonan dila. En ya sara, ba ya zuba iri, sai ya taka kurum. Da geron gizzo ya tsiro ya yi keyau, gwonan dila kuwa sai haki ya tashi. Dila ba ya tashi dawowa ba sai gero ya fara chikki. Kwanakinnan ba sauran shuka ba, komi da anshuka ba zaya tsiro ba. Da zuwanshi, gizzo ya je wurinshi, ya che "To, ga shi, na yi shuka a gwonanka, amma makaruwan dare ta tona gwonanka." Dila ya che "A, ba ta tona naka ba ta tona nawa?" Sai ya che "Ai da dare ne, tana tonawa chan kassa ba ta tona bissa, ba mai-gani." Sai dila ya che

"To madallah, amma ni ma en rama." Sai dila ya bari sai kaka ta yi, sai gizzo ya sa dawa a rumbu, da gero da dauro da wake. Sai dila ya samu koko, ya zuba ruwan zuma chikki, ya kawo ma gizzo. Sai gizzo ya sa hanu ya dandana, ya che "A, mine mai-dadi hakka?" Sai ya che "A, dawa ke nan da na barri a rumbu, na dawo dagga taffiya na kona na digo toka." Sai gizzo ya je ya sa ma rumbunshi wuta ya kona, ya diga tokan dawanshi. Ya dandama. Ruwa, ba ya yi zaki kamman zuma ba, sai ya koma wurin dila, ya che "Ai ban ji dadi ba." Dila ya che "Mi ka kona?" Ya che "Dawa." Ya che "A, a, ban che ka kona dawa ba, na che ka kona gero." Sai ya che "To." Sai ya je, ya kona rumbun gero, ya diga, ya dandana. Ya ji dowatchi. Ba ya ji dadi kaman zuma ba. Sai ya che da dila "Ban ji dadinshi (1) ba." Sai dila ya che "Mi ka kona?" Sai ya che "Gero." Sai ya che "A, a, ban che ka kona gero ba, na che dauro." Sai ya che "To." Sai ya je ya kona rumbun dauro, ya diga, ya dandana, ba ya ji dadi ba. Sai ya koma ya che da (2) dila "Ban ji dadinshi ba." Sai dila ya che "Mi ka kona?" Ya che "Dauro," ya che "A, a, ban che ka kona dauro ba, na che ka kona wake." Sai ya che "To." Sai ya je ya kona rumbun wake, ya diga, ya dandana, ya ji dowatchi, ba ya ji dadi kaman zuma ba. Sai ya che da dila "Ban ji dadinshi ba." Sai dila ya che "Mi ka kona?" Sai ya che "Wake." Ya che "Madallah, Gizzo, na rama maka mugunta da ka yi mani." Sai gizzo ya rassa abinchi, sai yana bara.

(1) I did not taste its sweetness, *i.e.*, it did not taste sweet to me.

(2) "Da" here means "to," sometimes used after "che," but "ma" is used after "gaya."

---

## 111

### The Lion, the Spider, and the Hyæna.

Zaki ke nan ya sayo ragonshi. Shina kiwonshi. Shi ke nan, sai rago ya yi girima, akasa masa suna Barra Randam (1). Akadaure masa gwarji a wiya. Rago ya yi girima. Ran nan zaki zashi kiwo da nisa. Sai ga gizzo ya ji labari, ya zo, ya che da zaki shi ba shi kiwon rago. Zaki ya che "A, a," ya che "Kadda wanni abu ya kama shi." Sai gizzo ya che "Ba abinda zaya same shi." Sai zaki ya che "To, bar em bar shi."

Da teffiyan zaki, gizzo ya kama rago. Ya taffi, ya yanka, ya chi. Ya aje pata da gwarji. Ya aje kitsen. Sai zaki ya komo, gizzo ya zo da kuka (2) ya che "Wanni abu ya kama rago." Sai zaki ya che "Kariya ne." Ya che "Gobe zan tara naman daji duka su zo su yi rawa wurina." Gizzo ya taffi gida. Ya taffi ya kirra kura, ya zo, ya che "Gobe za'ayi biki a kofan zaki. Ga fata ki daura." Sai kura ta karba, ta daura. Sai gizzo ya daura mata gwarji a wiya, ya kawo kitsi ya sa ma kura a baki. Sai ya che "To, kadda ki chi kitsen ba, ki bar shi, ado ke nan." Sai kura ta ji alfarma, wai gizzo ya ba ta ado. Safi ya yi naman dauji duk sun taru. Da sun taru, sai gizzo ya zo da dan ganganshi. Ya zo, shina kidda "Wane ya chi baba randam? Kura mai-chin baba randam. Pata a gato, patan baba randam. Gwarji a wiya, gwarjin baba randam. Kitse a baka, kitsen Barra randam." Kura tana rawa, tana wasa, ta che "Hakka magana ta ke (3), kadda ganga Gizzo, hakka magana ta ke." Sai zaki ya ji haushi, sai ya taffi ya buge kura, ya kasshe, sai naman daji duk sun gudu. "Zaki ya rama ke nan," en ji gizzo, "ashe kura ta chi rago."

(1) The Numuna word "Randam" means "Bull." The name has evidently been coined in order to give the opportunity for a play upon the words, and to deceive the Hyæna.

(2) "Came with crying."

(3) *I.e.*, That is quite true, she was delighted that she should have been credited with having killed a big bull, and so fell into the Spider's trap.

---

## 112

### The Cunning Spider and his Bride.

Wota yariniya ke nan, dakeyau. Kowa ya zo auren ta ita ta che ba dukiya za'akawo ba. Sai ubanta ya yi bichi akofan gida da kashi da fisari, duk abin dauda achikki. Ya che "To, wanda ya zo ya fude wurin ba ya zubda yawo ba ya chi abinchi, shi ne mijinta." To, kowanni sauraye ya zo, ya che shi ba ya iya ba. Sai gizzo ya che shi ya iya. Ya che "En na zo garin fudan nan anbarri ayi waka?" Sai uban ya che "A, ahanna mai-noma waka?" Sai ya che "To, gobe da safi na zo," en ji gizzo. Sai ya sa koki, matanshi, ta dama fura, ta sa achikkin kwore. Sai ya tsinke sili ya zuba achikkin kwore, kaman

kibiya ke nan. Da ya zo, sai uban ya che "To, ga bichin da zaka fuda." Sai ya che "To, ina da magana daya," ya che "Ni, en ina fuda, ba zan raba da kworena ba, zamanin nan ba ya kamata namiji ya rabu da kwore ba." Sai uban ya che "A, dakeyau, namiji ya raba da kworenshi?" Sai ya che "Ba wanni abu za'ahanna ka ba banda zubda yawo, bamda chin abinchi." Sai ya che "To." Ya karbe galma yana fuda, sai yana zubda yawo da wayo, yana waka "Ni gizzami na koko" sai ya che "Up tup tup, Up tup tup." Ya zubda yawo ke nan. Shi ke nan, da rana ya yi bakinshi ya komada, ya fitto da siliyan nan achikkin kwore, ya che zaya shainye daffi. Sai ya kafo bakinshi abakin kwore, sai ya chikka chikkinshi da fura. Sai ya tashi kuma, ya kama fuda, sai ya fuda bichi sarai. Sai buduruwa ta zo, ta che "Arururururuwi, mijina ke nan." Sai uban ya che "Madallah, shi ne mijin yariniyana." Shi ke nan, sai akayi kayan gara mai-dadi (da tallin mai, da gishiri, da dadowa, da shinkafa, da wasawasa). Shi ke nan, sai akakai yariniya gidan gizzo. Akwana atashi (1) sai yariniya ta samu chikki, sai ta haife yar-mache. To, en zata rafi diban ruwa, sai gizzo ya dauke yan, yana rawa, yana chewa "Da fura akwore na samu uwanki, na yi dabara, na yi dabaru." Sai wota tsofuwa ta ji (ta "Kwankwari korenki Taboki, kasshe mani kyaya, kasshe maki aure"), ta ji. Da ta dawo rafi sai ta gaya ma yariniya, ta che "Kiya ji abinda gizzo ya ke chewa?" Ya che "Da fura akwore ya aure ki, wai 'dabara da dabaru.'" Sai ta che "To, Tsofuwa, kin gani ina zone da mijina da girima da arziki, zaki passhe mani aure ke nan?" Sai ta che "To, tunda kin yi gardama, gobe da kin taffi rafi, ki zo ki makye." Ta che "To." Da safi da ta taffi raffi ta komo, ta makye. Sai gizzo yana rawa, yana chewa "Da fura a kwore na samu uwanki, na yi dabara, na yi dabaru." Sai ta zo ta sauke tulu, sai ta che "Ashe, da ka zo ka che zaka yi aure na, anfada maka ba azubda yawo, ba achi abinchi, ka yi dabara ka sha?" Sai ta che "To, tunda ka sha fura ni ba ni zamma a gidanka, zan taffi gidammu." Da ta taffi, ubanta ya che "Mi ya kawo ki?" Sai ta che "A, akwai abinda ya kawo ni." Sai ta che "Gizzo da ya zo aure na, ashe da dabara ya sha. To ni, ba ni zamma wurinsa ba." Sai uban ya che "To, ai gizzo ya zo biko na ji abinda ya gamma ku." Sai gizzo ya taffi garim (2) biko. Da ya zo, sai uban ya che "Mi ya gamma ku?" Sai gizzo ya che "A, akan waka ne, yariniya ta taffi rafi, ni ina rawa da dan, ina waka." Sai uban ya che "Wanni irin waka ka ke yi?" Sai gizzo ya che "Ke, Yar Alkawali, Yar Mutum Biyu." To,

da ta zo, sai uban ya che "Wakan ke nan da ya hada ku fada?" Sai gizzo ya che "I." Sai uban ya che "To, wannan fada ba ya isa yaji ba." Sai yan ta kwasshe kaya, ta koma gidan gizzo. Sai gizzo ya zo ya yi aiki, har yau ba aga la'ananshi ba, ba agani abinda ya yi.

(1) Lie down and get up, *i.e.* after a time.
(2) "N" often changes to "m" before "b" or another "m."

---

## 113

### How Spiders were Reproduced.

Gizzo ke nan. Kwanakin yunwa. Ba shi da abinchi, ya che zashi yawon karatu. Sai tinkiya ta che "Ga Dana taffi tare da shi ka koiya mashi karatu." Da suna taffiya sun zo wurin ruwa, sai gizzo ya che da dan tinkiya ya dama gari. Da ya dama gari, ya che "Kai ba zaka sha ba, ni ma zan sha, amma en ka yi bara ka samu." Sai suna taffiya, sai dan tinkiya, duk ya rami, ya zamma jijiya. Shi ke nan, da suka zo wanni gari, sai gizzo ya che "To, da dare, da ankawo tuwo, ko ba ni nan kadda ka fara chi, sai ka ba kare na sarikin gari." Sai ya che "To." Sai gizzo ya rikidda kare. Da ya rikidda kare akakawo tuwo, sai dan tinkiya ya yanke tuwo, ya jefa ma kare ya chainye, ya yanke masa ya chainye. Sai ya jefa masa duka. Da tuwo ya kare, sai gizzo ya rikidda, ya zamma gizzo, ya zo wurin dan tinkiya, ya che "Sun kawo tuwo, karen sariki ya zo ka ba shi?" Sai ya che "I." Sai ya che "To," gobe zamu tashi." Da gari ya waye suka tashi, dan tinkiyan nan yana biya da shi. Sai ya che "Ka gani yawon karatun nan ba mu hito da sa'a ba (1), mu koma gida," en je gizzo. Sai suka taffi. Da suka zo wanni kogi, sai gizzo ya fura wuta ganga ganga. Da akafura wuta, sai gizzo ya che "Ka ji, ni zan fada ruwa kai zaka fada wuta." Sai ya che "Tun da ba rain gizzo, ni, raina mi ya ampana?" Da ya ji gizzo ya fada a ruwa sai ya fada a wuta. Ya mutu. Sai gizzo ya fitto. Ashe ba shi dakainshi ya fada a ruwa ba, ya jefa da dutsi ne. Sai ya kankare gashin tinkiya, sai ya chi rabi awurin, rabi kuwa ya zuba a zabira. Shi ke nan, sai ya taffi. Da ya zo wojan gidan tinkiya, sai yana kuka, yana kuka, ya che "Amba ni yaro en koya mashi karatu, ga shi ya

mutu." Shi ke nan, sai tinkiya ta che " A, ba komi Gizzo, Allah ne ya yi hakka." Sai kadduwa, ita kuwa kadduwa, kishiyan tinkiya che, mijinsu daya, sai ta che " To ni da nawa dan, ku taffi tare." Sai ya che " To," en ji gizzo. Sai dan kadduwan nan, akayi mashi dan ludaye da dan kwariya, akabarza mashi gari. Da suna taffiya, sun zo kogi, sai gizzo ya che " Dan Kadduwa, dama garinka en sha, kai ko ka yi bara." Sai ya che " En na je bara ban samu ba fa?" Sai suka dama gari, suka sha tare, suka koshi. Dan kadduwa ya tashi dikir, gizzo kuwa ya tashi dikir. Sai suka taffi. Da suka zo wanni gari kuma, suka sauka, sai gizzo ya che " To, en ankawo tuwo da dare, ba ni nan, kadda ka chi, sai ka ba karen mai-gida yana zuwa." Sai dan kadduwa ya che " To." Shi ke nan, da dare ya yi, sai gizzo ya rikidda, ya zamma kare, ya zo. Dan kadduwa kuwa ya tara makodi agabbanshi. Da akakawo tuwo kare ya zo, sai ya jefa ma kare makodi. Sai ya gamma chin tuwo, ya koshi, sai gizzo ya rikidda, ya komo gizzo, ya che " Karen sariki ya zo ka ba shi tuwo ne?" Sai dan kadduwa ya che " Ni enna ruwana da kare? Sai na jefa masa da dutsi." Sai gizzo ya che " To, shi ke nan, sai gobe muwa tashi. Yawon karatun nan ba mun hitto da sa'a ba." Shi ke nan, sai ya che " To." Da suka zo kogi, sai gizzo ya fura wuta, ya che shi zaya fada a ruwa, dan kadduwa shi fada a wuta. Dan kadduwa, da ya ji gizzo ya fada a ruwa, sai ya dauke takalaman gizzo ya sa a wuta. Sai ya shiga chikkin zabiran gizzo, ya daure baki. Da ya fitto, shi gizzo, ya dibi takalama, yana chi. Sai ya che " Wannan yana chi ya koshi, amma ba ya yi mai ba, wanchan ya fi shi mai." Dan kadduwa kuwa yana ji chikkin zabira. Shi ke nan, da gizzo ya zo gidan kadduwa kuwa, yana kuka, ya che " Amba ni dan tinkiya ya mutu, ga kuma dan kadduwa ya mutu." Dan kadduwa, shina chikkin zabira, da ya ji hakka sai ya fitto " Bup," ya che " Kariya ne ka ke yi, ka chainye mani danuwana." Sai gizzo ya zubar da gudu. Sai tinkiya ta che " To, wa zaya kamo mani gizzo?" Sai jaka ta che " Ni zan kawo maki." Sai ta che " To, yi nakiya." Sai ta yi nakiya, akachuri na biyal-biyal dabam, na goma-goma dabam, na ashirin-ashirin dabam. Sai jaka ta hadiye duka. Sai ta zo wurin damfamin gizzo, tana chi. Sai gizzo ya che da matansa " Ke, fitta, kora mani jaka tana chin damfami." Da ta dauke kara ta duke ta, sai ta yiwo kashi nakiya na churi biyal-biyal. Sai matan gizzo ta dauka. Da ta chisa, ta ji zaki, sai ta kai wa gizzo. Da ya chi, sai ya che " Ke, enna kin samu wannan?" Sai ta che " Kashin jakan nan wadda tana chi muna damfamin nan." Sai

ya che "Ba ni sanda mazza." Sai ya je, yana bin ta yana bugen ta sai ta yi na goma-goma. Sai ya dauke, ya chi. Ya kara bin ta, ta yi na ashirin-ashirin, yana bin ta, yana dukan ta, har suka zo gidan tinkiya, gizzo ba ya sani ba. Sai akayi rup, akakama gizzo, akafiyadda shi akassa. Sai ya passhe, ya raba a bangon gida, da itache, da komi. Dalilin ke nan da ya zamma dayawa. Da daya ne.

(1) We have not brought out an hour, *i.e.*, we have not come at a lucky time.

---

## 114

### How the Woman taught the Spider Cunning.

Wota mache ta kirra gizzo, ta che "Ka zo en kara maka dabara." Ya zo, ta che "Taffi ka samu hawayan zaki." Ta che "Ka samu hakorin giwa, da patan karkeche." Sa'anan gizzo ya tashi, ya taffi hainyar fatake, ya kwanta, ya yi kaman ya mutu. Ya kwanta ya yi shiru. To, sa'anan fatake suka zo, suka wuche, suka che "Ai, gizzo ya mutu a hainya." Fatake suka wuche, suka kare, duk suka wuche sai mutum daya. Ya sake tashi aguje, shi gizzo, ya kewoya, ya rigaya su chan a hainya, ya sake kwanche a hainya kuma. To, sa'anan fatake suka zo suka wuche, suka che "Kai, gizzo yau suna mutuwa dayawa, ga wanni kuma." Suka wuche duk, saura guda dayan nan, ya zo shina kaiwa kanton gishiri. Sa'anan ya ga gizzo, ya che "To, bar en taffi en dauko wanchan, en zo en gamma da wannan, en chi." Da ya aje kayan ya taffi, shi gizzo ya tashi, ya dauke kayan. Da falke ya komo ba ya ga kaya ba, ba ya ga gizzo ba, duk chikkinsu biyu ba ya ga daya ba, ya gudu, ya bi yan-uwansa fatake. Gizzo ya taffi, ya passa kanto a fa. Sa'anan ya kirra giwa, ya che "Giwa, ga wanni abinchi na kawo maki." Sa'anan giwa ta zo, tana chi, tana chi, pa ya kariye hakori. Gizzo ya dauke hakori, ya boye. Sa'anan ya taffi ya kirra karkeche kuma, ya che "To, ku zo ku taru mu yi ma giwa waka, hakorinta ya kariye." Sa'anan suka zo suka taru, suna waka "Ga baba, Ga baba ba hakori." Sa'anan gizzo ya gudu wurin giwa, ya che "Giwa, kin ji karkeche suna yi maki zambo." Sa'anan giwa ta zo, ta che "Suna ungwa ne?" (1) Ya che "Ga su chana." Ya che "To, idan kin buga su,

ki bare pata ki yar abaya." Sa'anan giwa ta buge su, tana bugen su da hanun hanchi, tana bare masu pata. Gizzo ya dauke pata, ya taffi, ya boye tare da hakorin giwa. Sa'anan ya komo, ya tussa barkono achikkin koko, ya taffi ya samu zaki shina kwanche. Ya che "Na zo en yi maka maganin chiwun ido, na gani idanunka na chiwu." Zaki ya che "To." Gizzo ya sa masa barkono a idanu. Sa'anan zaki ya ji zafi, ya rufe ido, hawaye ina zuba. Gizzo ya tare su a koko. Ya che "To, zani gida kuma, sai gobe na zo zafi ya kare." Ya dauka koko, ya kama hainya zashi gida abinsa. Sa'anan ya dauke kokon hawayen nan, da patan karkeche da hakkorin giwa, ya zo wurin kamacha. Ya che "Kamacha." Ta che "Gizzo, ka komo?" Ya che "I." Sa'anan ta che "To, enna abinda ka samu? Kawo mu gani." To, ya kawo pata da hakori da hawayen zaki. Sa'anan ta che mashi "To, Shiga en koya maka dabara." Ta dauke kwariya baba, ta che "To, Gizzo, kwanta achikki en rufe ka en zo en kara maka dabara." Ta rufa shi. Sa'anan ta taffi woje, ta daka duchi, ta komo da shi. Da ta fitta, shi gizzo ya bude kwariya, ya fitta woje, ya koma kofan daki, ya boya. Ta dauko duchi, ta zo zata jefa a kwariyan nan wai ta kissa gizzo. Da ta jefa ta passa kwariya, gizzo ya che "Kwariyanki fa?" Ta che "Izan en kara maka dabara ka kare duniya." Ta kore shi. Ya gudu, ya bar kaya duk wurinta, sai kanto da ya boye a daji.

(1) Where are they. *See* Note IV. B.

---

## 115

### The Hyæna, the Scorpion, and the Goat.

Wanni ya tashi zashi wanni gari da ragonshi. Kunama ta che "Bar en zo en yi maka rakiya." Sa'anan kunama tana rikke da rago (1). Suka fitta woje, suka gammu da kura. Kura ta che "Bar en zo en yi maku rakiya." Sa'anan da suka tehhi wurin kwana, suka daura rago a jikkin itache. Kura ta che zata kwanta da nisa kadan, mai-akwiya (2) ya kwanta dabam da ragonshi, kunama ta kwanta kussa kussa da rago. Da dare ya yi tsaka, suna barchi, kunama ta tashi ta kwanta a wiyan ragonsu (3). Anjima kadan, sai kura ta che "Mai-rago, Mai-rago." Shiru. Sai ta che "Mai-rago." Ta kirra har so-uku, ya ki amsa. Sa'anan kura ta tashi, tana taffiya da hankali, tana zuwa

garin kaman rago. Da ta sa baki ta kama akwiya, kunama ta halbe ta a hanchi. Ta koma wurin kwanchiyanta chana, ita kura, kunama kuwa ta koma wurin nata. Sa'anan ta che "Kunama, Kunama." Ta che "Um." Ta che "Kin yi barchi?" Ta che "A, a, ban yi barchi ba." Ta che "Ni, za ni gida." Ta che "Ki hakura, gobe da safi mu taffi mu yanka nama mu yi sadaka, mu ba ki naki." Ta che "Ni, ba na zona ba, na taffi abina." Ta taffi, zafi ya same ta, ta yi ta gudu, tana kuwa "U, U" tana kuka. Tana zafi.

(1) "Da" appears to be unnecessary, as "rikke" can take a direct object.

(2) Should be "rago," an instance of Hausa carelessness. In the preceding story a ewe and a she-goat have the same husband. It is not often, however, that a ram and a she-goat are confused.

(3) Servants always say "our horse, our loads," &c., when referring to their masters' possessions.

---

## 116

### The Ungrateful Hyæna.

Wanni Ba-Filache ke nan. Shina da danshi, sunan dan Dan Makubibi. Sai ya taffi kiwon shanu, shanunsa dari. Sai dare ya yi mashi, sai yana waka, ya che "Ni Dan Makubibi, na yi daren kiwo." Sai suka gamma da kura, sai kura ta che "Dan Makubibi, ba ka ba ni sa daya en yi maganin kwadaye ne?" Sai ya che "A, a, ba ni ba ka achikkin wadannan ba, ba su da mai." Ya che "Sai gobe, almuru ya yi, na zo na daura maki awurin, abakin rijiya." Ya che zaya daura mata sa. Rijiya kuwa, tsakan hainya, hainyar kasuwa. Sai ya kawo duma, irinda akanfafe chikkinta akanyi kwariya da ita. Sai ya zo ya kewoya bakin rajiya da ita (1). Da zuwan kura, sai ta ga duma farifat, tana che shanu. Sai ta zo da gudu, ta fada achikkin rijiya. To, hainyan kasuwa, gada ta zo zata kasuwa. Sai gada ta zo, ta leka rijiya, tana so ta sha ruwa. Sai ta ga idon kura. Sai ta che "Op," ta che "Yau ruwa ya fi karifimmu." Sai kura ta che "Habba, Gada, zo ki yi mani rana." Gada ta che "A, a, ni ba ruwana, ni mai-guntul wuchiya." Sai barewa ta zo. Da ta leka, zata sha ruwa, sai ta che "Op, yau ruwa ya fi karifimmu." Sai kura ta che "Habba, Barewa, zo ki yi mani rana." Sai ta che "A, a, ba ruwana ni mai-guntul

wuchiya." Sai biri ya zo, ya leka, ya ga kura. Sai ya che "Op, yau ruwa ya fi karifimmu." Sai kura ta che "Habba, Biri, zo ka yi mani rana." Sai ya che "Kadda en yi maki rana ki mayar mani da dare." Sai kura ta che "Ba na yi maka ba." Sai ya mika mata wuchiyanshi achikkin rijiya, kura kuwa ta kama, ta fitto. Da ya fitto da ita, ya che "To, Kura, zani kasuwa." Sai ta che "Ba ka barri na bushe?" Sai ya che "A, a, abinda ni ke gudu ke nan." Da ta bushe, ta che "To, Biri, ba ka ba ni dan wuchiyanka kankani en yi maganin kwalima?" Sai ya che "To." Sai ta sa hakori ta deba kaman tsawan yasa. Sai biri ya che "Ya issa, zan taffi." Sai ta che "Ba ka barri en futa ba?" Sai biri ya che "Abinda ni ke gudu ke nan." Sai kurege ya zo, ya che "Ku zo en yi maku shera'a a gaton, itache." Sai ya che "Shera'an nan, kurege kuddis, biri darap, kura tawewe" (2). Da ta duba ta ga biri bissa, kurege ya shiga raminsa, ita kuwa ta kama hainya abinta.

(1) He went around the mouth of the well with it = he placed them (there were several, not only one as "ita" would imply) around the mouth of the well.

(2) Strange language so as to give the monkey a hint without letting the hyæna know until too late.

---

## 117

### The Girl who prevented the Beasts from Drinking.

Wannan guntul ne. Wota ke nan yariniya. To, akahaife mata kanuwa, sai su kan taffi gona, duk da uwan da uban da ita yar, su kan barri kanuwan achikkin tallen mai. Ashe kura ta zo gidan, sai ta ga tallen mai, sai ta dauke, ta hadiye. Sai akazo, ba agani yariniya ba, ko talle. Sai yan ta yi kuka, amma ta che ta ga wanda ya dauke mata kanuwan achikkin talle. Sai akwai wanni ruwa wurinda naman daji duka suna shan ruwa, sunansa Barri-Gudu. Sai yan ta debo ruwa duka, ta hau bissa kuka da shi, ta barri tabbo. To, duk naman daji su kan sha ruwa awurin. Sai zaki ya fara zuwa, tana waka, ita yan, ta che "Kai Zaki, enna zaka?" Sai zaki ya che "Zani Barri-Gudu en sha ruwa," sai ta che "Da ka ba ni kanuwana da na ba ka ruwa ka sha." Sai ya yi "Hakk," (1) ya che "Kin ga

abinda na chi, Hakk kin ga chiyawa ne." Sai yan ta che "To Kuka, taffi da ni bissa." Sai kuka ya kara tsawo. Sai bauna ta zo, sai ta che "Kai Bauna, enna zaki?" Sai ta che "Zani Barri-Gudu en sha ruwa." Sai ta che "Da kin ba ni kanuwana da na ba ki ruwa ki sha." Sai ta yi "Hakk," ta che "Kin ga abinda na chi, Hakk kin ga chiyawa ne." Sai yan ta che "To Kuka, taffi da ni bissa." Sai kuka ya kara tsawo. Duka naman daji suka zo, duk ta tambeya su hakka. Sai duka suna kwanche, kishin ruwa yana so ya kasshe su. Sai kura ta zo dagga baya duka. Sai ta che "Kura enna zaki?" Sai kura ta che "Zani Barri-Gudu en sha ruwa," sai ta che "Da kin ba ni kanuwana da na ba ki ruwa ki sha." Sai kura ta yi "Hakk," talle ya fitto da kanuwan achikki. Sai yan ta che "Na sani ke ne mai-kwadaye, ke ne kin dauka kanuwana." Sai ta che "To Kuka, koma da ni kassa." Sai ta zo ta ba su ruwa, suka sha. Sai ta dauke kanuwa ta mayar a gida. Iyakan wannan ke nan.

(1) The lion vomited.

---

## 118

### The Cunning He-goat, the Hyæna and the Lion.

Wanni bunsuru ya che shi ya san dinkin kwariya. Kullum yana wuchewa kofar gidan kura. Kura tana so ta tambaya shi, ta ji tsoro. Ta taffi gidan zaki, ta che "Bunsuru ya kan bi kofar gidana kullum," ta che "ina so en tambaya shi aikinda ya ke yi, ina jin tsoronshi." Sai zaki ya che "To, en ya sakye komowa, ki kirra shi, ki zo wurina." Ta che "To, izan ya zo, ka passa kasko ka che ya dinka, izan ba ya dinka ba ka che ni zan kama shi." Sai ya che "To." Sai kura ta koma gida. Bunsuru ya zo, sai ta che "Kai, Gadanga Wandawa ina kirranka." Sai ya che "To, mu taffi." Da zuwansu, sai zaki ya passa kwasko (1), sai ya che "Enna aikinka?" Bunsuru ya che "Ni mai-dumkin[1] kwariya ne." Sai zaki ya che "To, ga kaskona ya passhe, en ba ka dumka ba zan sa kura ta kama ka." Dagga nan sai kura ta che "Kai (2) dunke?" Sai bunsuru ya che "Habba, Kura, pada ne? Ai zan yi." To, shi kuma, shina da wanni dan kurtu ya zuba zuma achikki, shi bunsuru. Sai ya che ma zaki "To, abin dunke sai da jijiyan kura, enna za'asamu?" Sai zaki ya che "Ai, ga kura." Sai zaki ya che

"Kai Kura, kawo dan jijiyanki kadan." Sai kura ta sa hanu ta sinke dan jijiyan kaffanta, ta kawo, ta ba zaki. Zaki kuwa ya ba bunsuru. Bunsuru sai ya dauke dan jijiyan nan, ya saka chikkin zuma. Sai ya fitta da ita dagga chikkin zuma, ya mika ma zaki, ya che "Ga shi, ka shafe yawo, ka ba ni en para dinke." Sai zaki da ya sa baki, sai ya ji zakin zuma, sai ya hadiye. Saï bunsuru da ya hadiye, ya che "A, enna zan samu dan jijiya?" Sai zaki ya che "A, ga kura." Sai zaki ya che ma kura "Kai, debe dan jijiyanki kadan." Sai ta ba zaki, sai zaki ya ba bunsuru. Sai bunsuru ya sa achikkin zuma, ya ba zaki, ya che ya shafe yawo, ya ba shi. Ya che "Ai, kadda ka hadiye wannan kumá." Sai zaki, da ya dauke, sai ya hadiye. Sai bunsuru ya che "A, enna za'asamu dan jijiya kadan?" Sai zaki ya che "A, ga kura." Sai kura ta tashi da gudu (3), sai zaki ya bi ta, kura ta tsere dakat. Bunsuru shi kuma ya gudu, ya yi ma kura wayo ke nan.

(1) The storyteller often pronounces the same words differently. See also "pa" and "fa" in story 114.
(2) Kai = ka iya.
(3) With running = at a run.

---

## 119

### The Hyæna and the Wrestling Match.

Kura de ke nan. Tana da mijinta kure. Sai ta tashi ta dauke tulu, zata rafi. Sai ta je ta iske anawasa (1), da giwa, da bauna, da kanki, da gwanki, da barewa, da kurege, da zomo, da sari, da gaza. Sai suna wasa. To, giwa ita ne baba mai-shera'a. Sai ta che "To, wasan kukuwa, wanni ya kada wanni ya chi naman wanda ya kayar." To, da zuwan kura, sai sun che "Ba ki zuwa ki yi wasa?" Ta che "Ina yi manna." Da saukan tulunta, sai akagamma su (2) kukuwa da barewa. Da ta dauka bup, ta kayar akassa. Sai giwa ta che "Ai, je ki da shi, namanki, kin kayar." Da ta taffi, sai ta iske mijinta, sai ya che "Enna kin samu nama?" Sai ta che "Allah wadanka," ta che "Ga shi, anawasan kukuwa chan, wanda ya kada wanni ya dauka nama ya chi. Sai kana zone?" Sai ya che "Anayi yanzu?" en ji kure. Sai ta che "A, a, sun tashi, sai gobe." Ya che "To, Allah ya kai mu gobe." Yana murna. Gari ya waye, ba ya barchi ba, sai da sasafi ya che "Sun zo wasa?" Sai ta che "A, a,

sai da azuhur." Sai yana murna. Da azuhur ya yi, ya para zuwa pagen wasa, ya daura gwalji ashirin a gindi. Da zuwansu, sai suka che "A, yau anyi bako dan kukuwa." Sai giwa ta che "To, dan kukuwa ya shiga page, mu gani." Sai ya shiga page, yana rawa, yana rawa, yana rawa, sai ya mika hanu ma giwa, giwa ta kama shi kukuwa. Sai giwa ta che "Ka chikka karambani, ba ka nemi yara kankanana?" Sai ya mika ma bauna hanu, sai bauna ta che "Ka chikka karambani, taffi ka nema dan kankani." Sai suka che "A, wannan dan kukuwa." Sai giwa ta che "Mu tura mashi kurege, mu gani da gangan." Sai giwa ta che "Ga kurege, ku yi kukuwa." Sai kure ya che "Kai, kuwa rena ni." Sai giwa ta che "Ku yi de." Da zuwan kurege sai ya jefe shi bissa, sai ya bude baki, kurege ya fada chikkin baki. Sai ya hadiye. Sai ya mika ma gwanki hanu, sai ya che "A, a, kankanana ba sun kare ba." Sai akache "Gaza, fitta ki yi kukuwa da shi." Sai gaza ta che "To." Da gaza ta fitta, sai kure ya jefe ta abissa, ya bude baki, zaya yi mata kaman na kurege. Gaza, da ta komo dagga bissa, sai ta kama makogoro. Sai kure ya fadi, yana che "Wayo, wayo." Sai kure ya fisge, ya yarda gaza. Sai giwa ta che "To, ayi ma gaza gudumawan nama." Sai kure ya tashi da gudu, ya tsere dakar. Sai ya zo, ya gaya ma matanshi, ya che "Ke, Mata, halinki ba keyau, kin che anawasa, ga shi, anso akasshe ni achan." Sai ta che "Kai, de, malalache ne, ba ka chi naman barewan nan, ko kasshi."

(1) A good example of elimination.
(2) Su. Plural instead of singular.

---

## 120

### Why Dogs and Hares do not Agree.

Da kare da zomo suka yi abuta akauyen gari. Sai zomo ya che wa kare "Abutammu da kai ta yi yawa, zan kai ka garimmu, duka gari zomo ne, birnin zomo." Zomo ba ya iya daukan kare, sai ya ja akassa achikkin bargami. Da ya je, zomo duka suka yi mashi marhaba, suka che "Wanni irin kaya ka dauko?" Sai ya che "Kayan magani ne." Suka che "Kawo akarbe ka." Sai ya che "A, a, izan akarbe ni, magani ya kare ke nan." Da anyi abinchi, sai ya deba ya sa chikkin bargami, ya ba kare ya chi, har suka kwana biyu agarin. Sai

zomo ya che wa kare "Zan komo da kai kauye inda mu ke yi abuta." Sai yana jan bargami akassa da kare achikki, sai suka zo gwonan kura, kura tana aiki da yayanta. Da zomo ya ja kare, ashe sun taushe ma kura dawa. Sai kura ta che "Wanene zaya kariye mani dawa?" Sai zomo ya che "Ke Kura, halinki ke nan, ba ki so alheri?" Sai kare ya ji hakka, sai ya fitta bup dagga chikkin bargami. Sai ta che "Zan je en gani wanda suka kariye mani dawa." Da suka gane ta (1) tana zuwa, sai zomo ya gudu, kare ya gudu. Sai kare ya koma kauye inda su ke yi abuta da zomo. Kare ya iya saka, ya zona, yana saka a kauye. Sai kura tana bin su, sai ta zo, ta iske zomo a gainye, yana kwanche. Sai ya tashi bup, ya iske kare wurin saka. Sai ya che "Kare, kana saka ne? Kawo en karbe ka." Sai kare ya che "To, ni ma na gaji, sai ka hau, ni ma zan futa." Kare ya kwanta, yana futu. Sai kura ta zo, ta che "Achikkin ku wa na koro?" Sai zomo ya che "Wa kina ga yana lumfashi?" Sai ta bi kare da gudu, sai kare ya tsira dakar. Sai ya che "Um, ni kare, dakar na tsira ya fi dakar akakama ni." Sai ya che "Amma, na gammu da zomo. Na yi abuta da shi ya chi amanana."

Mafarin gabansa da zomo ke nan.

(1) The usual form is "gan ta."

---

## 121

### The Dog, the Salt, the Cake, and the Hyæna.

Kare da dadowa da gishiri suka tashi zasu bakonchi. Da suka iske kogi ruwa ya kawu, sai dadowa ya che ma kare shi fishe shi. Sai ya ki, sai dadowa ya ba shi hakuri. Da ya ba shi, sai kare ya dauke dadowa, zashi yi mashi fitto. Sai en ya taffi chikkin ruwa ya tsoma dadowa. Dakat dadowa ya fitta. Ya taffi ya aje dadowa a rana. Sai ya komo wurin gishiri, sai ya dauke gishiri, ya taffi ruwa. Sai ya jikka gishiri a ruwa. Da ya jikka gishiri, ya narike, ya bi ruwa, kare ya haye, ya zo wurin dadowa. Sai ya che su taffi kuma. Suka tashi suka taffi, suka taffi gwonan kura. Sai dadowa yana dauken bargami. Sai kare ya che "Bar en shiga bargami." Sai kare ya shiga. Da ya shiga, ya che dadowa ya dauke shi. Sai dadowa ya che shi kuma zaya rama. Kare ya che kadda ya bi da shi

achikkin gwonan kura ba. Sai dadowa ya dauke shi. Sai ya bi da shi achikkin gwonan kura. Da ya bi da shi, sai shina bangajen kwiyoyen gwona. Sai kare ya che "Habba, kadda ka bi." Sai kura ta che "Suwanene nana?" Dadowa ya che "A, mu ne." Sai ta che "Da ku da wane?" en je kura. Sai ya che "Da mu da kare." Sai kura ba ta ji ba. Sai suna taffiya, suna taffiya, dadowa shina bangajen kwiyoyen gwona. Sai kura ta che "Kai, wanni irin mutane kana?" Sai dadowa ya che "Mutum da kayan kare ba zaya kasa ratsen gwonan kura ba." Sai kura ta che "Kun che mine?" Sai dadowa ya che "Ina da kayan kare ne." Sai kura ta je, tana zuwa aguje, sai dadowa ya yarda kare. Sai dadowa ya gudu, ya bar kare nana, kura ta zo ta daka. Da ta daka, ta taffi, ta rassa wuta. Ta bar ma yayanta. Da ta bar masu, sai ta taffi neman wuta. Sai kare ya che ma yayan "Kun tabba ganin hanchina?" Sai yayan suka che ba sun gani ba. Sai kare ya che "Bude kadan en nuna maku hanchina." Da suka gani sai suka che "To, koma, mun gani." Ya koma. Ya che "Kun tabba ganin kaina?" Suka che ba sun gani ba. Sai ya che "Bude kadan ku gani." Da suka gani, sai suka che "To, koma, mun gani." Sai zuwa anjima kadan, ya che ko sun tabba ganin sawunshi. Suka che su ba sun gani ba. Ya che "To, bude kadan en nuna maku." Da sun gani suka che "To, mun gani, koma." Ya koma. Anjima kadan ya che "Tun da ku ke kun tabba ganin guduna?" Suka che ba sun gani ba. Sai ya che "To, bude kadan kuwa gani." Da suka bude ya yi sheka da gudu, sai kare ya taffi abinshi. Da ya taffi, uban ya komo, ya zo ya gani kare babu. Sai ya kama yayan da duka har ya kasshe su. Kare ya taffi, dadowa ya taffi nashi (1) woje dabam. Kare yana neman shi.

(1) It is unusual to find the passive pronoun before the noun. The hyæna has changed its sex.

---

## 122

### The Hyæna and the Bitch.

Da kura da kariya. Sai suka tara gida adaukan daji. Wannan ga nata rami, wannan ga nata dabam. Sai shi ke nan, har suka yi chikki, suka haifu. Ananan, sai kura ta che "Kariya, en mun je daji ba mun samu komi ba, mu zo ki kama danki

daya, ki yanka mu chi." Sai kariya ta che "To." Sai da suka je suka komo, ba sun samu komi ba, sai kariya ta zo ta kama dan kura, ta yanka. Sai ta yi abinchi, suka chi. Shi ke nan sai washen gari suka je daji, suka komo, har yanzu ba su samu komi ba. Shi ke nan sai kariya ta zo, ta kama dan kura, ta yanka, sai suka chi. Har yayan kura shida suka kare. Shi ke nan sai kariya ta je ta nema yayanta gu, sai ta aje su abissa bishiya. Ta che "En kun ji na che 'Yayana sur' ku sauko igiya en hau." Sai kariya ta koma gidan kura, sai ta che "Yayana sun kare, ko mu je mu kama naki mu chi?" Sai kura ta che "A, a," sai ta taffi raminta ta duba, ba ta ga komi ba. Sai shi ke nan, sai kura ta farfaro kariya, kariya sai gidanta. Da ta je, ta che "Yayana sur." Sai yaya suka sanka igiya, ta hau. Sai akabar kura akassa, yawo yana zuba. Sai kura ta taffi gidan mallami, sai ta che "Mallam, ba ka yi mani abin aduwa ba en na je na che 'Yayana sur' su sauko mani igiya en hau ba?" Shi ke nan sai Mallami ya che "To, zam ba ki," ya che "amma en kin gan kasshi, kadda ki dauka ki chi." Shi ke nan sai kura amba ta laiya. Da akaba ta laiya sai ta taffo, sai ta ga kasshi a hainya. Tana yunwa, sai ta chainye. Sai ta taffo gidan yayan kariya. Da zuwanta, sai ta che "Yayana shi." Sai yayan sun che "Ai, mun san ki de, ke che kura" (1). Sai kura ta koma wurin mallami. Sai ta che "A Mallam, magani ba ya chi ba." Sai ya che "Ai, na gaya maki en kin gan kashi kadda ki dauka." Sai ta che "To." Sai ta komo. Da zuwanta sai ta che "Yayana sur." Sai yayan karnuka sai suka sauko igiya. Da ta kussa hawa, sai yayan kariya suka ga kura che, sai suka sauke ta kassa, sai kura sai ta zo ta kaffe, sai ta zammi turimi. Sai shi ke nan, sai kariya ta zo ta gani. Da zuwanta, sai ta che "Sur Yayana" sai suka ja ta, ta hau samma. Sai yayan suka gaya mata labari.

(1) Very correct, but very unusual.

---

## 123

### The Cunning Goat and the Hyænas.

Bunsuru ne de. Ya tashi taffiya da sasafi, sai ya debi raba. Sai ya che zashi kasuwar kura zaya chi. Iya taffiya, ya gamma da kura, sai ta che "Bunsuru, enna zaka?" Sai ya che "Bar gaya min 'Bunsuru,' ni Allah ne." Shi ke nan,

sai ta che "En kai Allah ne, yi min ruwa en sha." Sai ya girgiza jikkinshi, sai ruwa ya fitto. Shi ke nan, sai kura ta taffi. Da ta taffi, sai ta dada koma (1) gun bunsuru, ta che "Kariya ne, en kai Allah ne kara min ruwa." Sai ya dada karkada jikkinshi, sai ruwa ya fitto. Sai ta che "To, je ka." Shi ke nan, sai ya tarada kuraye, sai suka farfaro shi aguje. Sun koro shi. Ya gudu har ya gamma da zaki. Sai zaki ya che "Bunsusu enna ka je?" Sai bunsuru ya che "Na chiwo kasuwar kura." Ya che "Da mi da mi ka sayo?" Ya che "Da fitsarin kura da kashi, dadi kuwa gare su" (2). Shi zaki ya che "Ba ni, en tabba en ji." Sai bunsuru ya ba shi zuma da nakiya. Sai zaki ya tabba, ya ja dadi. Shi ke nan, kuraye suna bin bunsuru zasu kama. Shi ke nan, sai zaki ya yi kirran kura. Sai ya che "Kura ya ki." Sai kura ta zo. Ya che "Yi min fitsari da kashi irin naku en ji. Shi ke nan, sai ta che Ai, ba mu da wanni kashi mai-dadi." Sai ya che "Kariya ki ke yi." Sai ta che "Allah kuwa, ba kariya ni ke yi ba." Sai ya kama kura ya matse. Si kura ta yi mashi fitsari. Ya tabba ya ji. Sai ya che "Dan-durinuwarki, da wanni mai-dadi." Sai shi ke nan, sai ya matse ta, ya matse ta, sai kura, ta mutu. Sai zaki ya taffi. Da ya taffi sai waddansu kuraye suka bi bunsuru zasu kama. Sai suka tarada bunsuru a gidanshi. Sai bunsuru ya che "To, ku tsaya, ina bin sarikin pawa kurdi." Ya che "En na karba, mu je en sayo maku nama." Sai suka che "To, mu taffi." Sai suka tarada irin tarkonnan da ya ke kaman naman daji. Tarko kuwa, andaura mashi chiniyar akwiya. Shi ke nan, sai ya che "To, ga shi, ku yi magana da shi, ya ba ku, ku taffi." Sai dayan kura ta che "Kai, Sarikin Pawa, ka ba mu manna mu taffi." Sai sarikin pawa ya ki magana (3). Sai kura ta yi farada chiniyar akwiya ta kama, sai tarko ya rikke kura. Sai yar-uwa sun gudu, sai bunsuru ya taffi. Sai dagga nan sai musu-tarko suka ji kukan kura, sai suka zo, suka fitta da ita, sai kura ta gudu. Sai ta je ta fada na iyayen kuma. Sai suka che "Ai, sai ki raba da bunsuru, en ba hakka ba sai ya kasshe ki." Shi ke nan, ta rabu.

(1) "Kara (or sakye), komowa" would be much more usual and correct.

(2) "Sweetness to them."

(3) A very graphic manner—as if the head of the market were really there.

## 124

### The Old Woman, the Hyæna, and the Monkey.

Biri ke nan. Kure ta je daji, ta ga wurin mai-keyau, ta che zata yi gida. Sai biri ya zo, shi kuma ya che wurin ya yi keyawun daki. Ya nomi wurin. Sai kura ta zo, ta che "Wanene ma-soyena ya nomi mani wurin daki?" Sai ta gina daki. Biri ya zo, ya che "Wanene ma-soyena ya yi mani daki?" Shi kuma ya yi jinka. Dare ya yi kuma, wota tsofuwa (Ta Sakala, mainki a kaure, kasshi pal kwando, mainki danki) ta zo ta shiga daki, hainyan kasuwa ne. Biri da ya zo, shi kuma ya dibi gada ya shiga daki, ba ya san tsofuwa ina nan ba. Sai kuma kura ta debo (1) bangan doki ta shiga, ba ta san biri ina nan ba, ba ta san tsofuwa na nan. Tsofuwa kuwa ta san suna nan, tana ganinsu. To, biri, en ya passa gada ya chi biyu, ya mika hanu zaya aje a swako, sai tsofuwa ta karba. Ita kura kuma ta che naman doki zata boye saura, sai biri ya karba. Da biri ya karba, shi kuwa ya mika a swako sai tsofuwa ta karba. To, tsofuwa, mai-karambani, ta che "Yara suna mani keyauta, mine zan ba su? Bar en ba su sako guzurin kasuwa." Su ba su sani tana nan ba. Sai ta mika muruchi, ta sa achikkin kworimin biri. Sai birri ya fitta bubup aguje, sai kura ta fitta bubup aguje. Sai sun ga junansu. Sai suka che "To, ayi gaya akan abinda ya ke chikkin daki." Sai akayi gaya da giwa da bauna da zaki da baziya da zomo da kurege da jimina. Sai kura ta che "Kowa zaya ga abinda ya ke chikkin dakin nan, sai em ba shi zambar dari." Biri kuwa ya che kowa zaya ga abinda ya ke chikkin dakin nan sai ya ba shi zambar dari. Sai akache "Wa za'asa achikkin daki?" Sai jimina ta che ita ta shiga. Ta che adaure jikkinta da igiya, en ta shiga su kuma suna jaya da igiya abaya. Ta che "En de kun je na che 'Ku ja'—ku ja." Jimina da ta shiga, sai tsofuwa ta kama wiyanta. Sai ta che "Ku ja." Suna ja, tsofuwa tana ja, sai tsofuwa ta yanke kain jimina. Sai jimina ta fadi ba kai, sai suka passhe. Awurin gudu sai giwa ta taka zomo da baziya da kurege, sai suka mutu, sai tsofuwa ta fitto a daki, ta debo nama. Ta gaji dakin kura ke nan da na biri.

(1) All the vowel-sounds in this word may change.

## 125

### Why the Hyæna and the Donkey do not agree.

Kura ke nan da jaki, abinda ya gamma su fadda. Kura ta che ma jaki " Wegawa da ka ke yi, ka wega kudu ka wega ariwa, mi ka ke samu?" Sai jaki ya che mata " Duka wegewa da ni ke yi, awega kudu anaba ni tsokar nama, awega ariwa anaba ni tsokar nama." Sai kura ta che " Ai, da gaski jaki ba ka rama, kullum da rani da damana kana kibba tibir tibir." Sai ta che " To, ni kuma yaya zan yi en samu?" Sai ya che " Abarri sai mun sauka, ki zo ki kwana achikkin mu." Sai ta che "To." Sai tana Allah Allah dare ya yi (1). Sai ta shiga achikkin jakuna, ta kwanta. Da gari ya waye, akache " Ajawo jakuna, asa masu kaya." Da akasa masu kaya duk, suka kare, sai ta che ita ba ta samu ba. Sai akakarbe kayan wanni dan jaki wanda ba ya iya kaya, akaba ta. Shi ke nan, da suna taffiya, sai akaduke ta so-daya. Sai ta wega kudu, ta wega ariwa, ba ta ga tsokar nama ba. Sai ta che " Kai Jaki, har yanzu ban sami komi ba." Sai jaki ya che "Ke, Kura, tun rana ba ya yi, za'aba ki karen kalache? Ai, sai rana ya yi," en ji jaki. Sai kura ta che "To." Sai suka kara gushi, kuma akadoke ta da itache. Sai ta wega kudu, ta wega ariwa, ta che " Kai Jaki, ba zan samu kalache ba ne? " Sai jaki ya che " Habba, Kura, kina garaje." Sai ta che " To, yau de na yi kokari na yau daya" (2). Sai suna taffiya, suna taffiya, akafiyada ita da tsumanjiya. Sai ta che " Jaki, ni kuma zan zubar da gudu." Sai jaki ya che " Habba, Kura, dummi? " (3). Sai kura ta che " Op, kowa kaman ka ne, Babam Banza?" Sai jaki ya che " To, ki kara kadan em ba ki ga amba ki ba, sa'anan ki gudu." Ta che " To, wannan kokari sabada kai zan yi." To, ashe kura ta fara gajiya, harshinta ya fitta. Sai masukaya suka che " Op, yar-durinuwa kura, ba ta da taffiya?" (4). Sai akayi mata taruwa da sanda (5). Da kura ta samu kanta sai ta zubar aguje. Sai ta che " To, Jaki ko a Lahira kadda Allah ya gamma mu da kai." Abinda ya sa su gaba ke nan.

(1) She was impatient. " O God, O God, may night come soon."
(2) For to-day only.
(3) Dummi = dun mi = don mi = domi.
(4) Has she no go, *i.e.*, cannot she travel ?
(5) Blows (sticks) were heaped upon her.

## 126

### The Lambs, the Hyæna, the Jackal, and the Jerboa.

Yan tumaki suka je wanka, sai kura ta tashi, ta zo chikkinsu, sai ta che ita zata yi wanka tare. Sai ta kan kama daya, ta kan dana achikkin ruwa ta kariye wiya ta boye. Sai kumadu ta kama wota, ta sa wanni ma-boye, har ta kasshe guda goma. Da tumaki suka fitta zasu taffi gida, sai suka ga ba goma achikkinsu. Sai suka che " Wankan nan ba ya yi mamu dadi ba, ba zamu kara wanka da kura ba." Shi ke nan, sai da dare kura ta dawo, sai ta shiga ruwa, en ta fitta woje da daya en ta aje, ta koma ruwa. Sai dila sai ya zo, ya dauke, sai ya je daji da nisa ya boye. Sai komadu ta fidda daya, en ta komo ruwa sai dila ya dauke. Sai kura sai sauranta daya a bakinta, sai ta che wa ya yi mata aikin nan? Sai ta dangana, ta taffi abinta gidanta. Sai kurege ya kawo mata albishir, sai ya che " Kura, mi zaki ba ni en na gaya maki enda nama su ke?" Sai ta dauko jika daya ta ba shi, sai ya dauka, ya kai dakinsa. Ta che " En ka je ka kai ni wurin namana en na samu, zan kara maka jika guda." Ashe, jikan nan jikan tusan kura ne, ta yi achikki, ta kama, ta daure. En ba ta da nama sai ta matse tusa achikkin miya ya zamma kaman kwado. Lokachin nan sai ya che " To, en kai ki wurin namanki." Suka je gun dila. Da suka je, kurege ya che " Sai ki kwanta nan kaman kin mutu." Sai ta yi kwanche. Sai ya je ya samu dila, sai ya che " Ga wanni naman daji ya mutu." Sai ta che " Op, jiya na halbe shi." Sai ta fitto, ta che " Wuche gabba ki kai ne wurin nama." Sai ya taffi yana kirare a kibiyansa, yana che shi mai-zubge ne mai-karewa dangi. Lokachin nan sai suka zo kan kura. Shi dila ba ya san kura ne ba, tana chikkin bunu. Sai kura ta tashi bup sai ta kama dila. Sai ta che " Mu je, ki kai ni wurin namana har ke" (1). Shi ke nan, dila de ta kai ta wurin namanta. Da ita da nama duk sai kura ta chinye, ta ba kurege daya achikkin ringi.

(1) My meat, including yourself.

127

WHY THE HYÆNA AND THE JERBOA CANNOT AGREE.

Kura da kurege suna aboki (1). Ya che "Kura, na ga gida da yam-mata, ni na taffi na nema daya, ke kuma ki nema daya, mu yi aure." Sai kura ta che "To." Sai kura ya same salka ya zuba kurdi achikki, kurege kuma sai ya zuba iska achikkin nasa. Da suka kussa, sai kurege ya che "To, Kai baba ne, kayanka na kurdi da nauyi, nawa da tufafi ne ba nauyi." Da shi ke kai baba ne, ka dauke nawa en dauke naka. Kura ya che "To." Da suka kussa da kofar gida, sai kurege ya che "Kura, albishirinka?" Ya che "Gidan da dakin awaki da dakin kaza, ni zan sauka dakin kaji, kai a dakin awaki." Kurege ya che "Chikkin daren nan na chi kaza biyal." Kura ya che "A, a, ni ba na iya hakka, gidan sarakuwa na chi daya." Da suka zo suka yi sallamma, akache "Marhabanku marhabanku." Da suka zo, kowa ya nuna kayanshi dabam. To kurege, da ya karbe kayan kura, ba ya mayar masa ba, ya yi nashi da shi (2). Kayan kurege na iska, awurin kura, ya zamma nashi. Da akaga kayan kurege na kurdi, sai akache "Ai wannan ya zo da gaskiya." Sai akakwanche kayan kura, sai iska ya fitta, sai ya bar salka falemin. Sai suka che "Wannan yawon zambar ya kawo shi." Sai akache "To, aba su masauke." Sai akache "To, ga dakin kaza, ga dakin akwiya, kowa ya zabe wurinda zaya kwana." Sai kura ya farada baki. Ya che "Ni, sai dakin akwiya." Sai kurege ya che "To, ni ma, na kwana dakin kaji." Ashe kurege yana so bada kura, akashe shi. Da suka shiga daki, sai kurege ya fitta, ya taffi wurin masu-gida. Ya che "To, ni, duk enda zani da zuchiya daya ni ke taffiya." Sai ya che "To, yanzu kun gani kun sauka da ni a dakin kaji, kura kuwa a dakin akwiya. Izan gari ya waye, ku che 'Kajin gidan nan ba mu san iyakachinsu, zamu kilga su. Da ankilga, asamu guda ayanka ma baki tuwo.'" Ya che "Ku che kuma 'Awakin gidan nan ba mu san iyakachinsu, mu kilga su, en baki zasu gida asallame su da bunsuru.'" Da gari ya waye akabude dakin kaji, akabude dakin awaki. Sai kurege ya che "Wai za'akilga kaji." Sai kura ya che "En ankilga kaji har akwiya za'akilga su?" Sai kurege ya che "Hakka ne na je suna fada." Da akakilga kaji, duk sun chikka, kurege ba ya chi ba, akache "Akilga awaki." Sai kura fa ya ji, sai ya che "Kurege ina jin zawaye." Sai ya fitta bayan gida. Sai kurege ya che da mutanen gida "To kun gani mafarin munafikinsa ba?" Da akakilga awaki, ba daya, sai akakirra samari, akache "Ku zo

mazza ku bi kura." Sai suna kirra, suna che "Kura ka zo wurin zanchen aurenka." Sai ya che "A, a, na passa." Sai akache "To ansan abinda ya yi, abi shi ahalbe shi." Da ya wega baya, ya ga anabin sa da baka, sai ya zubar da gudu. Sai ya tsere dakat. Ya che "Tsakanin mu da kurege ke nan." Ya che "Amma kurege ma muwa gammu da shi." To, abinda ya sa gabansu da kurege ke nan, abinda ya sa kurege ina tsira wurin kura sabada rame.

(1) "Aboki" is sometimes used for friendship, but "abuta" is a better word.

(2) "Made his own with it," *i.e.*, "pretended that it was his."

---

## 128

### Why the Donkey lives in the Town.

Jaki duk achikkin naman daji shi ne baba, en ji shi. Ya che en ya fitto daji, naman da zaya kasshe ba iyakachinsu. Kura ya che a, a, shi ne baba. Sai jaki ya che "Kura, ka taffi gobe, ka duba inda nama suka taru, sa'anan ka zo ka gaya mani." Kura ya che "To." Da safi kura sai ya taffi neman gunda nama suka taru. Da ya je ya tara da, su (1) giwa, su bauna, su maraya, su gwambaza. Nama sun taru dayawa, duk sun taru wuri daya. Sai kura, sai ta komo, ta gaya wa jaki. Sai ya che ta wuche ta kai shi gu. Suna taffiya, suna taffiya, suna taffiya, har suka zo wurin. Sai ya che "Kura, ki koma baya ki zamna har na kirra ki, ki zo ki chi nama." Sai jaki ya taffi, yana sanda sanda kadda naman daji su gan shi. Da ya yi kussa, sai ya fitto bup, ya yi "Hoha, hoha, hoha," irin kukanda su ke yi. Sai giwa ta ji tsoro ta gudu, ta taka bauna da maraya da gwambaza, da waddansu kaman dari ta kasshe, ringin suka gudu. Lokachin nan sai ya che da kura "Ya ki." Da kura ta zo, ya che "Ga shi duk abin nan na kasshe." Sai kura ta che "Tabas kai abin tsoro ne, kai ne sarikina." Kura tana tsoron jaki, kullum suna taffiya tare da kura. Tana che ko (2) kunensa kafo ne. Sai ran nan, sai ta che "En tabba kafon nan naka en ji?" Sai jaki ya che "Ga shi." Da ta tabba, sai ta ga abin ba tauri, sai ta che "Ashe, abin naki ba kafo ba ne?" Sai ya che "I, (3) kune ne." Sai ta che "To, dakeyau." Sai ran nan da almuru, jaki ya je, ina kiwo, sai kura ta daka sura, ta zo ta chiri tsuliyan jaki. Jaki da ya ji chiwu, ya gudu sai

chikkin gari. Da mutanen gari suka gani, suka kama, suka che sun yi jaki. Tun dagga wannan, jaki ba ya komo daji ba.

(1) Plural where we should use the singular.
(2) Saying or thinking.
(3) Where in English one would (incorrectly) use a negative.

---

## 129

### The Jackal and the Dog at the Marriage Feast.

Kare ya zo, ya che da dila " Anyi aure a gidammu jiya," ya che " Mu taffi dakin amariya mu sha mai, mai yana nan dayawa, mu taffi mu sha." Suka zo, suka shiga daki wurin mai, suka rikka sha, suna sha, suna sha, suka dosa (1) sha. Da suna sha, dila mai-wayo, shi kan fitta woje shi zo shi gwoda kofa ko kadda chikkinsa ya yi girima har ya hanna shi fitta. Kare ma, tun da ya shiga, ba ya fitta ba. Har masu-daki sun ji motsi, sun che " Wanene a daki ?" Suka fitta woje. Dila ya fitta, kare ya zo ya kasa fittawa, chikki ya hanna. Mutanen gida suka zo, suka buge kare da gaski, har kare ya yi masu wayo, ya kwanta kaman ya mutu. Da suka gani kare ya mutu, suka yas. Kare ya faraka (3), ya tashi, ya gudu.

(1) " Dosa," " dinga," and " rikka " all mean " to keep on doing."
(2) " He made to them cunning," *i.e.*, " he played them a trick."
(3) Or " falaka."

---

## 130

### The Contest of Wits between the Dog and the Jackal.

Dila da kare ke nan, suna yin aboki. Dila ya tambaya kare, ya che " Dabaranka nawa ? " Kare ya che " Goma sha biyu." Ya che " Naka nawa ? " Ya che " Sai daya." Sai dila ya che " To, mu zo mu taffi yawo, mu ga dabaranka." Sai suka taffi, suka iske kura ta taffi yawo, sai suka shiga gidanta. Sai kura ta dawo, sai ta che " A, Marhaba Dila." Sai dila ya che " Na zo gaishe ki ne, na yi baki" (1). Ya nuna mata kare, ya che " Ga abinda baki suka kawo mani guda goma, na kawo maki daya." Sai kura ta che " Madallah, Dila." Sai dila ya tambaya kare ya che " Kai kare, achikkin dabaranka goma sha

biyu saura nawa?" Kare ya che "Goma." Sai dila ya che da kura "Amma ki dube shi, ki gani, ku gamma ido kadda ki rena." Da kura ta duba kare suka gamma ido, sai jikkin kare duka yana rawa. Sai dila ya che mashi "Kai Kare, dabaranka saura guda nawa?" Sai kare ya che "Ai, sauran biyu." Sai dila ya che "To, gaya mani biyun nan en ji." Sai kare ya che "Dafari ne da anmatsa ni zan yi kuka, da kuma da ansakye matsa ni da karifi sai na yi kashi." Sai dila ya che "To, ka ga dabarana daya ya fi naka goma sha biyu." Sai ya che ma kura "Na yi shawara." Sai kura ta che "Wanni irin shawara?" Sai dila ya che "Ni mai-abu goma na kawo maki guda daya, ke kuwa aminiyana ne? Sai en koma gida da shi yanzu, en kawo maki uku dun guda daya ke ki ke chi (2), guda biyu ki ke ba yayanki." Sai ta che "To, madallah, je ka ka kawo." Da suka fitto kofar ramin kura, sai dila ya che "To, kawo wannan daya en je en chikka maki biyu." Sai kura ta che "A, a, barri dayan nan, ka je ka chikka biyu." Sai dila ya che "A, a, ba na yi hakka ba, en ba na koma da wannan, saura zasu gudu." Sai kura ta che "To." Sai ta kawo kare kofar rami, sai kare ya zubar da gudu. Sai dila ya zubar da gudu. Sai ya je ya kwanta kusa da gusun wanni itache. Shi kare ya zo, ya kwanta, ba ya san dila yana nan ba. Da ya zo ya kwanta, sai dila ya che "Kai ne, kare?" Sai kare ya che "I, Dila ne?" Dila ya che "To, ka ga dabarana daya ya fi naka goma sha biyu?" Sai kare ya che "Ai, hakkanan ne fa." Ashe magana suna yi, kura tana tsaye kansu, ba su gan ta ba. Kare yana kwanche, yana haki, sai ta che "Achikkin ku biyu wa na koro?" Sai dila ya che "A, wa na yi haki?" Sai kare ya tashi da gudu kura ta bi shi. Dila kuwa ya gudu, ya tsere.

(1) "Yi bako" to make (have) a guest.
(2) "You, you are eating," *i.e.*, "one for yourself."

---

## 131

### The City of Women.

*See* No. 82.

---

## 132

### The Boy who refused to Walk.

*See* No. 70.

---

133

### How the Goat and the Dog frightened the Hyæna.

Wannan kura ne da kare. Suka yi aboki, suka che "Mu taffi yawo neman abinchi." Sai kare ya che "Ba zani ba." Da ya che ba zashi ba kura ta taffi gidanta. Sai kare ya tashi ya taffi gidan bunsuru, sai ya che da shi "Ga shi, kura ta che en taffi yawo, ni kuma ba zani ba. Sai na taso, na zo gidanka." "Gara (1) da ka zo gidana ka gaya mani," en ji bunsuru. Sai ya che "To, mu tashi mu taffi gidan kura." Sai kare ya che da bunsuru "A, a, da na ki taffiya ne." Sai ya che "Mu taffi na san wayonda zamu yi." Sai ya yi kutun kere (2), sai ya dauka auduga ya sa ta chikki, sai ya dauka. Suka taffi gidan kura. Sai suka tarada kura tana kera, yayanta kuwa suna zona suna zugazugi. Sai ita uwan kura ta ga nama biyu ya zo, ta che "Marhaba." Shi ko kare da ya ga kura, yana kuka, yana zawo. Sai bunsuru ta (3) che "Yayan kura ba su iya zuga ba. Tashi en yi mata zuga" (4). Sai yayan suka tashi daga wurin zugan, sai bunsuru ya dauka zugazugi. Da ta dauka dafari tana waka, sai ta che ta chi zaki tara, ta chi bauna tara, kuma ta chi kura tara. Sai kura ta che "Mi kin che Dan Akwiya?" Ya che "Na chi zaki tara, na chi bauna tara, na chi kura tara." Kura ta che "Enna shaida da ka che ka chi kura tara?" Sai ya zara auduga achikkin kere. Da ta karba, ta ga auduga kaman jini, sai kura ta che "Dan Akwiya ina zuwa." Sai ta shiga chikkin gida. Da ta shiga sai ta fuda damfami, ta fitta da yayanta, ta gudu. Dan akwiya—shiru—shiru—ba ya ga kura ta fitta woje ba, sai ya che "Kare, tashi mu shiga chikkin gidan kura." Da suka shiga ba su ga kowa ba, sai bunsuru ya dauke kare ya rufe chikkin rumbu. Shi kuwa ya haka rami atsakar gida, sai ya shiga chikki, ya fitta da gemanshi awoje. Har kwana bakai ta yi. Sai kura ta che "Ai, bakin nan sun taffi gida." Sai yaya suka che "To, mu taffi." Da suka shiga chikkin gida, sai daya yaron ya kama gashi, ya che "Baba, ga shi." Sun yi fada har sun kama gemu sun ja. Sai ita kura dakanta ta ja gashi, ta fitto da dan akwiya duka woje. Sai akwiya ta yi kuka da karifi, kare ya yi nasa achikkin rumbu, ya che "Kama baban, kama baban." Sai kura ta yi dowa (5), tana zawo, sai dan akwiya ya aje kare a gida, ya che "Ga gidanka," sai shi kuwa, dan akwiya, ya taffi gidanshi. Sai kare ya samu gida, ya gaji, kura kuwa ba ta kara komowa gida ba. Masoman gaban kare na kura ke nan.

(1) Possibly "ya ke" is understood here, and also at (3).
(2) The kere juice mixed with lime juice makes a red liquid.
(3) Incorrect, change of sex.
(4) Change of person.
(5) Made (off to the) bush.

## 134

### The Beginning of the Enmity between Mouse and Man.

Wanni mai-gida ne. Tsakan dare ya tashi yana gassan nama. Sai kauren nama sai ya chikka dakin. Sai bera ya fitto dagga chikkin bunu, da ya zo, sai ya hangye gwaiwan mai-gida, mai-gida ina nan, ina ta gassa namansa. Bera yana che ko shi ni nama. Da ya zo ya kwashe kwada, ya taffi raminsa da su. Shi kuwa wanda akafisge kwadansa ba ya sani ba. Lokachin nan ya fidda namansa ya chi, da ya chi namansa ya gamma, ya hau kan gado zaya kwanta, sai ya ji jini ajikkin gwaiwansa. Sai ya ga kwada babu, ya che "Mi ya yi aikin nan?" Sai ya fura yula, ya duba, ya ga sawun bera, sai ya bi sawu har raminsa. Sai ya dauke diga, ya fuda rami, ya je ya tarada bera suna chin tsegwegwensa. Sai bera ya che wa ya ke shiga masa gidansa? Sai ya che barawo da ya zo ya fige dan tsegwegwensa, shi yana biyo. Sai ya che wa ya ke shiga masa gida ba ya sallamma ba? Sai ya che dakanta masa yana zuwa, en ji bera. Sai ya shiga chikkin dakinsa, ya dauke kworensa ya rataya, sai ya che su je wurin alkali. Sai mai-gida ya che "To, mu taffi." Sai alkali ya che "Mi ya gamma ku?" Sai ya che "Wannan ya zo ya fige min dan gwaiwana." Shi kuwa ya che "Tambaya shi domi ya shiga gidana ba ya sallamma." Sai ya che "To, en de ya rama maka kwadanka, kai ko kakka zaka rama masa shigar gida ba asallamma?" Sai ya che "To, shi wannan shera'an nasu," sai ya che "shi bera ya rama masa dan gwaiwa daya, shi kuma ya rama masa shigar gida ba sallamma. Sai ya che su je, sun sha pansa, ko achan aduniya sai asallamma. To yanzu aduniya ka iya shiga gidan wanni ba asallamma? Mafaran gaba wanchan ne, bera da mai-gida.

---

## 135

### The Waterfowl borrows the Dove's Beak.

Sheda ta taffi wurin kurichiya, ta che "Ina son aron bakinki, zani wurin bukin kajarini, dan sarikin tsuntsaye, Ina so en yi aro." Sai kurichiya ta che "To, amma kadda em ba ki aro kwana uku, kadda ki je ki yi wata uku. Kin san bakinki ba mai-iya chin abinshi da shi." Sai sheda ta che "Habba Kurichiya, ke ki yi mani rana zan mayar maki da dare? Ai, aro ne." Shi ke nan sai sheda ta taffi. Dagga kwana uku ta yi

wata uku (1). Sai dangin kurichiya suka che "Ke, kurichiya, en ba ki bi sheda ki karba bakinki, kiya mutu, ba ki iya chin abinchi." Sai ta che "To." Sai ta tashi. Da ta tashi, sai ta je wanni gari ta sauka a wanni itache. Sai ta che "Ku mutanen garin nan enna gidan kajarini, dan sarikin tsuntsaye? Sheda ta yi aron bakina. Dagga kwana uku sai wata uku." Sai ta che "Ba na iya chin abinchi da bakinta. En na je na chi abinchi, sai na fadi shekareki, na tashi zundundu." Sai mutanen gari suka che "A, ba anan ne ba, sai ki chi gabba, ki tarada su." Da ta tashi kuma, sai gidan kajarini, ta sauke a itachenda su ke daka (2). Sai ta che "Ku Mutanen Garin nan, enna gidan kajarini, dan sarikin tsuntsaye? Sheda ta yi aron bakina, dagga kwana uku sai wata uku." Sai ta che "Ba na iya chin abinchi da bakinta. En na je na chi abinchi, sai na fadi shekareki, na tashi zundundu." Sai akache "Mu barri daka mu ji wannan tsuntsu mai-dadin waka." Sai sheda ta che "Babu, ku yi aiki, ku yi aiki, kadda ku ji." Sai kuma ta sake fadi, ta che "Ku Mutanen Garin nan, enna gidan kajarini, dan sarikin tsuntsaye? Sheda ta yi aron bakina, dagga kwana uku sai wata uku." Sai ta che "Ba na iya chin abinchi da bakinta. En na je na chi abinchi, sai na fadi shekereki, na tashi zundundu." Sai shiru. Sai da akaji, akache "A, ga sheda nan." Sai ita sheda ta tashi, ta bi ta chikkin daki. Sai akache "Ki bi ta." Sai kurichiya ta bi ta, sai ta che "Habba Sheda, ba ni bakina, na ba ki aro kwana uku ke kin rikke sai wata uku." Sai ta karbe baki ta ba ta, ta karbe bakinta ta sa. Kurichiya ta fitta, ta taffi abinta. Sai sheda tana chikkin daki ta shiga tsari, bakinta ya tokare bango. Sai kajarini ya shiga daki, ya che "Enna sheda?" Sai ta che "Hakorina yana chiwu," tana boye baki. Sai kajarini ya che "Habba Sheda, da kin zo dafari na san bakinki ba naki ba ne." Sai ya che "To, ki zona a daki, kadda ki kara fitta sai buki ya watse." Kowa ya zo ya tambaya, ya che "Enna Sheda?" Sai akache "Ai, ba ta da lafiya." Shi ke nan, ba ta kara fitta ba sai buki ya watse.

(1) From three days she made (the time) three months.
(2) At its foot.

## 136

### The Search for a Bride.

Dan Sarikin Masar zashi Birnin Medina garin neman aure. Ya taffi wurin mallami. Mallami ya che "Taffi ka nema almajiri wanda zaya yi maka rakiya." Sa'anan ya taffi ya samu almajiri, ya zo da shi gida. Dare ya yi, almajiri ba ya yi wanni motsi ba, ba ya yi karatu da da dare ba. Safi ya yi, ya taffi shaida ma mallami, mallami ya che "A, a, ba ka samu almajiri ba." Ya che "Koma ka je ka nema wanni." To, ya taffi kasuwa kuma ya samu wanni almajiri, ya che "Zo mu taffi gidammu." To, yamma ya yi akayi masu abinchi suka chi. Sa'anan almajiri ya yi sallan almuru. Sa'anan ya che zaya shiga daki sai gobe. Da shigansa daki sai ya dosa karatu. Sai da gari ya waye dan sariki ya taffi wurin mallami ya che "Na samu wanni almajiri." Mallami ya che "Yanzu ka samu almajiri." Ya che "To, sai adaura aniya ku yi taffiya." Sa'anan dan sariki ya che "Muwa tashi gobe?" Mallami ya che "Kuwa tashi." Da safi ya yi, sai suka sa ma dowaki surdi, suka hau, suka fitta wojen gari, da su da iyalinsu pal, zasu garin neman aure. Suka fitta kofar gari, almajiri ya che "Ba ka sa akoma anema wanni dokin zagi daya, arikka dabam?" Sa'anan suka fitta, suka yi ta taffiya kuma. Akazo da dokin zagi guda daya dagga baya. Suka yi ta taffiya, suka issa dauji. Sai kurichiya guda biyu suka zo, zuka sauka, idanunsu daya kuwa. Kurichiya daya ta che "Dan Sariki da almajiri zasu Birnin Medina garin neman aure." Sa'anan dayan ta che "Ba ni ido en gani." Ta che "Dan sariki da dan mallami zasu Medina garin aure, en de rabonsu Allah ya ba su, em ba rabonsu Allah ba ya ba su." Sa'anan wachan wadda ta fara magana kuwa, ta che "Ba ni idanu en gani." Ta che "Dan sarikin nan, itachen nan da zaya wuche, shi wuche shi aguje." To, dan mallami ya ji, dan sariki ba ya ji ba. Ya che da dan sariki "Ka yi sukuwa ka wuche itachan nan." Sai ya yi sukuwa ya wuche. Da zaya wuche rashin itache ya fadi ya kariye kaffan doki, doki ya mutu. Sa'anan almajiri ya che "To, ja wanchan doki ka hau." Suka yi ta taffiya kuma. Suka zo kuma kogi, suka tutube rigansu suma wanka, kurichiya biyu suka zo suka sauka, suka che "Dan sariki da dan mallami zasu Birnin Medina neman aure." Kurichiya daya ta che "Ba ni idon en gani." Ta chiri ido ta ba ta. Ta che "Dan sariki da dan mallami, da sun sani da sun fitta dagga chikkin ruwan nan, su sare sanda biyu, su zo su ba rigan dan sarikin nan kasshi. Dan mallami ya ji, dan sariki ba ya ji

ba. Suka fitta dagga ruwa, suka sare itache, suka bubuga rigan. Dan mallami ya che da dan sariki "Guso ka gani." Da ya tagarda riga, machiji ya fitta, baba da gaski. Sa'anan ya che "Mu daure aniya mu taffi." Sa'anan suka daure surdinsu, suka yi ta taffiya zasu gari.

Suka zo bakin birni, a kofan gari. Sa'anan kurichiya biyu suka zo suka sauka. Daya ta che "Dan sariki da dan mallami suka zo neman aure." Wachan ta che "Ba ni ido en gani." Ta karba ta manna. Da ta manna, ta che "Dan sariki da dan mallami suka zo neman aure. Da de sun sani dan sariki ya shiga birnin nan asukuwane, em ba hakka ba ayi mugun aiki." Sai dan almajiri ya ji, dan sariki ba ya ji ba. Sai dan mallami ya che "Dan sariki, ka yi sukuwa ka shiga." Ya shiga asukuwane, sai birni ya ruche, ya ragaya ya wuche. Da dan sariki da dan mallami suka shiga gari, su kurichiya biyu suka koma abinsu. Suka taffi kaman kofan gidan sariki. Sariki ya che "To, akai su masauke." Da yamma ya yi kuma, dan sariki ya zo wurin buduruwa, ya che "Ina son ki da aure." Ta che "Ni ma, ina son ka, amma wanda zaya aure ni sai ya kwana bakai ba ya chi komi ba." Ya che "To, na yarda." Suka kwanta daki daya. Sai suka yi dara, shi ne chinsu. To dan almajiri dare ya yi, sai ya dauke buzu ya rataya, ya che "Ya Rasulu Wahidu." Mutanen wanni gida sun ba shi tuwo, mutanen wanni gida sun ba shi tuwo, mutanen wanni gida sun ba shi tuwo, har ya chikka kwariya da tuwo. Ya zo ya buge daki enda dan sariki ya ke. Bango ya bude. Ya ba shi tuwo yana chi, dan sariki ya koshi. Sa'anan kuma ya buga bango ya rufa, ya koma wurin kwanchiyansa. Daki fa, ba shi da kofa. Har kwana shida shina ba shi tuwo. Randa kwana bakai zaya chikka, daren bakai, almajiri ya je garin bara. To, ba adaffa komi sai gujiya. Ya samu gujiya achikkin koko, ya taffi, ya buga bango, abayan yaro. Bango ya bude. Shina diban gujiya, shina ba shi, shina chi. Shina dara da yariniyan kuwa, ita, ba ta gani ba. Da ya koshi, da ya kauda kai, sai gujiya daya ya fadi agabbanta, yariniya. Ta daka, ta duba, ta che "Minene wankai?" Shina zone shiru. Ta che "Ho, Lalatache, gobe muwa gammu." Ta tashi ta chiri zane har zanne bakai, ta aje. Ta sa hanu achikkin aljifun zanne, ta dauke bata, ta fude, ta dauke kwaran gujiyan nan, ta sa achikki. Sa'anan ta dauke zannuwanta ta daura. Sa'anan ta kwanta abinta kuma, ta che tana jin barchi. Almajiri ya tashi yana kuka, ya shiga chikkin gari. Sa'anan ya samu kanwa. Kanwa ta che "Kana son mine?" Yaro ya che "Kin ji abinda ya sa ina neman ki?"

Ta che "Mine?" Ya che "Dan sariki da yar sariki suna dara, na nemi abinda zaya chi na kai mashi, sa'anan ta gani mu yau." Sa'anan kanwa ta che "Mu taffi." Suka zo, ya buga kofa, daki ya bude. Sa'anan kanwa ta che "Mu shiga." Sa'anan kanwa ta shafe yariniya da magani. Sa'anan suka kunkunche zanne, Sa'anan suka sa hanu, suka dauka bata, suka bude, suka dauke dan gujiya, suka ba dan sariki ya chi. Suka dauka dan dara guda daya, suka sa achikkin bata, suka rufa, suka mayar mata achikkin aljifunta. Suka daura mata zannuwanta kuma. Sai kanwa da almajiri suka fitta, kowa ya taffi gidansa abinsa. Dan sariki ya yi barchi har gari ya waye. Ta yi kirra, ta che azo afiche su kuma, kwana bakai ya chikka. Akazo, akafishe su. Dan sariki kuma ya taffi masaukanshi, ita kuma ta taffi gidan ubanta. Ta taffi ta fadi ma ubanta, ta che "En dan sariki ya zo, sai ayanka, ya yi la'ana." Sa'anan azurhur ya yi, gari duk ya taru. Sa'anan akaaike dan sariki ya zo. Sa'anan uban ya che "Akirro yariniya." Akakirro ta ta zo. Da ta zo, uban ya che "To, ki zo ki kawo shaida mu gani." Ta zo ta kwanche zannuwan nan duk, ta sa hanu, ta dauke bata. Ta fitto da bata, ta mika ma kanen ubanta. Ya karba, ya mika ma Limamin garinsu. Ya che "To, bude batan nan," en ji sariki. Liman ya bude bata, sai ya ga dan daran nan achikki. Ya che da sariki "Ka gani?" Ya che amika ma kanensa. Ya che "To, ke, kin che mani gujiya ne. Ga shi ba gujiya ne ba." Shi dan sariki ya tashi, ya che "To, ku ba ni en gani." Da ya karba ya duba ahanunsa, ya che da su "To, kuwa gani, gujiya ne wannan?" Mutane suka che "A, a." Sai ya fidda takobinshi ya tashi zaya sare uban, suka fitta aguje duk zauren. Sa'anan almajiri ya tashi ya rungume shi, ya che "Yi hankuri." Sa'anan sariki ya che "To, taffi gida, sai dayamma ka zo adaure maka aure." Sa'anan yamma ya yi, suka zo, akadaure masu aure. Sa'anan dare ya yi akataffi da yariniya a gidanshi enda ya sauka. Akakai mashi yariniya.

Ananan, ananan, shi kan taffi wurin almajiri shi kan hira. Shi kuma, almajiri, shi kan tashi, shi kan zo wurinshi, shi kan hira. Ran nan almajiri ya tashi zaya zo wurinshi, sai ya samu machiji a turaba. Suka rikka kukuwa, machiji ya ga almajiri zai mashi, ya zuba ma almajiri miyo a idanu, idanu ya rufa. Shi kuma yaron ya soke shi da wuka, ya kasshe shi. Sa'anan yaro ya che "To, sai na koma gida kuma enda na sauka." Almajiri ya rikka sandanshi, yana lalaban turaba har ya taffi gida. Da safi, dan sariki ya zo, ya che "A, Wane, ban gan ka ba jiya." Sa'anan ya che "A, da ka wuche a turaba, nan ba

ka ga machiji a juji ba?" Ya che "Ni ne (1), mun yi fada da shi jiya, idanuna ya yi makanta." Ya che "Ashe, gobe muwa taffi gida." Ya tashi, ya che da sariki "Gobe muwa tashi, muwa taffi gida." Sa'anan sariki ya che "Lafiya?" Ya che "Lafiya, abokin taffiyana, machiji ya zuba mashi miyo a idanu, ya yi makanta." Sa'anan sariki ya che "To, kuwa tashi." Matan tana goyo. Sariki ya sa bayi, da mainya da yara, da dukiya pal. Da safi akafitta, za'ayi masu rakiya. Sa'anan kuma suka taffi abinsu, zasu gari. Suka isso wanni daji kuma, kurichiya biyu suka zo suka sauka. Dayan ta che "Dan sariki da dan mallami sun zo neman aure. Allah ya ba su sun samu, zasu taffi gida." Daya ta che "Ba ni ido en gani." Da ta manna, ta che "Ga shi kuma, dan mallami ya yi makanta." Daya ta che "Ba ni ido en gani." Ta che "Da de asani, akarbe dan yaron da akahaifa chan, ayanka, atabba jini na dan, ashafa masa a idanu, ido ya bude." Dan sariki ya ji, dan mallami ba ya ji ba. Sai ya koma asukuwane ya karbe dan, ya zo ya yanka, ya dibi jini a hanunshi, ya zo ya shafa ma almajiri ido. Ido ya bude. Suna taffiya kuma, uwan ba ta sani ba. Sai kurichiya biyu suka zo suka sauka kuma. Dayan ta che "Dan sariki da dan mallami suka zo garin aure. Allah ya ba su, sun samu. Sago da dan mallami suka yi kukuwa, sago ya fidda miyo achikkin idon yaro, ya zamma makafo." Sai suka koma hainya kuma. Dayan ta che "Ba ni ido en gani." Ta che "Da suka zo turaban nan, da sun sani, da sun koma wurin yaronda sun yanka nan, da sun diba gainye na wurin, da sun buge yaro da shi, sai ya tashi." Dan almajiri ya ji, dan sariki ba ya ji ba. Sai ya koma asukuwane wurin yaro. Dan sariki ya che "Zaka enna?" Ya che "Ina zuwa." Ya zo, ya kariye gainye awurin, ya buga yaro da shi, yaro ya tashi. Ya dauke yaro asukuwane, asukuwane, asukuwane, kuma ya zo, ya mika ma masu-goyo. Sa'anan ya wuche, ya chimma dan sariki ya che "Mu taffi." Ya che "Da ka taffi enna ne?" Ya che "Na yarda wanni abu ne, na taffi na daka." Sai da suka zo rafin kofan gari, suka bar iyalinsu su shiga gari kuma, sa'anan ya ga yaro kuma agoye. Sai ya ja rawani a baki yana dariya. Suka raba dukiya kuma, suka zona.

(1) It was I who did it. Plural for singular follows.

---

## 137

### THE ORIGIN OF THE CROW.

*See* No. 64.

## 138

### THE WOMAN AND HER STRANGE SUITORS.

Wata bazawara ba ta da miji, sai ba wanda ya fara zuwa neman auren ta sai kadangari. Yana zuwa kullum kullum, yana neman anre. Sai bera ya ji labari, sai ya taffi wurinta, ya che "Ke, de, Allah wadan ki, ba wanda zaya nema auren ki sai kadangari?" Sai ta che "Mine gare shi?" Sai bera ya che "Op, ai makafo ne, ba ya gani da da dare." Sai ya che "En kin gardama, ba makofo ne, sai da ya zo gobe, izan zashi gida, ki rikke shi, ki che 'A, a, sai rana ta fadi.'" Sai kadangari ya zo, suna tadi, suna tadi, suna tadi, yamma ya kussa yi. Da ya ga rana ya kussa fadi, sai ya che "Iss zani gida." Sai ta che "A, a, barri de, manna, anjima kadan ka taffi." Sai ya barri. Sai rana ya fadi, sai ta che "To, tashi ka taffi gida." Sai ya che "To." Da ya fitta, sai yana tuntubi, yana karo. Sai kafin ya yi taffiya kaman kaffa ashirin dufu ya yi, sai ya samu dan chiyawa, sai ya sa kainsa achikki. Sai ya kwana nan. Da sasafi, mata ta che "To, bar en bi sawunshi, bera ya che makafo ne, izan makafo, ba ya kai gida ba." Tana taffiya, tana taffiya, tana taffiya sai ta zo ta gan shi akwanche. Sai ta che "Mi ya sa ka ka kwana nan tun jiya?" Sai ya che "Iss, rabuwana da ke jikkina ba shi da lafiya." Sai ta che "Ashe, azanchi da bera ya gaya mani gaskiya ne, kadda ka kara zuwa gidana, Makafo." Shi bera kuwa, shi ta ke so. Sai zakara ya ji labari. Sai ya zo, ya che "Op, Allah wadan ki, ba wanda zaya nema aurenki sai bera, barawo, wanda ba ya zuwa kasuwa?" Sai ta che "Ashe, barawo ne?" Sai ya che "To, en kin gardama, sai gobe ki che shi rame ki kasuwa." Sai ta che "To." Sai bera ya zo, suna tadi, suna tadi, suna tadi, sai ta che "To, ina so ka rake (1) ni kasuwa." Sai ya che "A, a, ni bera, tun kakan kakan ubana ba ya zo kasuwa, ni en taffi kasuwa?" Sai ta che "A, habba, Bera, ba za'agan ka ba." Ta kawo dan kwotachi, ta zubarda dawa, ta che "Nan zaka shiga, ba wanda zaya gan ka." Sai ta taffi. Da ta taffi, ta kai tsakan kasuwa, ta bude. Da ta bude, sai mutanen kasuwa sun che "A, ga bera, barawo. Ku kasshe, ku kasshe, ku kasshe." Sai ya tsira dakat. Sai ta che "A, azanchen zakara gaskiya ne." Sai ita ya ke so kuma, shi, zakara. Sai giwa ya ji labari, sai ya zo, ya che "Allah wadan ki, aurenki sai zakara?" Ya che "Wannan malalache wanda ba ya iya aikin komi?" Ya che "To, en zakara ya zo, ki gaya masa hakkanan." Da zakara ya zo, sai mata ta che "To, ka ji abinda giwa ya fada." Ya che "Kai malalache ne,

ba ka iya aikin komi." Sai ya che "Hakka giwa ya fada?" Ya che "Giriman jikkinshi na wofe (2), kowanni aikinda ya yi ni ma na yi." Da giwa ya zo, ta che "Ka ji abinda zakara ya fada?" Zakara ya che "Kai giriman jikkinka na wofi, komi ka yi ya yi. Sai giwa ya che kariya ya ke yi." To akwai wanni kudundufi, fadansa kaman gida baba. Sai giwa ya tara itache da haki, ya zubar achikki, ya che "To, zakara ya zo ya dauke." Zakara ya zo, ta che "To, giwa, ka ga aikinda ya yi, amma ya che ka debe." Sai zakara ya wo gaya na kaji, suka zo suka chiri itache duka, suka zubar haki duka, kudundufi ya koma yanda ya ke da. Sai giwa ya zo, sai matan ta che "To, ka ga aikinda zakara ya yi?" Sai giwa ya che "To, gobe en zakara ya zo, ki che gobe muwa yi yaki da shi da ni." Da zakara ya zo ya ji, sai ya che "To, sai kowa shi gaya danginshi." Giwa ya taffi ya gaya naman daji duk. Zakarra kuwa ya gaya tsuntsu duk. Sa'anan suka zo wurin yaki. Shafo ya che "Ni ne sarikin yakinka."

The rest is the same as No. 22.

(1) This verb seems to have two pronunciations, "raka" with a long first "a" which would remain "raka ni," and "rakka" which becomes "rakke ni."

(2) Lit. The size of his body is ("ne" understood) of worthlessness. "Giwa" is here masculine because the animal must evidently be a male.

---

## 139

### The Ungrateful Boy and the Dove.

Wannan ne de, da shi da ubanshi suna nan, ba su da arziki, har uban ya mutu. Uban ba shi da dukiya, ba komi sai rigan kabar. Shi ke nan, sai yaron ya gudu, iya taffiya, iya taffiya, chikkin daji. Shi ke nan, sai kurichiya ta zo ta sauka, ta che "Yanzu ko yan Adam, ayi maku rana ku yi wa mutum dare?" Sai yaro ya che "Allah ba zan yi maki ba." Sai ta che "To, ka ga zan ba ka dukiya, en na ba ka dukiya, em ba ka mata, en yi ma katon gari wanda ba kamanshi, amma en na zo zan yi chewa 'Mai-Rigar kabar, Mai-Wandon kaba, Dan Mutsiyata'" ta che "Har ya (1) so-goma." Ya che "To, na yarda." Sai da zata tashi, sai ta ba shi gari, ta ba shi bayi, ta ba shi dokuna, ta ba shi mata, duk ta ba shi, duk talakawan gari ta ba shi. Da ta ba shi, sai ta tashi. Matan gari kuwa su biyu ne

matanshi, sariki. Anayi mashi fadanchi kullum. Sai kurichiya ta zo, ta che "Mai-Rigar kabar, Mai-Wandon kaba," ta kan che "Dan Mutsiyata." Ya kan che "Um." Kullum, har kwana tara ya yi. Sai ran nan, sai washen gari ya zo, sai ta che "Mai-Rigar kabar, Mai-Wandon kaba, Dan Mutsiyachi." Sai ya yi shiru. Sai uwar-gida ta che "Wanni abu ne ya ke damen ka kullum?" Ya ki amsawa, shi sarikin. Sai matar gidan, sai ta buge kurichiya. Da ta buge kurichiya, ta tashi dagga garin. Sai ta tashi da garinta, ta barri yaro da rigar kabar kauwi.

(1) "Yi" or "kai" understood.

---

## 140

### The Most Cunning of all the Birds.

Da hankaka, da bardo, da kurichiyan gida, da hasbiya suka gardama. Kurichiyan gida ta che ta fi hankaka wayo. Bardo ya che ya fi kurichiyan gida wayo, hasbiya ta che ta fi bardo wayo. Sai suka che "To, kowa shi fadi wayonsa, aji." Sai hankaka ta che "Mutum ina tsaya shum," ta che "en ya duka ya karkata, zaya yi mugunta." Sai kurichiyan gida ta che "To wayonki ke nan hankaka?" en ji kurichiyan gida. Ta che "Amma ki yi hankali da mai-chin gariba." Ta che "Dun mi?" en ji hankaka. Sai kurichiyan gida ta che "A mai-chin gariba ba shi ne ya tsaya shum? En ya jefe ki da dan gariba da ya ke bakinshi fa?" Sai ta che "A, ni na fadi nawa wayo, sai ke ki yi naki." Sai ta che "To, ni, nawa wayon ba ni kamuwa a tarko." Sai bardo ya che "Ni kuma, ba ni kamuwa a tarko." Sai hasbiya ta che "Ni, kuma, ba ni kamuwa a tarko." Shi ke nan, sai akache "Ke, Kurichiyan Gida, yau zaki yi korto a masusuka, inda yara suna yin tarko." Sai ta zo. Da ta zo, sai yara suka yi tarko achikkin keke. Sai ta zo tana korto, tana korto, tana korto, sai tarko ya kama ta. Da ya kama ta, sai yara suka zo da gudu suka kwanche. Dagga nan sai hasbiya ta che ma bardo "Ashe irin wayonda kurichiyan gida tana yi ke nan?" Sai ya che "A, ga shi mun ga nata, saura nawa da naki." Sai hasbiya ta che "To, gobe, Bardo, kai zaka korto." Da ya zo, yana korto, yana korto, yana korto, sai tarko ya kama shi daro. Da ya kama shi, da yara suka zo su kwanche shi, sai ya papaka, ya kwurche. Sai ya je, ya che da hasbiya "Ni na kwurche dakat yau." Sai hasbiya ta che

"Ai, Bardo, da kai da kurichiyan gida ba ku da hankali? Barri gobe ka zo ka ga wayo." Da gari ya waye, sai hasbiya da matanshi zasu korto a masusuka, yara sun zo sun gara tarko sun watsa dawa achikki. Sai da hasbiya ta sauka da matanshi sai suna chin dawa, suna chin dawa, suna chin dawa, sai hasbiya namiji ya ga tarkon nan. Da bardo da hankaka suna bissa, suna kallo, suna che "Tarko zaya kama ta." Da hasbiya ta ga tarkon, ya che ma matanshi "Lahidi gudu, kassa nan da gashi ne." Sai suka tashi bup, suka yi bissa. Sai hankaka ta che "Tabbas, hasbiya ta fi mu wayo." Ka sani en hankaka tana nan, en ka karkata, sai ta tashi. Wayonda ta sani ke nan.

---

## 141

### The Wild Cat and the Cock.

Da muzuru da zakara. Suka che su yi abokantaka. Sai muzuru ya che "Enna zan same ka?" Sai ya che "Anan zaka same ni." Sai ya che "To, yau tsakan dare ina zuwa mu yi hira." Sai tsakan dare sai ya taffo, ya zo yana kirra "Saidu, Saidu." Zakarra ba ya amsa ba, ya gaya masa sunansa ne. Ya kuma kirra "Saidu?" Zakarra ba ya amsa ba. Sai jijifi ya yi, sai zakarra ya yi "Puk, puk, puk," ya che "Wa ya ke kirran Saidu?" Muzuru kuwa ya ga gari ya waye, ya gudu wurin buya. Sai da mareche kuma suka gammu, sai ya che "Kaka na zo da dare ina kirran ka, ban ji ka ba?" Sai ya che "A, na taffi wurin kwana ne, barchi ya kama ni." Ya che "To, yau mu yi hira, kadda ka shiga achikkin gida." Sai ya che "To." Sai ya taffi. Sai tsakan dare sai ya taffo, ya zo yana kirra "Mabayi mabayi." Zakara ba ya amsa ba. Ya kuma kirra "Mabayi, Mabayi." Zakara ya che "Wanene yana kirra Mabayi ye?" (1) Sai muzuru ya che "Abin haushi, abin haushi." Sai ya che "Ba zaka fitta ba." Ya che "A, a, sai da sasafi." Sai jijifi ya yi, sai zakara ya yi "Chikka kalike, chikka kalike, chikka kalike." Sai da mareche kuma suka gammu, sai muzuru ya che "Kaka na zo da dare ina kirranka 'Mabayi,' ban ji ka ba?" Sai ya che "A, a, na yi amsa manna." Ya che "To," yau mu yi hira, kadda ka shiga achikkin gida. Ya che "To." Suna wasa, suna wasa, suna wasa, sai muzuru sai ya dane shi, sai ya che "Kurayit." Sai mutumen gida suka che "Wanene?" Sai muzuru ya che "Mu ne, muna wasa." Sai zakara ya che "Wanne irin wasa har na

yi kashi?" Sai ya che "En tabba jan nan na kainka en ji?" Da zakara da ya sunkwiya, sai muzuru sai ya shamge kai, ya chinye. Sai kankanan zakaru suna che dagga chan "Amana, amana." Muzuru sai ya che "Amanan mine?" Sai ya dauke gudan jikkin zakara ya shiga kurimi da shi. Dagga nan kuma amanan zakara da muzuru ta kare.

(1) A Jemaan Daroro ending.

---

142

THE GIRL, THE SNAKE AND THE PIGEON.

Yam-mata suka taru, suka taffi daji, suka hau kan bishiya. Lokachin nan sai igiyan kasa ya zo ya kewoye gindin bishiya. Yana neman wata wai ta Talele, domin farin jininta yana so ya hadiye. Shi ke nan, yariniya daya ta sauko, ta che "Machiji, ba ni ne Talele ba, ba ni wuri en wuche." Ya ba ta gu ta taffi; ya che ita Talele ya ke nema. Wota kuma ta zo, ta che "Machiji, ba ni ne Talele ba, ba ni wuri en wuche." Ya ba ta gu ta taffi; ya che ita Talele ya ke nema. Wota kuma ta zo; duk suka wuche sai ita Talele, ita daya akan bishiya. Lokachin nan sai hasbiya ta zo, ta che "En de mutum ya yi maku alheri sai ku yi mashi keta, amma zan yi maki wanni alkawali. Kin ji abinda yam-mata su ke fadi? Sai ki tube zannenki duka ki ba ni, zan kawo maki a gida." Sai ta tube, ta ba ta. Lokachin nan sai ta sauko kassa kadan. Sai ta che "Machiji, ba ni ne Talele ba, ba ni wuri en wuche." Ya ba ta gu ta taffi, ta taffi gida. Sai hasbiya dagga samma sai ta che da machiji "Ka gan ni, ni ne Talele, amma na taffi." Lokachin nan sai ya ji haushi, sai ya chije wutsiyansa, sai ya mutu awurin. Lokachin nan hasbiya ta tashi, sai ta je gidan Talele. Lokachin nan ta che "To, ga kayanki." Talele ta che ita ta ba ta bayi biyal. Ta che ba ta so. Sai ta che abinda ta ke so, en de ta zo ta debe dan tsaba, azubar mata akasa, en ta chi ta tashi ta taffi. Shi ke nan, kullum ta kan zo, sai aba ta tsaba. Ran nan Talele ta tashi ta taffi wurin kawanta achikkin gari. Sai hasbiya ta zo gidanta, ita Talele. Da ta zo tsofuwa a gidan Talele ta tashi ta duke hasbiya, sai hasbiya sai ta mutu. Talele ta komo. Da ta komo, ta che "Wa ya duke hasbiyan nan?" Sai akache kakanta ne. Sai Talele ta dauke wuka, ta fude chikkinta, sai ta mutu sabili da ankasshe hasbiya. Alkawalinsu ya zo daya.

## 143

### The Tender-hearted Girl and the Fish.

*See* No. 3.

---

## 144

### The Girl who stole the Snake's Egg.

Wata yariniya ke nan, ta je ta iske kwain sago, ta dauka. Sai sago ya tashi ya bi ta, yana chewa "Ta mulu mulu (1), Yariniya ba ni kwaina." Sai yariniya tana gudu, sai ta gamma da fatainya suna noman kansu. Sai suka che "Yariniya, mi ki ke gudu?" Sai ta che "Wanni abu ne." Sai suka che "Op, ba kin gani muna noman kanmu ba? En ya zo sai mu sare shi." Sai yariniya ta koma woje daya, ta tsuguna. Sai zuwa chan sago yana chewa "Ta mulu mulu, Yariniya ba ni kwaina." Suka che "Mine wannan?" Sai ta che "Ai, abinda ina gudu ke nan." Sai suka che "A, ki yi ta gudu mu muwa boye." Sai yariniya ta yi ta gudu, ta zo ta iske gatari suna faskaren pa. Suka che "Yariniya, mi ki ke gudu?" Sai ta che "Wanni abu ne." Sai suka che "Op, ba kin gani muna faskaren pa? En ya zo ba zamu faskare shi ba?" Sai ta zona. Sai zuwa chan sago yana chewa "Ta mulu mulu, Yariniya ba ni kwaina?" Suka che "Mine wannan?" Sai ta che "Ai, abinda ina gudu ke nan." Sai suka che "A, ki yi ta gudu, mu zamu boye." Sai tana gudu, tana gudu, ta zo ta iske buzuzu yana noma, yana waka, yana che "Chirin chirin waragaja" (1). Sai ya che "Yariniya, mi ki ke gudu?" Sai ta che "Wanni abu ne." Sai ya che "Op, ba kin gani ina chirri? Koma ki zona." Sai zuwa chan sago yana chewa "Ta mulu mulu, Yariniya ba ni kwaina?" Sai ya che "Mine wannan?" Sai ta che "Ai, abinda ina gudu ke nan." Ya che "To." Shi ba ya kula da shi ba, yana wakan shi "Chirin chirin na waragaza." Sai sago ya che "Kai, ba ni ajiyana." Sai ya che "Ajiyan durin-uwarka." Sai sago ya che "Ni?" Sai ya che "Kai." Sai sago ya che "To, sai ka ga aikin durin uwarka." Sai sago ya dauke buzuzu ya hadiye. Sai ya fitto a kwayan idon sago, ya yi ta wakanshi "Chirin chirin na waragaza." Sai sago ya sake hadiyen sa, sai ya fitto tsakar kai. "Chirin chirin na waragaza." Sai ya sake hadiyensa, sai ya fitto dagga chikinsa "Chirin chirin na waragaza." Sago ya fadi, ya mutu. Sai ya che "To, Yariniya, ki taffi gidanki."

(1) Magic words of whose meaning the narrator was doubtful.

## 145

### The Girl who married a Snake.

Wata buduruwa ke nan. Duk gari ba mai-keyawunta duk gari, kowa samari, kowa ya zo neman aure. Sai ta che aurenta ba na kurdi ba, ta che " Sai wanda akawanka jikkinshi akaduba, jikkinshi duka ba aga tabbo guda daya ba." Duk saure suka zo dagga wanni gari, dagga wanni gari, dagga wanni gari, akaduba jikkinsu, duk ba wanda ba shi da tabbo. Sai ta che ba mijinta achikkin su. Sai sago biyu achikkin daji suka ji labari, sai suka rikidda mutum. Sai suka zo, suka che sun zo neman aure. Sai akayi ma daya wanka, akaduba jikkinshi, tun dagga kaffa har ido babu tabbo ko guda daya. Sai ta che "To, mijinta ke nan." Sai kanuwanta ta che zata bi ta, sai ta che " Kadda ki bi ni ki kasshe mani aure." Sai kanuwan ta zamma kuda, ta shiga chikkin kayanta. Sai suna taffiya, suna taffiya achikkin daji, suka iske gara. Su mazza suka che " Ki buga gara, ki dauke fura dagga chikki mu chi" (1). Sai ta dauko ta dama masu, suka sha. Sai suka je gidansu. Da suka ji gidansu sai ta sauke kaya. Da ta sauke kaya sai ta ga kanuwanta ta fitto. Sai ta che " Ashe, na hanna ki ki biyo ni, sai kin bi ni ki kasshe mani aure?" Sai ta kiyale ta, ta che " Zan bar ki ki zona wurina, amma izan na ga zaki kasshe mani aure zan kore ki ki koma gida." Suna nan zone, mazza su kan taffi rafi da sagogi, su kan chi kwado. Sai kanuwan ta hau bissa itache awurin ruwanda su ke chi kwadi awurin (2). Sai tana yi masu waka, tana chewa. " Ina gaishe ku mazzan yana." Sai suka che " Wannan tsuntsu mai-dadin waka, en mun chi matammu sai mu ba ki kai." Sai ta je ta gaya ma yan, ta che, " To, mazzanki fa, machisai, zasu chi ki." Sai ta che " To kin fara? Da kin zo na che zaki kasshe min aure." Sai ta che " To, en kina che ina kariya ne, sai rana ya yi sun taffi rafi, na taffi da ke mu hau itache." Sai ta che "To." Da rana ya yi da mazza suka taffi, sai ita kuma da kanuwan suka zaga, suka je itachenda kanuwan ta kan tsaya bissa shi ta kan yi masu waka. (3) To, sai mazza suka zamma sagogi suka hadiye kwado. Sai kanuwan ta che " To, bar en yi masu waka, ki ji abinda zasu fada." Sai ta che "Ina gaishe ku mazzan yana." Sai suka che "Wannan tsuntsu mai-dadin waka, en mun chi matammu sai mu ba ki kai." Sai ta che "To, kin ji abinda suka fada ye?" Ta che "To, na ji." Sai ta che "Mu taffi gida mu gudu." Sai suka zo suka gudu, suka gudu, suka gudu, suna so su koma garinsu, su yar da kanuwan. Sai sagogi suka dawo,

ba su gan su ba, sai suka che "Ai, nama ya gudu." Sai suka zamma sagogi sosai, suna gudu, suka iske su. Da suka iske su sai kanuwan ta buga yanta da hanu, sai ta rikidda, ta zamma kututuri da hakori. Sai aboki ya che "A, ga kututuri da hakori." Sai ya che "Mu koma gida mu dauke gatari mu sare shi." Da suka koma gida, sai kanuwanta ta buge ta, ta zamma mutum kuma. Kafin sagogi suka dawo, ita yar da kanuwan suka ketare rafi a kofan garinsu. Sai sagogi sun gani ba su da dama su taffi wurinsu sai suka aike wurinsu da zage. Suke che "Kuna zabe, muna so mu chainye ku." Sai sagogi suka koma daji. Su yam-mata suka shiga gari. Yan ta che "To, ni, ba na kara zaben miji ba, ko kuturu amba ni na yarda." Saboda ta sha wuya ke nan.

(1) These insects store up grain in their hills, the husks can be seen if one kicks down the hill (jibba).

(2) Lit. "Then the younger sister climbed a tree in the place of (near) the water, they were eating frogs in its place (where)."

(3) A somewhat similar construction.

---

## 146

### How the Hunter was hunted.

Wannan mallami ke nan. Yana da danshi, Suna kasshe bauna, suka kasshe bauna dayawa. Sai bauna ta rikidda ta zamma mache dakeyau, ta che sai ta rama, zata kasshe dan mallami. Sai ta zo chikkin gari, sai samari, kowa ya zo ya neme ta ta ki shi. Sai ta che sai dan maharbe tana so. Da dan maharbe ya zo, ta che "Madallah, ga saure da zani wurin shi en kwana." Sai ya dauko ta, suna kwanche a dakinshi suna tadi, suna tadi, sai ta che "Kai, amma duk gari ba masu-halbe kaman kai da ubanka." Ta che "Kuna da magani ne?" Sai ya che "I, muna da magani manna, ataffi halben bauna ba magani? Sai ta kasshe mutum." Sai ta che "Wanni irin magani wurin ku kuna ba ta ne?" Ya che "I." Ya che "Mu kan rikidda sure." Ya che "Mu kan rikidda kututuri achikkin hainya kuma." Ta che "Su ke nan biyu?" Sai ya che "Mu kan rikidda zop—." "Kai," en ji uban yaro, "Ka yi shiru." Sai suka barri wannan tadi kuma. Sai ta kwana wurin shi. Gari ya waye, ta che "To, ka zo ka yi mani rakiya." Sai ya che "To." Sai ya dauko kwore ya rataya. Sai ta che "A, rakiya nawa sai da kwore?" Ya che

" A, ko ina komowa en ga nama, sai en harbe." Sai ta che " A, a, ba zaka kai ni da nisa ba." Sai suka je, suna taffiya, suna taffiya, suna taffiya, suna tádi, sai ya che " To rakiya ta issa, zan koma gida." Sa ta che " A, a, kai ni wurin rafi chan, ka koma." Da suka taffi rafi, ta che " To, bar ni anan, ka koma gida, ni kuma zani garinmu." Sai ya ketare rafi, ita kuwa ta ketare rafi, rafi na tsakansu (1), ba mai-ganin wanni. Sai ta kwanche zanne ta yar, ta kwanche kalabi ta yar, sai ta birgima, ta zamma bauna. Ta tashi, sai ta zo ta sha gabban shi. Sai ya che " Op, ga bauna, ni ban zo da komi ba." Sai ta taso mashi, zata dauke shi da kafo, sai ya zamma sure, sai ta teffi zata dauke sure, sai ya tashi ya zamma kututuri. Sai ta tashi za ta tunkwiye kututuri, sai ya tashi, ya zamma zobe. Sai ta zo ta dauke, ta che " To, ya che 'Zop,' uban ya hanna, amma 'zop' ba 'zobe' ba ne." Sai ta yarda shi achikkin chiyawa. Sai ta che " To, chikkin itache duka ba mai-sunan 'zop,' sai, zobe." Ta che " Zobe ne, barri en je en neme shi, en kasshe shi." Sai ta zo ta yi nema, ta yi nema achikkin chiyawa, ba ta same shi ba. Sai ta che, " Ubanshi ya chera da shi, en ba don hakka ba da na kasshe shi." Sai ta yi taffiyanta. Sai yaro ya koma gida, ya gaya ma ubanshi. Sai uban ya che " To, Kai, ba ka da hankali. Mache ko ka chikka son ta, ba ka bude mata chikkinka." Iyakan wannan.

(1) How the river could have been between them after they had both crossed it is not clear.

---

## 147

### The Man who married a Gazelle.

Wanni mutum de iya da mache (1). Sai wata kuma mata ta zo ta aure shi, ita kuma barewa che, sai ta zo ta rikiddi mache mai-keyau, ita ta zamma kishiya. Da ta aure shi, ananan yana noman kubewa. Shi ke nan, ran nan wache, ba ita che barewan ba, akasa ta ta je ta debo kubewan. Sai ta je, ta chikko kwariya pal. Shi ke nan, anaike barewa, sai ta je ta samu. Sai ta kirrawo yan-uwanta, sai da ta yi kirran su, sai suka chainye kubewa. Shi ke nan, sai ta komo gida, sai ta che ita ba ta ga komi a gona ba. Sai miji ya che " To." Da zata sake taffiya, sai akasa yaro dan uwar-gida ya bi ta abaya, ya ga abinda ta ke yi a daji. Ita kuwa ba ta sani ba. Shi ke nan,

sai yaro ya je, ya hau bishiya mai-dufu. Shi ko, ya rigaya ta zuwa gwona. Da ya zo ya hau bishiya mai-dufu. Sai ya boye. Shi ke nan, sai ta je ta yi kirran yan-uwanta barayi. Suka zo, suka taru, suka chainye kubewa. Da suka chainye, sai ita ta rikiddi mutum, ta koma gida. Ta che ita, ba ta samu komi a gwona ba. Sai yaro ya zo, ya gaya wa uban. Sai uban ya che "To." Da akakwana kaman uku, sai akache ta koma ta debo kubewa. Sai ta taffi. Sai mijin ya bi bayanta. Da ta je, sai ta aje kwariya, ta rikiddi, ta zammi barewa. Da ta zammi, sai ta je ta yi kirran yan-uwanta. Ta yi kirransu, suka zo, suka samu kubewa, suka chainye. Mijin kuwa, yana kalon su. Sai yan-uwan suka taffi, sai ita ta rikiddi mutum, sai ta dauke kwariya ta taffo gida, ta che ba ta samu komi ba. Sai mijin ya komo, sai ya che "Op, ashe, wanche barewa che?" Ita kuwa tana nika. Da yana magana sai wutsiyar barewa ya fitto. Sai ta bar nika, sai ta rikiddi, sai ta taffi aguje. Sai mijin ya bi ta, ba ya same ta ba. Sai ya komo gida, ya zona.

(1) Very unusual, "mata" is the proper word. "Iya" for "ina."

---

## 148

### The Elephant's Daughter.

Wanni mutum, giwa tana kwanche. Da tana kwanche, sai ya zo ya yi mata chikki. Da ya yi mata chikki, sai ta haifu yariniya. Giwan kuwa tana barchi, ba ta tashi ba har wokachin, har yariniya ta yi girima. Shi ke nan, sai giwa ta tashi dagga barchi, sai ta che "Ke, Yariniya, mi ya kawo ki nan?" Ta che "A, dagga chikkinki na fitto." Shi ke nan, sai ta che "To." Yariniya kuma, mai-muna ta che. Sai giwa ta che "Yanzu kadda ki zona nana, sai ki shiga chikkin gari." Ta che "En kin zona nan, sai yan-uwana zasu chi ki." Shi ke nan, sai giwa ta je, ta yi mata itche, ta kai ta sayar ta samu abinchi. Sai yariniya ta che "To." Sai giwa ta che "To, kullum Jimuwa ta yi, ki zo." Ta che "To." Sai ta tashi, sai ta taffi gari, sai ta je bakin rijiya wurinda akedeba sariki ruwa. Sai ta ga bayin sariki suna diba ruwa. Sai ta che "Du Allah ba kuwa sa min ruwa en sha ba?" Sai wata baiwar sariki ta che "Dan durin uwarki." Sai ta che "Mumuna da ke, wa zaya ba ki ruwa ki sha?" Sai yar-uwanta ta che "Habba, ba ta manna." Sai ta ba ta, ta sha. Ta che "Yata, yanzu

ba na samu wurin rabawa gidanku ba?" Sai dayan ta che "Wai, mi za'ayi da ke?" Sai yar-uwar ta che "Ai, na ji yaya tana neman wota yariniya ta zona." Shi ke nan, sai suka taffi gida. Sai ita baiwa ta che "Yaya, ga yariniya, ko kina son ta?" Ta che "Yowa, madallah." Sai yariniya ta zona. Kullum Jimuwa tana taffiya gidan uwan, giwa, sai uwan ta yi wa yar itche ta teffo gida. Ita matar, da ta ke gunta yarta (1), ta haifu dan sariki. Shi kuwa, dan, en ya zo garin chin abinchi, sai ya che "Akawo da yariniya ya chi abinchi." Sai amboye yariniya. Har salla ya zo. Sai kaman jajiberin salla ya zo, sai yariniya ta gudu, ta taffi chan gidan uwar. Shi ke nan, sai yariniya ta zo, ta gaya mata, ta che "Jibi salla." Sai uwar ta che "To, koma tukun." Sai ta che "To." Ta koma gida. Sai daren salla ya yi, sai ta koma wurin uwar, sai uwar ta dauke ta, ta hadiye, ta fitto da ita zazur rabin jikkinta zinariya. Da ta fitto da yariniya, ta duba, sai ta koma hadiyen yariniya, ta fitto da ita rabi zinariya, rabi azurufa. Shi ke nan, sai akafitto mata da kujiran karifi, da mutane masu-kidda, da mutane masu-ganguna, da yam-mata. Sai ta teffo gari, ta sauka gunda akayi wasa, sai ta zona. Akaaje mata kujiran karifi. Sai dan sariki ya zo, ya che yana son ta da aure. Ta che "To, ni ma, ina son ka." Ya che "Em ba ki bawa goma?" Ta che a, a, ba ta so. Ya che "En kawo maki kwariya goro goma." Ta che ba ta so. Shi ke nan sai ta che "Shi, dan zoben hanunka shi ni ke so." Sai ya che "To, shi kadai ki ke so?" Sai ta che "I." Sai ta tashi, ta taffi gidan uwar. Shi ke nan, sai ya raka ta, sai ya koma gida. Sai yariniya ta isa gida, sai uwar ta koma ta hadiye yariniya, sai ta fitta da ita mumuna, bakeyau. Sai ta yi mata itche, sai ta komo gidan sariki, yariniya. Sai wache ta ke gunta, ta che "Enna kika taffi ne?" Ta che "Na je daji ne, na yi batan kai." Sai ta che "To." Sai dan sariki ya saye fura, ya che yariniya ta dama mashi. Sai ta dama, ta dauke zoben nan da ya ba ta, ta zuba achikkin fura. Sai yaro da ya sha, sai ya ga zobe. Sai ya che "Enna kin samu zoben nan?" Sai ta che "To, ka gani de?" Ya che "Zoben nan nawa ne." Sai ya rabi da ita. Sai yaro ya gaya ma uban, sariki. Ya che iya son yariniya da aure. Sai akaba shi, ya aura. Sai yariniya ta taffi, ta gaya wa uwan, chan daji. Sai uwan ta yiwo mata kayan ado. Shi ke nan, sai suka zona.

(1) "Whom she was with her (as) her daughter."

## 149

### The Wonderful Horse.

Yara uku, uwa ta mutu, uba ya mutu. Mainyansu biyu ba su aikin komi sai dara. Auta ba ya dara, sai yawo karban magani. En ya ji labarin mallami mai-magani, ya taffi wurin shi, aba shi maganin rikidda. Sai ya ji labarin Iblis, tana bada maganin rikidda. Sai ya je, ya che "Iblis, na zo wurin ki ne, aba ni maganin rikidda en zamma doki." Sai ta che "To." Ta kawo ta ba shi. Sai ya koma gida. Da ya koma gida, ya che ma yan-uwanshi su tuka gindi da tabebeyi. Sai suka tuka. Sai ya dauke su, ya kai su baban gari masalin Zaria, sai ya zamma doki Ba-Asbini. Masu-gari suna saye doki Ba-Asbini bayi goma sha biyu. Da ya gamma hakka, sai ya che ma yan-uwan "To, ku kama ni, ku taffi da ni wurin sariki, shi ba ku bayi goma sha biyu." Sai suka taffi wurin sariki, suka che "Ga dokimmu, muka kawo 'garin sayaruwa." Sai sariki ya che "To, dokinku dakeyau, na saye bawa goma sha biyu." Suka che "To, kadda ka daure shi suku suku ya gudu, sai da karifi." Sariki ya che "To, na ji." Sai da ya daure shi achikkin gida. Sai ran na kewoyen gari ya zo. Sai sariki ya che "To, bar en hau dokina da na saye bawa goma sha biyu en ji dadi." Da ya hau shi, yana rawa, yana rawa, yana rawa, da ya ga mata sai ya durkusa ya gaishe su. Sai sariki ya che "Kai, ni ban tabba gani doki da dadi hakka."

Sai da suka kussa kofar gidan, sariki ya sauka, sai doki ya gudu. To, garin kuwa akwai doki alfin, sai duk suka bi shi aguje, sai ya chere masu. To, akwai wanni mai-tambayar magani achikkin gidan sariki, shi kuwa shina da doki. Sai sariki ya che "To, ka bi shi, koenna ya shiga ka kamo." To, yana gudu, yana gudu, yana gudu, shi kuma yana bin shi, yana bin shi, yana bin shi. Da ya ga ya kussa kama shi, sai ya tashi, ya zamma shiruwa. Shi kuma mai-bin shi, shi ya yarda nasa doki, ya zamma mikiya, yana bin shi. Da ya wega, ya gan shi ya zo kussa da shi, sai ya rikidda, ya zamma gauraka. Shi kuma, mai-bin shi, ya rikidda, ya zamma borintimki. Suna yi, suna yi, suna tashi, suna tsere, suna zuwa garin Auta. Da ya ga ya kussa kama shi, ya rikidda, ya zamma shalala. Shi kuma mai-bin shi ya zamma chada. Sai suka zo, suka sauka bissa itache da yan-uwan Auta su ke dara. Ga shi, sun sauka tare, ga shi mai-gudu, ga shi mai-son kama shi. Sai shi, Auta, ya rikidda, ya zamma dan-darra, ya fada wurinda yan-uwansa suna yi. Shi kuma mai-bin sa ya rikidda, ya

zamma mutum, ya che ma yan-uwan "Ku ba ni dan-darana." Sai suka che "A, a, dagga enna ka zo da dan-dara?" Sai ya che "A, ku kilga manna, kuwa gani wanni ya hau." Sai suka kilga, suka che "Ai, ga wanni ya hau, zo ka dauke abinka." Ya sa hanu zaya dauke shi, sai dan-dara ya zamma kunama, ya halbe shi. Shi kuwa ya rikidda sago zaya hadiye kunama. Da zaya hadiye shi, shi kunama, ya zamma kasa. Da sago ya ga kasa ya yi mashi girima, ba zaya iya hadiye ba, yana dubawa, sai shi Auta, wanda ya rikidda kasa, ya che "Kai, tashi, mu zamma mutane." Suka tashi, suka zamma mutane. Sai Auta ya che "Don bawa goma sha biyu da na karba gun uban-gidanka, shi ya sa kana bi na?" Sai ya che "To, ina zamma wurin sariki, ya san ina tambaya. To, wanni tambaya ya zo zaya karbe masa kaya?" Ya che "To, en ban bi ka ba, sariki ya che ni munafuki, shi ya sa na bi ka." Auta ya che "To, tashi ka taffi gida." Ya che "A, a, ba zan san gida dagga nan." Sai ya che "To, muwa rikidda hankaka, en kai ka gida." Sai suka rikidda hankaka, suka tashi. Da suka kussa ga garin, sai ya che "To, ka gani kuma?" Sai ya zamma mutum kuma, ya je wurin sariki, ya che "To, na bi shi, na bi shi, har kwana uku, ni ban same shi ba." Sai sariki ya che "To, enna dokinka?" Ya che "Na bar shi a daji." Sai akasayo masa wanni doki, akasayo mashi kaya na dubu don ya yi wahala kwana uku saboda sariki.

---

## 150

### The Lucky Youngest Son.

*See* No. 80.

## (*b*) STORIES IN MAN, 1911 and 1913.

### 151

### The Boy who cheated Death.

*See* No. 96.

---

### 152

### How the Boy escaped from the Witch.

Wannan ne, wanni yaro ya tashi taffiya. Da ya tashi taffiya, ya che shi zaya je ya ga yanda duniya ta ke. Shi ke nan, sai ya tashi da dokinshi kato, da kaza achikkin bargami. Da ya taffi, iya taffiya, sai ya daura ma doki aska kaman ashirin. Iya taffiya, iya taffiya, iya taffiya, sai ya tarada gidan maiya chan daukan daji, gida kuwa kato ne, da katanga, da zaure kaman ashirin. Ya je, ya tarada maiya ta yi fati-fati. Duk jikkin, koenna baki ne. Shi ke nan ya hango ta, iya kan doki. Wannan baki ya che "Ni kin ba ni, ni ba kin ba ni ba." Wannan baki kuwa ya che "Ni kin ba ni, ni ba kin ba ni ba." Sai yaro ya shiga zaure. Da ya kussa da zaure chan, zauren da ta ke, sai ya che "Salla'am aleikum." Sai nan da nan ta shafe bakuna da hanuna, sai baki daya. Sai ta che "Aleika salla'am." Sai ta che "Bako, shigo manna." Ta che "Ka gani?" Ya che "A, a, ban gan ki ba." Ta che "Kai, de, fadi gaskiya." Ya che "Allah, ban gan ki ba, sai de wannan gani da mu ke yi zanchen nan." Sai ta che "To, ga daki mai-keyau, shiga." Sai ya shiga, ya kwunche surdi akan doki, ya daure.

Shi ke nan, sai ya yi kwanche, iya futa, dare ba ya yi ba tukuna, maiya ta yi mashi abinchi ya chi. Sai ya che "To." Shi ke nan, sai da da dare ya fige kazansa, sai ya gassa, sai ya chi ya koshi. Sai mache ta yiwo abinshi, ta kawo wa yaro. Shi ke nan, sai yaro ya che "To, Madallah," sai ya karba, ya aje, ya ki chi. Sai ya yi rami achikkin daki, da ya yi rami sai ya zubar da tuwo achikki, ya rufe. Shi ke nan, da ya zubar,

sai ya kai mata kwariya. Shi ke nan, da ya kai mata kwariya, dare ya yi.

Da dare maiya ta wasa wuka zata zo ta yanka yaro. Shi ke nan, en ta taffo, sai doki ya yi haniniya—ya sani ita maiya che, shi dokin. Shi ke man, sai mache ta koma. Da ta koma, ta kwanche, sai barchi ya dauke ta. Da barchi ya dauke ta, sai yaro ya tashi, ya daura surdi, zaya gudu gida. Sai ya bar rawaninshi achikkin doki don kadda ta farga, ta che ya gudu ne. Sai yaro ya hau, iya sukuwa, sai mache ta faraka. Da ta faraka, sai ta duba doki, ba ta kowa ba, sai rawani. Sai ta dauke rawani agujiya. Tana che " Ka bar rawaninka," iya che "Na bar maki taushi." Tana che "Na ga sauraye da tsoro." Da ta yi kussa zata kama wutsiyan doki, sai aska ya yanka ta a hanu. Shi ke nan, da ya yanka ta, ta tsaya, tana lashewan jini. Sai yaro, sai ya yi nesa har ya kai bakin kogi. Sai ta je ta yi mashi kogi agabban shi. Sai yaro ya zo, ya duba, kogi ya yi yawa, sai doki ya tsale, ya kwan a wanchan gechi.

Shi ke nan, sai maiya ta barri yaro, ta koma gida. Da ta koma gida, sai yaro ye che "Ai, Allah ya so ni."

---

## 153

### How the Ill-treated Girl became Rich.

*See* No. 93.

---

## 154

### Dan Kuchingaya and the Witch.

*See* No. 94.

---

## 155

### The Witch who ate her Children.

Wannan de, mache, maiya che, sunanta Umbajiya. Da ita da yayanta, su goma sha biyu yayan. Sai ta ture su su je daji, suka bar baban a gida. Sai ta che da shi " Hau ka chiro min kubewa." Sai ya che " To," sai ya hau. Sai da ya chiro kubewa ya gangaro da shi, sai suka fada achikkin turimi.

Da suka fada, sai ta kiriba yaro a turimi tare da kubewa. Shi ke nan, sai ta yi abinchi da yaro.

Sai yan-uwan suka komo, sai ta che "Ga naku abinchin." Sai suka chi, ba su sani ba. Shi ke nan, washen gari zasu daji, sai ta che daya ya zona. Sai daya ya zona. Ta che "Hau ka chiro min abu." Sai ya che "To." Sai ya hau, sai ya tsunko, sai ya gangaro, sai suka fada tare da kubewa. Sai ta kiriba, sai ta yi abinchi, sai suka zo suka chi, ba su sani ba. Duk ta chinye yayan, sai dan kankani, Auta, shi kadai. Shi ko, Auta, ya gudu.

Da ya gudu, ta neme shi, ta rassa, sai ta bi shi. Iya gudu, iya gudu, iya gudu, sai ta hango shi, sai ya che "Maramazza Doki, Baba, kai ni gida." Ai sawunshi ne dokinshi. Sai ya zo ya samu masu-shuka. Suka che "Samari, mi ka ke gudu?" Ya che "Uwana ne zata chi ni." Sai suka che "Zona, ko da fatainya ba muwa kasshe ta ba?" Shi ke nan, sai ya che "To." Sai uwar ta taffo, tana waka, tana chewa "Barraram, barraram, Dodo, zani gida, ga ni nan Dana." Sai da suka ji zuwanta, sai tsoro ya kama su, sai suka che "Yaro, yi ta kainka, mu mu yi ta kaimmu." Shi ke nan, sai yaro ya taffi, ya che "Maramazza Doki, Baba, kai ni gida." Sai ya zo ya taradda masu-kira. Sai suka che "Yaro, mi ka ke gudu?" Sai ya che "Uwana ne zata chi ni." Sai suka che "Zona, ko da zugazugi ba muwa kasshe ta ba?" Sai uwar ta taffo, tana waka, tana chewa "Barraram, barraram, Dodo, zani gida, ga ni nan Dana." Sai da suka ji zuwanta, sai tsoro ya kama su, sai suka che "Yaro, yi ta kainka, mu mu yi ta kaimmu." Shi ke nan, sai yaro ya taffi, ya che "Maramazza Doki, Baba, kai ni gida."

Shi ke nan, sai ya taradda masu-yaki. Sai suka che "Yaro, mi ka ke gudu?" Sai ya che "Uwana ne zata chi ni." Sai suka che "Zona, muwa kore ta da yaki." Sai uwar ta taffo, tana wakanta. Sai da suka gan ta, sai suka yi ta yaki. Sai da suka yi ba su kasshe ta ba, sai suka che "Yaro, tashi ka taffi." Sai ya che "To."

Sai iya gudu, iya gudu, iya gudu, sai ya je gidan bushiya. Sai bushiya ta che "Yaro mi ka ke gudu?" Sai ya che "Uwana ne zata chi ni." Sai ta che "Zona nan." Sai da ta taffo, sai ta tambaya bushiya, ta che "Ba kin ga yaro ya fuche ba?" Ta ki magana. Sai ta che "Ba kin ga yaro ya fuche ba?" Ta ki magana. Sai maiya ta ji fushe, sai ta dauke ta, ta hadiye; sai bushiya sai ta fuda chikkin maiya, ta fitto. Sai ta dauke ta, ta dada hadiwar bushiya; sai bushiya ta keta

kirijinta, ta fitto. Sai ta dauke ta, ta kara hadiwa; sai bushiya ta fitto dagga zuchiyanta, sai ta kasshe maiya. Sai ta che " Yaro, ka fitto, ka taffi."

---

## 156

### The Witch who ate her Grandchild.

Wannan de, uwanta maiya che, sai ta haife yariniya; yar, ita ba ta maita. Sai akazo akaaure ta a wanni gari. Akaaure ta, akataffi da ita. Da akataffi da ita, sai tana nan, har ta yi chikki, ita yariniya, sai ta haifu da. Da ta haifu, sai akayi suna, akasa dan sunansa Allah Sidi.

Shi ke nan, yaro ya yi girima, sai ya yi dama kadan, sai yariniya ta che zata taffi ta ga gidansu. Da ta zo, akakwana biyu, sai uwar ta ba ta kwando da mararaki da burimi, ta dauko ruwa. Ta taffi, en ta dauko ruwa sai ruwa ya zube. Shi ke nan, sai uwar ta dauke yaro, ta sa shi achikkin turimi zata daka. En zata daka, sai yaro ya yi dariya, en ya yi dariya sai maiya ta aje tabariya har ya so-uku. Sai maiya ta rufe ido, sai ta daka yaro. Da ta daka, sai ta kwashe yaro, ta yi abinchi da shi. Da ta yi, sai ta aje wa yariniya hanu da abinchi.

Sai yariniya ta gaji, ta taffo gida, da ta taffo, sai ta che "Ga naki abinchi." Sai yariniya ta dauko, tana chi, sai ta ga hanun yaro achikki. Sai ta mayar, ta taffi chan gidan mijin, tana kuka. Ta je, ta che "Ankai yaro wurin uwana, ga shi, ta kasshe." Shi ke nan, sai miji ya che "To, muwa rama."

Sai miji ya yi rijiya mai-zurufi, sai ya dauko kain rumbu, ya sa achikkin rijiya, ya debo kayan itche kaman uku, sai ya zubar achikkin rijiya; sai ya sa wuta. En de ya sa wuta, sai wuta ya kama itche, ya chi, da ya chi, sai gun ya yi ja wur. Sai ya dauko tabarima, ya sa tabarima kaman uku a bakin rijiya. Sai ya aike da uwar yariniya, ya che yariniya ta mutu. Sai yariniya, ya boye ta a daki. Sai uwar ta taffo, zata yi gaisuwar mutuwa. Shi ke nan, sai da ta zo, sai akache " Zona kan tabarima." Shi ke nan, da ta zona, suna gaisuwa, sai ko maiya ta hauka achikkin rijiya; ta mutu. Sai akache "Yariniya, fitto, abinda uwanki ta yi mana mun rama." Sai yariniya ta che "To." Sai kuma sai suna nan, har yariniya ta samu wanni chikki.

---

## 157

### The Three Youths and the Three Devils.

*See* No. 90.

---

## 158

### The Youth who courted a Witch.

Wata karuwa che, ta tashi ta je wanni gari. Samarin garin nan ya zo gun ta, sai ta che ba ta so; wanni ya zo gun ta sai ta che ba ta so. Duka sauraye suka zo, sai ta che ba ta so. Lokachin nan sai dan sariki ya tashi ya je, ya che ina son ta, sai ta che "Ni ma, ina son ka." Sai ya dauke ta, ya kawo ta dakinsa. Dan sariki ya che shi zaya daura mata aure. Ita kuwa, ta che "In de zaka daura mani aure, sai ka fadi maganinda ya ke chikkinka na ji." Lokachin nan sai ya che zaya gaya mata. Sai ya fara mata, ya che "Dutsi." Ya che yana zamma garafunu. Ta che "To, na ji biyu." Ya che "Ina zamma ruwa," ya che "Ina zamma kash—." Sai uwa tas ta che "Ragi manna." Sai ya yi shiru. Shi ke nan, sai ya che magani ya kare da ya ke chikkinsa.

Sai da gari ya waye, da hantsi, sai mata ta che ya raka ta zuwa garin iyayenta. Sai dan sariki ya che "To." Suka tashi, suka kama turaba. Suna taffiya a daukan daji, sai ta fidda zannenta daya, ta yatse. Sai ya che "Op, kin yarda zannenki?" Sai ta che anan ta samu. Suna taffiya kuma komodu, sai ta sinche kuma zannenta duka, ta zubar, sai kuma ta zamma aljanna. Sai ta dauke dan sariki, ta buga a kassa, sai dan sariki sai ya zamma dutsi. Sai ta dauke dutsi kuma, ta zo ta dauka a kassa, sai ya zamma garafunu. Sai ta fige garafunu, ta zo zata kiriba, sai kuma ya zamma kashin awaki. Sai ta tsaya, ta duba nan, ta duba nan, sai ta che "Na ji ya che 'Kash—,' uwansa ta hanna." Sai ta dauko kashin awaki, tana dubawa, sai ta yarda kashin awaki kuma. Halyo ta komo, ta dauke kashin awakin, ta che "Ko shi ne, ko ba shi ne ba?" Sai ta jefa shi da karifi achikkin daji. Da ya ji ya fadi, sai ya zamma mutum, ya gudu gida.

---

## 159—166

### The Morals of the Hausas as indicated by their Folk-lore.

The Hausa text and the English translations of these will be published together in "Man" this year.

## (c) STORIES IN *THE TAILED HEAD-HUNTERS OF NIGERIA*.[1]

### 167

THE MALLAM, THE SPIDER, AND THE HYÆNA.

*See* No. 103.

---

### 168

THE SPIDER, THE FISH, AND THE LION.

Gizzo ke nan. Akayi yunwa. Da akayi yunwa, ba ya da abinda zaya chi. Sai biribiri su ke debo kainya a tabki mai-fadi dayawa, ba mai-shiga wurin. Itachen kainya atsakan kogi ya ke. Sai ya debo kainya ya kan zo, tsakan gidan gizzo, sai ya zuba mashi kainya biyu, ya dauke ya chi. Da ya komo kuwa, sai ya che ya ba shi fufuki. Suka tashi tare, suka je kogin nan awurin kainyan nan. En zaya deba sai ya hanna shi. Sai ya yi mashi wayo, ya che " Mu kan kwanta a itache, mu yi barchi, kainya ya nuna."

To, da su ke yin barchi, ita ta chiri gashinta a jikkin gizzo. Da ta chiri, sai ta tashi, ta bar shi akwanche. Da ya yi motsi, sai ya fada achikkin kogi. Da ya fada achikkin kogi, sai gidan yan ruwa. Sai akayi mashi marhaba. Da suka yi mashi marhaba, sai sun yi gardama, wanni ya che dan-uwanshi, wanni ya che ba dan-uwanshi ba. Sai wanda yana gardama ya che " Adama kunun dorowa da zafi, idan dan-uwammu ba ne sai ya fuche." Sai ya che " Akai rana arikka motsiwa, kadda asa hanu." Sai ya shainye. Sai suka che " Dan-uwammu ne." Sai akakai shi dakin kifi da ta yi kwai dari. Sai ya che ma yaran gida " Izan ku ji 'pus,' ku che 'Tusan bako'."

---

[1] N.B.—These tales have been much more freely translated than those which precede, for the book is not one upon the Hausa people.

Sai ya dauke kwai, ya sa a wuta. En ya yi "Pus" yara sun che "Tusan bako." Sai mainya suka che "Ubanku, kuka yi mashi shegantaka?" Sai ya che "Ku bar su, ai ni kakansu ne." Sai ya chainye kwai dari sai ya bar daya.

